**NATIONAL OPEN UNIVERSITY OF NIGERIA**

**FACULTY OF ARTS**

**COURSE CODE: HAU 208**

**COURSE TITLE: HAUSA SOCIAL INSTITUTIONS (2 Credit Units)**

**COURSE GUIDE**

COURSE CODE: HAU 208

COURSE TITLE: HAUSA SOCIAL INSTITUTIONS (2 Credit Units)

CREDIT UNIT: 2

COURSE STATUS:

SEMESTER:

REQUIRED STUDY HOURS: 4 Hours per week

EDITION: First Edition 2019

Course Team:

Course Developer:

Course Writer: Dr. Abdullahi Sarkin Gulbi –UDUS

Instructional Designer:

Learning Technologists:

Content Editor:

Copy Editor:

# HAU 208 HAUSA SOCIAL INSTITUTIONS (2 Credit Units)

National Open University of Nigeria

Headquaters

14/16 Ahmadu Bello Way

Victoria Island

Lagos.

Abuja Annex

245 Samual Adesujo Ademulegun Street

Central Bussiness District

Opposite Arewa Suites

Abuja.

E-mail: centralinfo@nou.edu.nig

URL: www.nou.edu.nig

National Open University of Nigeria

First Printed: 2019

ISBN

All Rights Reserved

Printed by……………………

For

National Open University of Nigeria

ABIN DA KE CIKI

Gabatarwa……………………………………………………………1

Manufar Kwas…...................................................1

Manufar Kwas……………………………………………...1

{unshiya………………………………………………………1


FASALI NA 1: HAIHUWA DA TSARIN IYALIN HAUSAWA

KASHI NA 1: Azuzuwan Mutane a Zamantakewar Hausawa……………… 2

1.0 Gabatarwa………………………………………………….2

2.0 Manufar Darasi…………………………………………….2

3.0 Ma' anar Ajin Mutane……………………………………….2

3.1 Rabe-raben Azuzuwan Mutane………………………………2

3.1.1 Ta Fuskar Sarauta………………………………………………3
3.1.2 Ta Fuskar Tattalin Arziki ……………………………………...3
3.1.3 Ta Fuskar {aurace-}aurace ……………………………………3
3.1.4 Ta Fuskar Ilimi ………………………………………………3
3.1.5 Ta Fuskar Ajin Shekaru…………………………………………4
3.1.6 Ta Fuskar Jinsi……………………………………………………4
4.0 Kammalawa………………………………………………4
5.0 Ta}aitawa……………………………………………………5
6.0 Auna Fahimta…………………………………………………5
7.0 Manazarta……………………………………………………5

KASHI NA 2: Tsarin Iyali a Zamantakewar Hausawa

1.0 Gabatarwa………………………………………………….6

2.0 Manufar Darasi…………………………………………….6

3.0 Mene ne Iyali?..........................................................................................6

3.1 Matsayin Iyali da Ayyukansu a Gidan Bahaushe……………………6
3.1.1  Maigida da Ayyukansa……………………………………………6
3.1.2 Matan Gida……………………………………………………8
3.1.3 {annan Maigida…………………………………………………8
3.1.4 Kakanni……………………………………………………9
3.1.5  ' Ya' ya……………………………………………………………9
3.1.6  Jikoki:……………………………………………………9
3.1.7 Barwan Maigida:……………………………………………10
4.0 Kammalawa…………………………………………10

5.0 Ta}aitawa……………………………………………10
6.0 Auna Fahimta………………………………………10
7.0 Manazarta…………………………………………11
KASHI NA 3: Al’ adun Aure a Rayuwar Hausawa
1.0 Gabatarwa.........................................................................................11
2.0 Manufa...............................................................................................11
3.0 Ma’ anar Aure...................................................................................12
3. 1 Bukin Aure.........................................................................................13
3.2 Tsarin Neman Aure A Al’ ummar Hausawa..........................................13
3.2.1 Soyayya Tsakanin Saurayi Da Budurwa..............................................13
3.2.2 Tsarin Soyayya a Al’ adar Hausawa....................................................14
3.2.3 Al’ adar Zance ko Ta]i........................................................................14
3.2.3.1 Tsarin Zance a Al’ adar...................................................................14
3.3 Shigar Iyaye Wurin Neman Aure............................................................15
3.4 Fitowa Gida (Bi]ar Iyaye) .....................................................................15
3.5 Gaisuwar Abokai...................................................................................15
3.6 Tsarin Na-Gani-Ina-So A Al’ adar Aure.................................................16
3.7 Bukin Aure............................................................................................16
3.7.1 Nason Zamunanci Cikin Al’ adun Nema Da Bukin Auren Hausawa................16
3.7.2 Nason Sutura .....................................................................................17
3.7.3 Nason Al’ adun Ki]a da Wa}a ..............................................................19
3.7.4 Nason Al’ adar Fati Da Fikinik............................................................19
3.7.5 Nason Shaye-Shaye............................................................................20
3.7.6 Nason Gur~acewar Tarbiyya................................................................20
4.0 Kammalawa...........................................................................................21
5.0 Ta}aitawa..............................................................................................21
6.0 Auna Fahimta........................................................................................21
Manazarta...................................................................................................21

KASHI NA 4: Al’ adun Haihuwa

1.0 Gabatarwa……………………………………………………22

2.0 Manufar Darasi………………………………………………22

3.0 Ma’ anar Haihuwa……………………………………………22
3.1 Al’ adu Kafin da Bayan Haihuwa……………………………23

3.1.1 Al’ adar Goyon Ciki……………………………………………23

3.1.2 Kayan {auri……………………………………………………25

3.1.3 Bukin Suna……………………………………………………25

3.1.4 Wankan Jego…………………………………………………..26

3.1.5 Kayan Gara……………………………………………………27

3.1.5 Renon Abin da aka Haifa……………………………………27

3.2 Matsayin Haihuwa a Al’ ummar Hausawa…………………………28
3.2.1 Abin Alfahari…………………………………………………28
3.2.2 Tausayi ga Wanda bai Samu ba………………………………28
3.2.3 Hanyar [ebe Takaici……………………………………………29
3.2.4 [ebe Kewa a Cikin Gida………………………………………29
3.2.5 Hanyar Samun Kula a Yayin Tsufa……………………………29
4.0 Kammalawa…..……………………………………………30
5.0 Ta}aitawa……………………………………………………30
6.0 Auna Fahimta…………………………………………………30
7.0 Manazarta………………………………………………………30
KASHI na 4: Tarbiyya

1.0 Gabatarwa……………………………………………………31

2.0 Manufar Darasi……………………………..………………31

3.0 Ma’ anar Tarbiyya…………..…………………………………31

3.1 Hanyoyin Tarbiyya a Al’ adar Bahaushe………..………………32
3.1.1 Hanyar Tatsuniya……………………………………….....32
3.1.2 Hanyar Iyaye Mata……………………………………….....33
3.1.3 Iyaye Maza ……………………………………………...33
3.1.4 Hanyar Ma}wabta……………………………………..34
3.1.5 Hanyar Shugabanni……………………………………34

3.1.6 Sauran Al’ umma…………………………………………35
3.2 Matsayin Tarbiyya…………………………………………..35
4.0 Kammalawa…………………………………………………36
5.0 Ta}aitawa…………………………………………………36
6.0 Auna Fahimta………………………………………………36
7.0 Manazarta…………………………………………………36
KASHI NA 5: Zumuncin Hausawa
1.0 Gabatarwa…………………………………………………37

2.0 Manufar Darasi…………………………………………….37

3.0 Ma’ anar Zumunci…………………………………………37
3.1 Rabe-raben Zumunci………………………………………38
3.1.2 Zumunci Unguwa…………………………………………38
3.1.3 Zumunci Gari……………………………………………..39
3.1.4 Zumuncin Sana’ a…………………………………………39
3.1.5 Zumuncin Addini…………………………………………40
3.2 Dalilan Zumunci……………………………………………40
3.4 Matsayin Zumunci…………………………………………41
4.0 Kammalawa…………………………………………………41
5.0 Ta}aitawa……………………………………………………41
6.0 Auna Fahimta……………………………………………...41
7.0 Manazarta…………………………………………………...41
FASALI NA 2: SULHU A ZAMANTAKEWAR HAUSAWA

KASHI NA 1: Sulhu da Sasantawa a Zamantakewar Hausawa

1.0 Gabatarwa………………………………………………..42

2.0 Manufar Darasi……………………………………………42

3.0 Ma’ anar Sulhu………………………………………………42
3.1 Sulhun Gargajiya…………………………………………..43
3.2 Rabe-raben Sulhu……………………………………………43
3.2 .1 Sulhun Cikin Gida……………………………………..44
3.2.2 Sulhun Waje…………………………………………….45
3.3 Rikice-Rikicen da ke Haddasa Sulhu……………………………...45
3.4 Dalilan Sulhu………………………………………………...45
3.5 Sigogin Sulhu………………………………………………...46
3.6 Muhimmancin Sulhu a Zamantakewarmu ta Yau…………………...46
4.0 Kammalawa………………………………………………...47
5.0 Ta}aitawa…………………………………………………...47

6.0 Auna Fahimta……………………………………………47
7.0 Manazarta……………………………………………..48
KASHI NA 2: Taubasantaka
1.0 Gabatarwa……………………………………………48
2.0 Manufar Darasi………………………………………48
3.0 Ma' anar Taubasantaka……………………………………49
3.1 Dalilan Taubasantaka……………………………………49
3.2 Rabe-raben Taubasantaka………………………………50
3.2.1 Taubassan Bahaushe na Jini………………………………50
3.2.2 Taubassan Bahaushe na |angaren Uwa ……………………50
3.2.3 Taubassan Bahaushe na |angaren Uba……………………51
3.2.4 Kaka da Jika………………………………………………..51
3.2.5 Taubassan Bahaushe ta Fuskar Al'ada……………………...51
4.0 Kammalawa…………………………………………52
5.0 Ta}aitawa……………………………………………52
6.0 Auna Fahimta…………………………………………52
7.0 Manazarta……………………………………………52
KASHI NA 3: Ma}wabtaka
1.0 Gabatarwa……………………………………………53
2.0 Manufar Darasi………………………………………53
3.0 Mene ne Ma}wabtaka?...........................................................................54
3.1 Dalilan Ma}wabtaka……………………………………55
3.2 Matsayin Ma}wabtaka……………………………………57
4.0 Kammalawa…………………………………………57
5.0 Ta}aitawa……………………………………………57
6.0 Auna Fahimta…………………………………………58
7.0 Manazarta……………………………………………58
KASHI NA 4: Ayyukan sa kai a Zamantakewar Hausawa
1.0 Gabatarwa……………………………………………59
2.0 Manufar Darasi………………………………………59

3.0 Ma' anar Ayyukan sa Kai……………………………………..59
3.1 Dalilan Ayyukan sa Kai……………………………………59
3.2 Rabe-raben Ayyukan sa Kai……………………………….60

3.2.1 Aikin Gayya……………………………………………….61

3.2.1.1 Gyaran Hanya…………………………………………..61

3.2.1.2 Gyaran Ma}abartu……………………………………..61
3.2.1.3 Gayyar Noma……………………………………………61
3.2.1.4 Taimakon Gajiyayyi da Maras Lafiya………………...63
3.2.1.5 Ayyukan Samar da Tsaro………………………………63
3.3 Matsayin Ayyukan sa Kai…………………………………...64
4.0 Kammalawa……………………………………………….64
5.0 Ta}aitawa………………………………………………….64
6.0 Auna Fahimta…………………………………………….64
7.0 Manazarta…………………………………………………65
KASHI NA 5: Ayyukan Dole a Zamantakewar Hausawa

1.0 Gabatarwa…………………………………………………65

2.0 Manufar Darasi……………………………………………65

3.0 Ma' anar Ayyukan Dole……………………………………..66
3.1 Rabe-raben Ayyukan Dole…………………………………66

3.1.1 Neman Abinci………………………………………………..66

3.1.2 Koyon Sana' o' i…………………………………………….67

3.1.3 Neman Ilmi da Inganta Tsarin Bayar da Shi………………...69

3.1.3.1 Ilmin Gargajiya (tatsuniya, da sana' o' inmu)………………69
3.1.3.2 Ilmin Addinin Musulunci………………………………..70
3.1.3.3 Ilmin Boko……………………………………………….70
3.1.4 Biyan Harajin Kasuwa…………………………………….71

4.0 Kammalawa……………………………………………….71
5.0 Ta}aitawa………………………………………………….71
6.0 Auna Fahimta……………………………………………..72
7.0 Manazarta…………………………………………………72

FASALI NA 3: AL' ADUN MUTUWA DA BARKWANCIN HAUSAWA

KASHI NA 1: Al’ adun Mutuwa

1.0 Gabatarwa…………………………………………………72

2.0 Manufar Darasi…………………………………………….73

3.0 Ma’ anar Mutuwa………………………………………….73
3.1 Sunayenta…………………………………………………74
3.2 Dalilan faruwar Mutuwa…………………………………..74
3.3 Alamomin Fitar Rayuwa…………………………………..75
3.4 Tabbatar da Faruwar ta…………………………………….76
3.5 Bizne Mamaci……………………………………………...76
3.6 Al’ adun Mutuwa Gabanin Musulunci..………………………….76
4.0 Kammalawa……………………………………………..77
5.0 Ta}aitawa………………………………………………..77
6.0 Auna Fahimta…………………………………………….78
7.0 Manazarta………………………………………………..78

KASHI NA 2: Zaman Makoki

1.0 Gabatarwa………………………………………………..79

2.0 Manufar Darasi……………………………………………79

3.0 Ma’ anar Zaman Makoki…………………………………….80

3.1 Zaman Makoki Kafin Bayyanar Musulunci………………………80

3.2 Zaman Makoki Bayan Zuwan Musulunci………………………80

3.3 Zaman Makoki da Bun}asar Zumuncin Bahaushe…………………82

3.3.1 Ha]a kan Dangi na Jini……………………………………………82

3.3.2 Raya Zumuncin Auratayya…………………………………………..82

3.3.3 Kyautata Dangantaka a Tsakanin Ma}wabta…..………………………83

3.3.4 {ara Dan}on Zumnuta a Tsakanin Masu Sana’ a………………………84

3.3.5 Kara da Gudunmawa………………………………………………84

3.4 Zaman Makoki a Yau……………………………………………85

3.5 Matsalolin Zaman Makoki a Yau da Hanyoyin Magance su……………...86

3.6 Hanyoyin da Za a Magance Matsalolin…………………………...87

4.0 Kammalawa……………………………………………………..87
5.0 Ta}aitawa…………………………………………………….87
6.0 Auna Fahimta………………………………………………...88
7.0 Manazarta…………………………………………………….88

KASHI NA 3: Rabon Gado
1.0 Gabatarwa……………………………………………………89
2.0 Manufar Darasi………………………………………………89
3.0 Ma’ anar Gado……………………………………………….89
3.1 Dalilan Rabon Gado…………………………………………89
3.2 Matsayin Gado……………………………………………….90
3.3 Muhimmancin Gado………………………………………….91
4.0 Kammalawa……………………………………………………91
5.0 Ta}aitawa……………………………………………………..92
6.0 Auna Fahimta…………………………………………………92
7.0 Manazarta……………………………………………………92
KASHI NA 4: Barkwanci a Zamantakewar Hausawa
1.0 Gabatarwa……………………………………………………93
2.0 Manufar Darasi……………………………………………..93
3.0 Ma’ anar Barkwanci…………………………………………93
3.1 Rabe-raben Barkwanci………………………………………94
3.1.1 Barkwanci ta Fuskar Aure da Ya}i………………………………94
3.1.2 Barkwancin Gobirawa da Yarbawa ……………………………94
3.1.3 Barkwancin Katsinawa da Kabawa………………………………95
3.1.4 Barkwancin Katsinawa da Ha]ejawa……………………………96
3.1.5 Barkwancin Kanawa da Daurawa………………………………97

3.1.6 Barkwanci Ha]ejawa da Katagumawa……………………………………….97

3.1.7 Barkwanci Hausawa da Wasu {abilu…………………………………….97

3.1.8 Katsinawa da Nufawa……………………………………………….98

3.1.9 Katsinawa da Barebari………………………………………………..98

3.1.10 Katsinawa da Gobirawa……………………………………………..99

3.1.11 Barebari da Fulani…………………………………………………99

3.1.12 Barkwanci Hausawa da Buzaye……………………………………..99
3.1.13 Barkwanci Hausawa da Ibo…………………………………………100

3.1.14 Barkwanci Zamfarawa da Dakkarawa……………………………….101

3.2 Barkwancin Hausawa ta Fannin Sana' a…..………………………….102

3.2.1 Masunta da Mahauta…………………………………………...103

3.2.2 Mahauta da Majema/Makiyaya……………………………………103

3.2.3 Wanzamai da Ma}era/ Sharifai……………………………………103

3.2.4 Barkwanci Masu Goro da Masu Gishiri…………………………….104
3.2.5 Barkwanci Masu Ra}umai da Masu Jakai………………………….104
3.2.6 Direbobin Mota da Masu Ra}umai………………………………….104
4.0 Kammalawa……..…………………………………………………..104

5.0 Ta}aitawa……………………………..……………………………105

6.0 Auna Fahimta……………………………………………………….105

7.0 Manazarta…………………………………………………………..105

# NATIONAL OPEN UNIVERSITY OF NIGERIA

## HAU 208: HAUSA SOCIAL INSTITUTIONS (2 Credit Units)

## Gabatarwa

Wannan kwas ya himmatu ne wajen bayyana batutuwan da suka shafi al'adun zamantakewar Hausawa. A cikin muhimman batutuwan kuwa sun }unshi azuzuwan (rukunin) mutane a zamantakewar al'ummar Hausawa ta fuskar matsayi, jinsi, daraja da kuma ilmi. A wani sashen kuwa a za a duba yadda zamantakewar aure da tsarin iyali na Hausawa ke gudana. Sauran batutuwan kuwa sun ha]a da ; Al'adun Haihuwa da reno (tarbiyya), Taubasantaka da 'yanuwantaka da kuma ma}wabtaka a zamantakewar Hausawa. A }arshe kuma a kawo al'adun mutuwa da tsarin rabon gado da kuma gurbin barkwanci a zamantakewar Hausawa.

## Manufar Kwas

Manufar wannan kwas ita ce a samar wa da ]alibai ko masu karatu bayanai da za su ba su haske ko masaniya a kan batutuwan da suka shafi al'adun zamantakewar Hausawa, kama da tsarin zamantakewar iyali da haihuwa da tarbiyya da zumunci ma}wabtaka da kuma al'adun mutuwa.

## {unshiya

Wannan kwas ya }unshi fasali guda uku muhimmai, kuma kowane daga cikin fasullan suna ]auke ne da kashi hu]u zuwa biyar, wannan ya bayar da jimlar kasusuwan guda goma sha hu]u a gaba]ayan kwas ]in. A cikin kowane kashi akwai tambayoyin auna fahimta da aka yi zuwa ga ]alibai domin su zamar masu wata kafa ta auna fahimtarsu zuwa da darussan.

# FASALI NA 1: HAIHUWA DA TSARIN IYALIN HAUSAWA

## KASHI NA 1: Azuzuwan Mutane a Zamantakewar Hausawa

### 1.0 Gabatarwa

A }ar}ashin wannan darasi za a tattauna ne dangane da rukunin mutane a zamantakewar Hausawa. Darasin zai duba yadda ake iya rarrabe Hausawa rukuni-rukuni ta la'akari da matsayinsu da tattalin arzinkinsu da ilmi da kuma jinsi.

## 2.0 Manufar Darasi

Wannan darasi an gina sa ne da nufin fayyace wa ]alibi ko mai karatu samun masaniya game da azuzuwan mutane a zamantakewar Hausawa. Wanda ake sa ran a }arshen darasin ]alibai su iya rarrabe rukunin mutanen da ake da su a tsarin zamantakewar Hausawa ta fuskar matsayi da tattalin arziki da kuma ilmi.

## 3.0 Ma'anar Ajin Mutane

Wannan wata hanya ce ta rarrabe mutane zuwa rukuni-rukuni ta la'akari da ilminsu da ayyukansu ko sana'o'insu da kuma yanayin tattalin arzikinsu. Dangane da haka, Hausawa kamar sauran al'ummun duniya sukan kalli azuzuwan mutane ne ta lura da matsayi da ilmi da tattalin arzikin mutum kafin su yanke masa hukuncin ajin da yake.

## 3.1 Rabe-raben Azuzuwan Mutane

A }o}arin rarrabe azuzuwan mutane, masana da dama sun bayar da nasu ra'ayi dangane da hakan, wasu suna kallon abin cewa a }asar Hausa rukunin mutane iri biyu ne, akwai sarakuna ko masu gari da kuma talakawa, yayin da wasu ke da fahimtar cewa ana iya raba kowace al'umma ne zuwa gida uku (3), wato Mutane na sama da rukunin tsakiya da kuma na }asa. Misali masana ilimin Zamantakewar [an'Adam sun raba mutane zuwa gida biyar (5), akwai rukunin sama (masu ilmi), Tsaka-tsaka, na tsakiya, da ma'aikata da kuma rukunin talakawa. Sai dai duk da wa]annan hasashen, zai kyautu a wannan mataki mu ]auki ajin mutane a al'ummar Hausawa kamar haka;

### 3.1.1 Ta Fuskar Sarauta

A zamantakewar Hausawa akwai wannan kaso na sarakuna da talakawa. Bisa al'ada babu gari ko }auyen da za a rasa wa]annan rukunin mutane ( Masu gari da Talakawa). Wannan ne ya sa aka raba mutane ta fuskar matsayin sarauta. A fahimtar wannan kaso }asar

Hausa mutum biyu ne ke cikinta, wato rukunin masau sarauta da talakawa. Masu sarauta sun shafi sarakunan da suka kan godon sarauta da zuri’arsu gaba]aya. Sauran al’ummar kuwa komai ku]inka, to talaka aka ajiye ka, domin sarki yana da ikon ba ka umurni ko ya zatar da  wani hukunci a kanka. A hangen wasu ma cewa suka yi ko da ‘ya’yan sarauta idan ba su zamo sarakuna ba, to su ma talakawa ne.

### 3.1.2 Ta Fuskar Tattalin Arziki

A bisa al’adar Hausawa ana raba mutane ta fuskar }arfin tattalin arzikinsu. Wannan kaso ne ya bayar da damar nuna bambanci a tsakanin masu hali da maras hali na dukiyar ku]i da sauran }addarori. Mutane kan ga kansu da wani matsayi na daban a cikin al’umma musamman idan sun mallaki wasu ku]a]e. Za a tarar ana girmama su da yi masu fada idan dai har suna yin alhairi ga talakawan da suke zaune tare da su.

Wannan ya haifar da tazara a tsakanin masu ku]i da maras ku]i, sai zamana talakawa maras ku]i suke dogaro ga masu ku]i domin samun abin masarufi ta hanyar yi masu hidima ko }wadago da kuma a wasu lokuta neman tallafinsu.

### 3.1.3 Ta Fuskar {aurace-}aurace

{aura shi ne mutum ya bar muhallinsa na asali zuwa wani wurin da ba nasa ba a bisa dalilai mabanbanta. Idan mutum ya bar garinsu ya koma wani gari na daban, to anan ya sami kansa kenan cikin rayuwar ba}unci, irin wannan rarrabewar ya haifar da samun ‘yan gida da ba}i. Dangane da haka wannan kason jama’a yana lura ne da ‘yan }asa da kuma ba}i, ko ]an birni da ]an }auye.

### 3.1.4 Ta Fuskar Ilimi

Hausawa sun ce “Ilimi gishirin zaman duniya”. A kowace al’umma ta duniya ana bugun gaba da masanan da ke cikinta, domin su ne fitillun wannan al’umma a harkokin yau da kullum. Matsayin ilmi ne ga ci gaban }asa da bun}asarta ya haifar da ake ganin raba al’umma gida biyu, wato ta la’akari da masau ilmi da kuma maras ilmi daga cikin al’umma. Masu ilmi har kullum su ne ke da alhakin zartar da harkokin mulki da ayyukan

hukuma na gwamnati, su ne maras ilmi ke yi wa hidima domin su sami abin masarufin tafiyar da rayuwarsu da sauransu.

### 3.1.5 Ta Fuskar Ajin Shekaru

Ajin shekaru yana nufin a banbanta mutane ta fuskar shekarunsu na haihuwa. A tsarin zamantakewar Hausawa kowane rukunin jama'a sukan zauna ne ta 'yan tsaransu a fuskar shekaru. A irin wannan rabe-rabe ne aka sami rukunin yara da matasa da kuma tsofaffi. Dangane da haka, masu wannan ra'ayin kason sun tafi a kan cewa kowace al'umma ta duniya suna da rabuwa ta ajin shekaru inda za a sami yara-matasa-tsofaffi.

### 3.1.6 Ta Fuskar Jinsi

Jnsi kalma ce mai nuni ga namiji ko mace. Don haka, ana kasa al'ummar Hausawa zuwa gida biyu muhimmai wanda ya ha]a da jinsin namiji da kuma jinsin mace. A nan ana kula da ayyukansu da al'ada ta tanadar masu wajen rarrabewar, misali a bisa al'ada namiji shi ne ke zama uba mai ikon kula da gidansa da iyalinsa ta fuskar samar masu da abin masarufi da kare mutuncinsu. Ita kuwa mace al'ada ta tanadar mata haihuwa da kula da yaran da ta haifa wajen gina tarbiyyarsu.

## 4.0 Kammalawa

A cikin wannan darasi an yi }o}arin kawo bayanai da suka tabbatar muna da kashe-kashen mutane a zamantakewar al'ummar Hausawa. Darasin ya fito da hanyoyin da ake bi wajen kasa mutane rukuni-rukuni kamar yadda al'ada ta tanada.

## 5.0 Ta}aitawa

A ta}aice darasin ya yi magana ne game da azuzuwan mutane a cikin zamantakewar Hausawa a inda aka yi la'akari da yadda Hausawa suke kallon rukunin mutane ta fuskar matsayin sarauta da ilmi da ku]i da kuma jinsi.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Kawo kashe-kashen rukunin mutane a zamantakewar Hausawa.

2. Ta yaya }aura-}auracen al'umma kan taimaka wajen samar da wani kaso na ajin mutane?

## 7.0 Manazarta


Abdullahi I.S.S (2008). " Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa."Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria. Institute of Education.ABU Press.

Bichi A.Y (2013). Tsokaci a Kan Bukukuwan Hausawa na Gargajiya wajen cigaban Al'umma. Zaria. Ahmadu Bello University, Press.

CNHN (1981). Rayuwar Hausawa. Lagos. Thomos Nilson Nigeria Limited.

[angambo, A. (2008) Rabe-raben Adabin Hausa. Zaria, Amana Publishers.

Gusau, G.U (2012). Bukukuwan Hausawa. Gusau: Ol-Faith Prints.

Yahaya da Wasu (2001). *Darussan Hausa don {ananan Makarantun Sakandare.* Zaria. ABU Press.


## KASHI NA 2: Tsarin Iyali a Zamantakewar Hausawa

## 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an yi bayani ne dangane da ajin mutane a zamantakewar Hausawa, a nan kuma za a dubi tsarin iyali ne da ayyukansu a zamantakewar iyali na Hausawa.

## 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce a }arshen darasin ]alibi ya sami masaniya dangane da tsarin iyali a zamantakewar Hausawa  musamman a cikin gidan Bahaushe da ayyukan da suka ke~anta ga kowane daga cikinsu.

## 3.0 Mene ne Iyali?

Iyali kalma ce da ke nufin al'ummar da ke cikin gidan Bahaushe wa]anda suke aiwatar da rayuwarsu a }ar}ashin ikon maigida wajen bayar da umurnin a yi ko a bari. Dangane da haka, a tsarin zamantakewar a Hausawa kowane gida za a tarar yana tattare da wa]annan mutane da suke tafiyar da rayuwarsu  a }ar}ashin kulawar maigida, Daga cikin rukunin mutanen da ake samu a cikin gidan Bahaushe za a tarar akwai, shi kansa maigida, Matan gida, mahaifan maigida (kakanin gida), '}annan maigida, 'ya'yan gida, jikoki da kuma barwan maigida.

## 3.1 Matsayin Iyali da Ayyukansu a Gidan Bahaushe

A wannan kason kuwa za a dubi matsayi da ayyukan mutanen da ke cikin gidan Bahaushe ne ta la'akari a ayyukan da suka rataya ga kowane rukuni daga cikinsu kamar yadda za a gani a nan }asa;

### 3.1.1  Maigida da Ayyukansa

A tsarin zamantakewar Hausawa maigida sarki ne a cikin gidansa, domin shi ke da ikon gudanar da gidansa kamar yadda al'ada ta tanadar masa. Don haka, ayyukan suka rataya ga maigida ko magidanta a }asar Hausa suna da yawa, ga ka]an daga cikinsu kamar haka;

-Shi ne shugaban gida mai jagorantar al'umurran gidansa.

- Shi ke da alhakin samar wa iyalinsa muhalli da shata wa kowa inda zai zauna.
- Shi ke da alhakin samar da abubuwan more rayuwa a cikin gida kamar fitila da gyara ginin gidan idan ya soma lalacewa.
- Shi ke da alhakin ciyar da iyali a }alla sau uku a rana da duk abin da ke ala}a da ciyarwa kamar zuwa cefane, samo itace, ]ebo ruwa (idan babu a cikin gida) ds.
- Shi ke kula da lafiyar mutanen gidansa.
- Shi ke kula da duk bu}atocin iyalinsa.
- Shi ke kare mutuncin iyalansa.
- Shi ke sulhu a tsakanin mutanen gidan idan bu}ata ta taso.
-Shi ke sasanta rikicin a tsakanin iyalansa da na waje.
- Shi ke zuwa ko ya tura neman auren 'ya'yansa maza.
- Shi ke bayar da auren 'ya'yansa mata ko ya wakilta a aurar.
- Shi ke wakiltar gidansa a duk wasu al'amurran da suka shafi zumunci a waje ko ya wakilta.
- Shi ke kar~ar ba}i da sallamar su idan sun tashi.
-Shi ke za~e ko ra]a wa yaran da aka Haifa suna da yanaka masu dabbar suna.
-Shi ke da alhakin bu]e gida da kulle gida (safe da dare).
- Shi ke kula da tarbiyar iyalansa baki ]aya.
-Shi ke kula da hul]a da makwabtansa.
- Shi ke kula da karatun yara da mata.
- Shi ake nema idan ]aya daga cikin iyalansa suka yi laifi.
-Shi ne al}alin gidansa game da duk wanda ya sa~a wa dokokin gida da na al'ada.

**3.1.2 Matan Gida**

Wa]annan su ne rukunin matan da aka auro a cikin gidan Bahaushe daga wani gida. Da zarar aka aure mace a al'adar Bahaushe, to al'ada ta tanadi wa]annan ayyukan a kan matar da aka aura kamar haka;

-Kula da miji a kan abubuwan da suka shafi lafiyarsa, dukiyarsa, suturarsa, ]akinsa, rowan shansa, da na wankansa, butar alwarlarsa, mayafinsa, gadonsa, da tsaftace gadon da uwa uba yi masa ladabi da biyayya .

- Ita ke kula da harkokin gida musamman idan ya fita neman abinci.

- Ita ce mai haihuwa , shayarwa da kuma reno.

- Yin abinci a gida da dangoginsa, kamar daka, ni}a, tanka]e, sussuka da sauransu.

- Tsaftace farfajiyar gida baki ]aya.

- Tarbiyar 'ya'ya mata da maza }anana(koya masu abin da ya dace su sani, karma shara, wanke-wanke, ladubban matantaka, girki ds).

- Kula da makwabta mata da suke hul]a da gidan.

- Kula da bukukuwan da suka shafi gidan.

- Tabbatar da an kiyaye dokokin miji na cikin gida.

- Ita ce likitar gida wajen kula da bayar da magani ga yara.

- Ita ce mai kula da dabbobin gida.

### 3.1.3 {annan Maigida

Zamantakewar Hausawa kamar yadda aka sani zama ne irin na gandu in da ake samun mutum da iyalansa da }annansa da iyayensa duk a gi]a. Hakan ya sa wannan darasi ya gay a dace ya fito da ayyukan }annan maigida a cikin gidan Bahaushe kamar haka;

-Su ne suke wa}iltar maigida a wajen taron aure ko suna ko wani bukin al'ada.

-Su ne ke tsawata wa yaran gida idan sun yi ba daidai ba.

-Su ne ke taimakawa wajen aiwatar da wasu ayyukan kula da gida.

-A wajen su ake neman auren 'yar maigida idan ta kama.

### 3.1.4 Kakanni

Wa]annan suna da babban matsayi a gidan Bahaushe. Domin Su ne iyayen maigida da suka haife shi, don haka ake girmama su a cikin gidan Bahaushe. Daga cikin ayyukansu a cikin gida sun ha]a da;

- Kula da duk wata mata da haihu a cikin zuri'ar gidan.
- Shiga tsakani wajen tabbatar da mijin da jikokinsu mata za su aura.
- Jawo hankalin maigida bisa wata matsalar gidansa, musamman a tsakaninsa da matansa ko ]iyansa ko makwabtansa.
- Yi wa jikokinsu tatsuniya da ba su mafaka idan sun yi laifi.
- Wasa da jikokinsu da kwantar masu da hankali .

### 3.1.5 'Ya'ya

Duk wani ko wata da ke a }ar}ashin kulawar maigida wadda aka haifa a gidan ko aka ]auko ri}o ko kuma aka zo da ita a matsayin agola, to su ne ake nufi da 'ya'yan gida. Su ma suna da ayyukan da suka ji~ince su kamar haka;

- Su ke da alhakin biyayya ga iyeyensu maza da mata.
- Su ke aiwatar da }ananan ayyukan cikin gida kamar kai ni}a da fa]in haihuwa da share gida da wanke kwanoni.
- Su ke kai sa}on kunya ga maigida a cikin gida.
-

### 3.1.6 Jikoki:

Su ne 'ya'yan da maigida bai haifa da cikinsa ba, irin wa]annan su ne da ]iyan maigida suka haifa kuma suke zaune a wuri ]aya. A bisa al'ada akwai wasa a tsakanin maigida da jikokinsa maza da mata. Daga cikin ayyukansu a cikin gida kuwa sun ha]a da;

- Yin biyayya ga iyayensu da Kakaninsu da suke a cikin gidan.
- Aiwatar da }ananan ayyukan cikin gida kamar sauran yara.
- Wasanin barkwanci da kakanninsu da suke a cikin gida.

### 3.1.7 Barwan Maigida:

Su ne masu yi wa maigida hidima a cikin gidansa ko a gonarsa ko kuma a masana’antarsa. Irin wa]annan mutane suna aikin kula da lamurran gida ne domin samun ladan aikinsu ga maigida. Daga cikin ayyukansu kuwa sun ha]a da;

-Aiwatar da duk wasu ayyuka masu nauyi/wuya kamar kula da ciyarwa doki, ko faskare ko saro itace ko wankin yaran gida da iyayensu tare da goge tufan a wasu lokuta sukan kula da shagunan maigida ds.

## 4.0 Kammalawa

A wannan darasi an fito ne da tsarin iyali a zamantakewar Hausawa da kuma irin yadda ake ganin su a dun}ule tamkar tsintiya a kodayaushe. A cikin bayanan an amfana ga sanin ire-iren ayyukan da suka rataya ga kowane rukuni na mutanen da suke a cikin gidan Bahaushe kama daga maigida kansa har zuwa ga barwansa.

## 5.0 Ta}aitawa

A ta}aice darasin ya tattauna yadda al’ummar Hausawa suka shahara wajen zama a wuri ]aya da kuma taimakon juna ta fuskar al’adun zamantakewa. An kuma kawo ayyukansu a ciki da wajen gida domin a tabbatar da zaman lafiya da lumana.

## 6.0 Auna Fahimta

1. A tsarin zamantakewar Hausawa bayyana fitattun ayyukan maigida a ciki da wajen gidansa.
2. Mata a wajen Bahaushe suna da rawar da suke takawa wajen kula da iyali. Tattauna tare da misalai.
3. Fayyace ayyukan barwan maigida a tsarin iyali na Hausawa.

## 7.0 Manazarta

Abdullahi I.S.S (2016) “Laccar Ajin ALH 402: Hausa Culture II”.Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Jami’ar Usmanu Danfodiyo, Sakkwato

Ann.B, Cultural studies, New Historcism: An over view of cultural studies.

Bunza A. M 2006: *Gadon Fe]e.* Ibrash publications ltd, Lagos.

CNHN (1981). Rayuwar Hausawa. Lagos. Thomos Nilson Nigeria Limited.

Sarkin Gulbi, A 2015: *Gender Conflicts in Hausa Proverbs.* Paper published in conference proceedings on Folklore, organized by BUK.

## KASHI NA 3 : Al’adun Aure A Rayuwar Hausawa

### 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna yadda al’ummar Hausawa suka shahara wajen zama a wuri ]aya da kuma taimakon juna ta fuskar al’adun zamantakewa. An kuma kawo ayyukansu a ciki da wajen gida domin a tabbatar da zaman lafiya da lumana. A wannan darasi kuwa, za a duba al’adun Aure a zamantakewar Hausawa. Don Haka, kamar yadda aka sani aure yana ]aya daga cikin matakan rayuwar kowace al’umma ta duniya,ba ma Hausawa ka]ai ba,kuma shi ne mataki na farko na samar da al’umma ta gari.Al’ummar Hausawa ba }aramin muhimmanci ta bai wa lamarin aure ba tun gabanin da kuma bayan saduwarsu da addinin Musulunci.Kazalika akwai nason magani sosai a cikin sha’anin auren Bahaushe,tun daga neman auren,da zaman auren da kuma matakan rabuwar auren.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce daga }arshen darasin ]alibai su sami masaniya dangane da yadda al’adun neman aure da zamantakewar auren Hausawa yake a jiya da kuma yau.

### 3.0 Ma’anar Aure

Aure kamar sauran ~angarorin al'ada ya samu bayanai ta fuskar ma'ana kamar haka; A gaskiya zai yi wuya kai tsaye a ce ga ma'anar aure guda ]aya kar~a~~iya kuma gamsasshiya ga al'umma baki ]aya.Wannan kuwa ba zai rasa nasaba da ganin cewa, kowace al'umma tana da yadda ta ]auki aure ba. Bisa ga wannan ne masana ilimin zamantakewa (*Sociologists*) da ]aliban al'adun al'umma musammam na Hausawa suka kawo ra'ayoyinsu dangane da ma'anar aure. M A Rauf (1970:78) ya bayyana cewa; bisa ga shari'ar musulunci aure shi ne:

> {ulla wata yarjejeniya da za ta haifar da
> halaccin saduwa da mace da samun zuri'a.
> Kuma wani bangare ne na mu'amula da ibada.

Habibu Alhassan da wasu (1980, da 1982) sun ha]a hannu suka ba da ma'anar aure kamar haka:

> Aure ala}a ce ta halaccin zaman tare tsa}anin namiji da mace. Ana yin sa ne saboda abin da aka haifa ya sami asali da mutumci da kiwon iyaye. Kuma shi ne maganin zina da 'ya'ya marasa iyaye.

Wannan ma'anar ta nuna aure zamantakewa ce a tsakanin namiji da mace tare da amincewar juna. Ita kuwa Fatihiya Migdad Sa'ad (1998:196) tana da ra'ayin aure a Musulunce shi ne:

> Aure shi ne halaccin zaman namiji da mace
> tare da cika wasu dokoki , tare da ba kowa nasa
> hakkin zamantakewa a tsakaninsu. Wannan
> yarjejeniyar ta zama tare kuma za a yi ta bisa
> koyarwar addinin Musulunci wanda ake samu
> a cikin al'}ur'ani da hadisan manzon Allah (SAW).

Yarjejeniya ce ta halaccin zaman tare a tsakanin namiji da mace domin kyautata

mutunci,da abin da aka haifa da kuma kariya daga aikata zinace-zinace.

Shi kuwa Ibrahim da wasu (1986) cewa suka yi:

> "Aure wata hanya ce ta }ulla zaman tare tsakanin
>
> namiji da mace ba tare da iyakancewa ba,sai dai
>
> in mutuwa ta raba,wanda ake tabbatarwa ta hanyar
>
> ma'auran da waliyyansu da kafa shaidu."

Suna nufin cewa aure shi ne zaman tare a tsakanin namiji da mace da akan }ulla ta hanyar ma'auran, da waliyai,da kuma shaidu.Wannan ma'anar ta kusanci kawo muna

abubuwa muhimmai na aure da ya shafi addinin Musulunci,duk da yake ba su ce komai ba a kan sadaki.

Sarkin Sudan (1999)cewa ya yi:

> “Aure hanya ce ta rayuwa mai ]orewa tsakanin mace
>
> da namiji wadda akan gina ta hanyar shimfi]a]]un ka’idoji
>
> da al’umma ta tanada wanda kan haifar da nisha]i tsakanin
>
> ma’aurata da taimakon juna da samar wa ‘yayansu asali
>
> da kyakkyawan reno.

Shi ma wannan ya tafi a kan cewa ala}a ce ta zaman tare a tsakanin namiji da mace da akan ha]a bisa shimfi]a]]un }a’idoji da nufin samar da nisha]i da taimakon juna,da kuma zuri’a ta gari.

To ke nan,aure shi ne halaccin zaman tare da ake }ullawa a tsakanin namiji da mace. A bisa yarjejeniyar ma’aurata, da waliyansu,da kafa shaidu, da sadaki,da nufin ]aukar ]awainiyar matar domin samun zuri’a ta gari da kaucewa aikata zina.

### 3. 1 Bukin Aure

A }ar}ashin wannan fasali za a yi bayani ne dangane da al’adun da ke tattare a neman aure da bukin aure da tasirin zamunanci a cikin sha’anin aure a }asar Hausa. Sai dai kafin nan zai kyautu a ]an bayar da bayani a kan ma’anar aure a cikin al’ummar Hausawa daga bakin masana da manazarta.

### 3.2 Tsarin Neman Aure A Al’ummar Hausawa

Neman aure a cikin al’ummar Hausawa wani abu ne da ke da tsari da matakai da ake bi wajen tabbatar da shi, samuwar wa]annan matakai suna taimakawa ainun wajen gina al’umma ta gari. Ka]an daga cikin wa]annan matakan kuwa sun ha]a da;

#### 3.2.1 Soyayya Tsakanin Saurayi Da Budurwa

Soyayya ita ce }auna ta wani mutum ko wani abu daban. A zahiri an fi amfani da wannan tsakanin namiji da mace musammam saurayi da budurwa. Soyayya a harkar aure wata abu ce mai muhimmancin gaske ga auren Hausawa. Idan babu soyaya da wuya a iya zaman aure, don haka, soyayya ita ce }ashin bayan zaman auren Hausawa da ma sauran

al’ummun da ba su ba. Duk da yake ana iya samun zaman aure ba tare wata soyayya ba. Misali irin auren na kama da Hausawa kan yi a wasu lokuta, ko kuma a ce auren tilas.

### 3.2.2 Tsarin Soyayya a Al’adar Hausawa:

A al’ummar Hausawa, tsarin soyayya kan taka muhimmiyar rawa a tsakanin saurayi da budurwa. Galibi wannan soyayyar ita ke }ara dan}on zama tare wanda zai haifar da aure. Bincike ya gano cewa, al’ummar Hausawa suna da soyayya iri biyu ne zuwa uku .Ga su kamar haka:

- Soyayyar da ke haddasuwa saboda ha]uwar jini tsakanin saurayi da budurwa. Wannan yana iya shafuwar }irar jikin saurayi ko budurwa.
- Soyayya saboda kyawawan ]abi’un mutum.
- Soyayya saboda hali (arziki) watau ana samun ginuwar soyayyar Bahaushe saboda irin arzikin gidan saurayi ko budurwa.

Duk wa]annan nau’o’in soyayya suna ginuwa ne ya yin da saurayi zai rin}a ganin budurwa yana yi mata wata ‘yar kyauta. Bincike ya gano cewa an fi samun soyayya ta zahiri a tsakanin saurayi da budurwa kafin zuwan addini Musulunci. Don haka, muna iya cewa soyayya  a wannan zamani ta yi }aranci, don an maye ta da sha’awa . Za ta yi yu saboda rashin wannan soyayya ake samun yawaitar mutuwar aure a cikin al’ummar Hausawa a yau. Domin ita sha’awa gushewa ta ke, amma soyayya ba ta gushewa. Hasali ma soyayyyya ga Bahaushe a wancan lokacin ta dogara ne a kan irin bajinta da kirkin saurayi, domin ba a duban arzikinsa balle a dubi abin da za a samu daga cikin arzikinsa ko na gidansu.

Wani abin kulawa a nan shi ne , ga al’adar Bahaushe saurayi ke ganin budurwa ya ce yana so, duk da yake a al’ada da addinin  Bahaushe ba a yarda saurayi ya rin}a cu]anya da ‘yanmata a tsakaninsu ba. Don haka, lamarin soyayya abu ne mai muhimmamci ga zamantakewar neman auren Hausawa, musamman a }asar Hausa.

### 3.2.3 Al’adar Zance ko Ta]i

Wannan shi ne zuwa hira da saurayi kan yi a gidan Budurwa ko wani muhalli na daban da suke ha]uwa a wani lokaci na musamman . Galibi a irin wannan hirar (zance) ana tattauna lamurran yau da kullum ne.

#### 3.2.3.1 Tsarin Zance a Al’adar

Al’ummar Hausawa kamar sauran al’ummu sun ba wannan al’ada muhimmanci sosai . Don haka, sun tanadi wani tsari na musammam domin aiwatar da ita. Ganin cewa, an fahinci irin ha]arin da ke tattare da wannan al’ada, sai aka tanadi lokaci da wuri na aiwatar da wannan al’ada. Domin ba su yarda su bar ‘ya’yansu mata ba tare da sa ido da jagoranci ba. Da farko za mu ga cewa wannan al’adar sai da dare ko yamma ake yin ta, kuma galibi gidan budurwa ake zancen, inda ake samun gidin bishiya ko zauren gida a zauna ana hira, duk da yake zamani ya kawo ana hira da ‘yan mata a cikin mota.

A cikin al'adar akwai tsarin zuwa da 'yar rakiya, kuma al'ada ba ta yarda saurayi ya rin}a zuwa zance kullum ba, wanda yake galibi an fi zuwa zance ranar kasuwar garin. Akwai al'adar ba da ku]in jin-kira. A da, akwai al'ada ta tsarance inda saurayi zai rin}a zance da budurwa har ta kai su kwana ]aki ]aya, amma saboda gaskiya da aminci ba za su san juna ba. Wannan al'adar ta kau a halin yanzu, saboda tasirin addini Musulunci a cikin sha'anin rayuwar al'ummar yau.

### 3.3 Shigar Iyaye Wurin Neman Aure

Bisa ga tsarin neman auren al'ummar wannan gari, iyaye suna da muhimmanci. Da yake aure al'ada ce da ake yi domin zaman rayuwa baki ]aya, don haka, addini da al'ada sun aza ma iyaye ha}}in nemar wa 'ya'yansu matar aure. Iyaye suna bi]ar ma 'ya'yansu aure a gida mai asali domin su suka san tarihin gidajensu, kuma suna da masaniyar halin tarbiyar gidan. A nan, iyaye suna kulawa da wannan ne domin kaucewa gur~ata zuriyarsu da wani jini mai tarihin wani abin kunya. Misali sata ko wata cuta ta musamman kamar kuturta.

A lokacin neman auren, iyaye suna duban inda yarinya za ta samu abinci. Domin abin kunya ne ga Bahaushe ya ba da aure ga gida wanda ba ya ciyar da matarsa.

### 3.4 Fitowa Gida (Bi]ar Iyaye)

Iyaye suna fitowa bi]ar aure ne idan sun tabbatar da mutumcin gidan da za su neman auren. A nan, idan za su fita sukan ta fi da goro da 'yan wasu ku]i da za a aza sama. Mafi yawa akan samu dattijai ne 'yan uwa su kai wa]annan kaya. Duk da yake a yanzu ana samun masu ba da auren ba tare da sanin dangin uwa ba balle na uba. Bisa ga tsari, idan iyaye suka isa gidan yarinya, bayan sun gaisa, sai su bayyana abin da ke tafe da su. Ana wannan neman ne a wurin iyayen yarinya ko wani danginta na jini kuma namiji. A wannan lokacin sai iyayen yarinya su ma su fa]i nasu bayani na amincewarsu ko rashin amincewa. Duk da haka, wani lokaci tun yarinya na ciki ko jaririya ake fara neman aurenta ta hanyar ba da zobe da za a sanya mata mai nuna an yi kamen ta kenan.

### 3.5 Gaisuwar Abokai

Wannan wani mataki ne daga cikin tsarin al'adun neman auren HausawanKasar Hausa. Abokai su ne wa]anda mutum ke zaune da su lafiya suna yawo tare da cin abinci tare da dai sauran mu'amaloli. Ita wannan al'ada ana yin ta ne bayan Saurayi da Budurwa sun sasanta kansu da niyyar auren juna, kuma iyaye sun isa gida neman auren an kuma amsa saurayin ya ci gaba da neman auren. A nan ne saurayi zai samu abokansa domin su fito gaisuwa. A irin wannan lokacin ne ake tura abokai gaisuwar sanin dangin yarinyar.

A al'adance, idan za a tafi wannan gaisuwar, ana zuwa da goro ne da wasu 'yan ku]i wanda za su rin}a bayarwa. Lokacin wannan gaisuwar, saurayin da ke neman auren ba

ya magana sai dai abokansa su yi. Wannan al'adar ana yin ta ne domin gabatar da saurayi ga sauran dangi domin su san shi, ya san su.

### 3.6 Tsarin Na-Gani-Ina-So A Al'adar Aure

A al'dar neman aure da bayar da shi a wannan yanki, bayan magana tsakanin saurayi da budurwa da iyayen yaro da na yarinya ta zauna , watau an amince wa juna. Daga nan ne za a kai kayan na-gani-ina –so, su wa]annan kayan galibi ana samun wasu dattijai maza ko mata ne su kai wa]annan kayan, za~en dattijai ba zai rasa nasaba da irin matsayinsu a cikin al'umma ba, domin sun fi sanin irin lafuzzan da za su yi amfani da su. Galibi wa]annan kaya ana ha]awa da 'yan wasu ku]i da goro a ciki, sauran kayan sun ha]a da tufafin sanyawa da na kwalliya. A nan yawan kayan ya danganta ne da irin }arfin arzikin gidan saurayi.

Bayan an kai wa]annan kayan ne za a dawo da bayanin da aka samo daga gidan budurwa dangane da kayan.Wa]annan kayan za a rin}a yawo da su gida-gida ana nuna ma dangin yarinya , wani lokaci ma, goro da ku]in da aka aza sama ana rabawa sauran dangin shaidar cewa 'yarsu ta sami masoyi/miji. Duk da yake kafin shigowar addini, Hausawa suna amfani da kayan gona ne da wuri a matsayin kayan na-gani-ina-so. Zamunanci ya kawar da wannan.

### 3.7 Bukin Aure

Bayan an haye dukkan wa]annan matakai da aka lisafa sama, abin da zai biyo baya shi ne, shagalin buki. Bukin aure kan fara ne tun lokacin shiga shirye-shiryen saka amarya lalle zuwa kai amarya ]akin mijinta. Kafin saka amarya lalle akwai al'adar lefe da akan kai a gidan amarya daga gidan ango, duk da yake wasu iyaye sukan yi hani ga aiwatar da wannan al'ada. Abin la'akari a nan shi ne, sha'anin neman aure da bukin auren al'ummarKasar Hausa a halin yanzu cike yake da nason zamunanci da ba}in al'adu kamar yadda za a tattauna su a nan gaba.

#### 3.7.1 Nason Zamunanci Cikin Al'adun Nema Da Bukin Auren Hausawa

Hausawa na cewa "Zamani riga ne". Ba shakka zamani ya kawo canje-canje masu yawan gaske a cikin auren Hausawa da ma sauran al'ummar Hausawa tun daga neman aure har zuwa ]aurinsa. Dalilin shigowar zamani ya kawo sababbin abubuwa cikin sha'anin auren Hausawa da kuma yin watsi da wasu tsofaffin abubuwan da aka saba da su. Alal misali, a zamanin da iyaye ke nema wa 'ya'yansu aure ga iyayen yarinyar da suke son ya aura. Ba yara ke za~i da kansu ba a da, iyaye ke yi musu za~in wadda za su aura domin yaro bai san abin da ya fi cancanta gare shi ba bale ga waninsa. A kan wannan ne Hausawa suka ce "Ta yaro kyau gare ta ba ta da }arko." Ba a zancen neman aure ka]ai ba, akwai nason zamananci a sauran matakan neman aure. Wa]annan sun ha]a da kayan toshi da kayan zance da dukiyar aure har da sa rana. Zamananci ya yi tasiri sosai domin ana sanya ranar ]aurin aure, sai yaron da ke neman auren ya ce ranar da aka saka domin ]aura aurensa ba ta yi masa ba domin wata 'yar matsalar da ba ta kai ta kawo ba, ba tare da la'akari da yi

wa iyayensa ]a'a ba. Wannan na }ara tabbatar da nason zamananci a cikin matakan neman auren Hausawa. Ai shi ya sa [anmaraya Jos ya yi wa}ar biyayya ga iyaye tare da barin sa~a musu. Ga abin da ya ce:

"Yan yara ku bi ma iyaye,
Ku bi malaman makaranta,
Irin haka Allah ke so."

Bayan wannan kuma, akwai wata mawa}iya, Fati Nijar a cikin wa}arta mai suna Alan Gidigo da ta }ara tabbatar da zancen da ke sama, kan cewa zamani ya yi naso }warai cikin matakan neman aure na Hausawa. Ta goyi bayan 'ya'ya mata da su yi tsaye su za~i wanda suke so ba wanda aka so musu ba. Ke nan a nan tana horo ne ga 'ya'ya mata da ka da su kuskura a yi musu za~en tumun dare. Ga abin da ta ce:

Jagora: Ke yarinya za~i dogo
'Y/Amshi: Ke yarinya za~i dogo
Jagora: Za~i dogo na [anwuro dokin Iyani
'Y/Amshi: Ala gidigo".

Idan aka yi la'akari da abin da Fati Nijar ke kira kansa za a fahimci tana yi ne domin 'ya'ya mata su yi wa iyaye bore kan cewa za~ar musu mazan aure da ake yi ya ishe su don haka a bari kowa ta za~a wa kanta mijin da take so da aure.

### 3.7.2 Nason Sutura

Wannan ba abu ne da ke ~oye ba bale a yi dogon bayani kansa. Idan ba a samun sa gidan kowa da kowa, zan ce mafi yawan gidaje ana samu. Daga cikin suturun, wasu na ba}i ne wasu kuma na gida ne. Akwai nason tufafin Turawa da Larabawa da Indiyawa da Faransawa da sauransu da yawa. Wannan kuma ya faru ne sanadiyar kalle-kallen fina-finan wa]annan mutane a cikin talabijin da hotunan kalanda. Ai mafi yawa daga cikin mawa}an Hausa na fina-finai da ke wannan }asa tufafinsu na mutanen }etare ne musamman mata. Akwai ]inki kala-kala da Hausawa suka ]auka matsayin ba}in al'adu a lokacin bukin aure da suka ha]a da ***fitted*** ***(****Mai matse jiki****)*** da ***umbrella*** *(mai fa]i)* da ***pre-fitted*** da ***gown*** (Doguwar riga) da ***half gown*** **(**Rabi waje**)** da ***stella (****Rigar yayi)* da ***show me your back*** **(**In ga bayarki**)**da **buba (**Fa]i ko shan iska**)**da **wasila** (rigar yayi) da sauransu. Da jin wa]annan sunaye babu kokanto sunaye ne na wasu al'ummu da ba Hausawa ba. A nan ne za a ga yarinya ta ci ado, idan aka gan ta a cikin bidiyo za a zaci Ba'indiya ko Balaraba ko Baturiya ce idan aka yi la'akari da tufafin da ta sanya. Idan aka bincika za a tarar Bahaushiya ce wata }ila ma ta Kebbi ko Kano ko Katsina ko Sakkwato ko Zamfara. Mai son gane wa idonsa ya je wuraren da aka ambata a sama a lokacin bukin aure zai tabbatar da cewa ba}in al'adu sun }ara wa Borno dawaki ta fuskar al'adun auren Hausawa.

Haka kuma, idan aka dubi gida Nijeriya za a ga irin saka/sanya wannan sutura ta wasu }abilu ta yi naso a cikin al'adun Hausawa na aure musamman Yarbawa da Inyamurai, duk da ba nasu ka]ai suka yi nason ba. Hausawanmu sun ]auki al'adar Yarbawa ta ]inka tufafi iri ]aya ba tare da samun bambanci ba a lokacin bukin aure. Yarbawa na kiran wannan ***Oshobe (I shall be)*** ko Anko. Bayan wannan ma abin haushi shi ne ]inkin lalaci ba na mutumci ba. Akwai wani ]inki da ake yi wa yara 'yan mata mai suna "Saka]a-hannunka–masoyi" a inda za a iya ganin hamutar yarinya ko da daga nesa bale kusa. Akwai a matse }ugu. Akwai irin wa]annan ]unkuna da yawa ba wannan ka]ai ba. Zamani ya yi sanadiyar canje-canje masu yawan gaske a cikin al'adun Hausawa ta fuskar aure. Haka kuma, al'adar ~arnar ku]i a ~angaren ]inka tufafi a lokacin bukin aure ya zan ya yi. Kai! Kitson da 'yan mata ke yi ma ba na Hausawa ba ne a lokacin bukukuwan aure. Ko dai ya kasance na Yarbawa ko na Ibo ko wasu }abilu na daban, kuma kowane da nasa suna. Duk abin da aka fa]i a ~angaren mata ana samun wani abu a na maza sai dai, abubuwan sun fi naso a ~angaren dangin Shai]an (mata). Haka kuma a Katsina akwai wata fita da ake kira ***Arabian night*** inda ake yin fitar Larabawa a lokacin bukin aure, duk da yake wannan ~arnar ba ta kawo ba. A ~angaren maza jallabiya fara suke sanyawa mata kuwa ba}a suke sanyawa. Don gudun faruwar wannan ne Sarkin taushin Katsina ya yi wata wa}a ta '**FESTAC 77**' inda yake horon Hausawa yara da manya yana cewa:

Jagora:Yara-yara 'yan makaranta,
: Manya da }an}ananku ku ]au horona
'Y/Amshi: Ku kama al'adu na iyayenku
: Kar ku yarda da aikin banza
Jagora: Sai ku kama al'adu na iyayenku,
'Y/Amshi: Kar ku yarda da aikin banza
Gindin Wa}a: Nufinta ne wasan gargajiya,
:Ta sa mu }ara fahintar juna.

Wannan mawa}i ya yi horo ga dukkan al'ummar Hausawa tare da jan hankalinsu domin su ri}e al'adunsu da hannu biyu ba tare da sanya wasa ko abin da zai aibata al'adun ba, kar su aminta da wasu ba}in al'adu bale ma su fifita su a kan nasu (*xenocentrism*). Ga abin da ya }ara fa]i dangane da wannan:

Jagora: Gwannati tana da yawan jama'a,
: Garga]i ga babba da yaro,
'Y/Amshi: Kowa ya kama al'adunshi,
:Akwai wa]ansu mutane,
:Sun yar da nasu sun bi na 'yan cirani.
Gindin Wa}a: Nufinta ne wasan gargajiya,
:Ta sa mu }ara fahintar juna.

Tabbas gaskiya ce maka]a ya fa]a domin akwai wa]anda suka fifita al'adun wasu a kan nasu ba tare da yin la'akari da aibin watsi da nasu ba, ta hanyar rungumar na wasu. Allah Ya sawwa}a![1]

### 3.7.3 Nason Al'adun Ki]a da Wa}a

A nan, ba abin musu ba ne domin ya zama ruwan dare game duniya a }asar Hausa. A wannan zamani nason ba}in al'adu na ka]e-ka]e da wa}e-wa}e sun yi naso sosai a cikin al'adun auren Hausawa kuma ba mai tada hannu ya ce ba haka abin yake ba. A ta}aice, sanin kowa ne cewa mafi yawan Hausawa sun yi watsi da ka]e-ka]en gargajiya da raye-rayensu suka cirata zuwa ga na ba}i. Mafi yawan kayan ki]an Hausawa an fara watsi da su domin sun zama tsohon ya yi, aka rungumi wa]anda ba su kai su daraja ba kamar yadda Sarkin Taushin Sarkin Katsina ya yi bayani. A zamanin da ake ciki an yi jana'izar mafi yawa daga cikin kayan ki]an Hausawa da suka ha]a da kalangu da ganga da duma da }aho da kuge da kurya da kotso da dundufa da taushi da sauransu sai dai ka]an da ba a rasa ba. Ko su ma domin kada a rasa wuta ne a ma}era ko kada a rasa nono ruga. Ba shakka, an koma ga kayan ki]an zamani irin jita da fiyano da gangunan bigala da sauran irinsu. Har ta kai ga ba a gayyatar maka]in da ke amfani da kayan ki]an gargajiya zalla sai can ba a rasa ba ko shi a }auyuka da ka]an a cikin birane domin }auyawan da suka kwararo ciki. Mafi yawa idan aka saurari maka]an Hausa tare da yin la'akari da kayan ki]ansu za a tarar sun saka kayan ki]an zamani cikin ki]an da suke yi. Misali, [andago da Mai Asharalle a Katsina da Sarkin [ori a Sakkwato da wasu da dama. Mafi yawan ka]e-ka]en da ake yi a cikin wa}o}in bukin aure sigar wa}o}in ba}i suke ]auke da su.

Idan aka yi zancen wa}e-wa}e kuwa, ba sai an yi dogon bayani ba domin abubuwa ne da aka shedar a wannan zamani. Maimakon wa}ar gargajiya da sautin gargajiya, sai aka musanya da na ba}i inda za a ji muryar Turawa ko Indiyawa ko Larabawa da sauran 'yan }asa ma}wabta irin Yarbawa da Ibo da sauransu.

### 3.7.4 Nason Al'adar Fati Da Fikinik

A da, ba fati ko fikinik Hausawa ke yi ba. Abin da suke yi shi ne 'Ajo' domin taimaka wa ango ya samu abin tarbon amaryarsa. Maimakon wannan sai aka sami nason ba}in al'adu na yin fati da fikinik a lokacin bukin auren Hausawa. Fikinik ba komai ba ne sai iskancin da ake yi a cikin daji da Hausawa suka ara suka yafa domin ganin an yi da su ba tare da an bar su a baya ba, kuma ba tare da sanin manufarsa ba. Ba komi ya haddasa wannan ba sai kalle-kallen fina-finan da ake yi na zamani. Wani abin da ya kamata a sani a nan shi ne, babu ~arnar da ba a yi a wajen fati da fikinik. A daji ake yin fikinik. Fati kuwa, a cikin gari ake yin sa. Sai dai saboda ci gaban mai ginar rijiya da ya sa Hausawa suka samu na ~atar basira, an fara barin garin da ake bukin aure a je wani gari a yi hayar otel domin a yi fati can. A can ne mafi yawan samari da 'yan mata ke fa]awa a tarkon she]an na zina, abin da ke sanadiyar gur~atar tarbiyyar al'umma baki ]aya. Za a fahimci cewa

[1] Bunza, D.B, "Zama da Madauki kanwa ke sa farin kai: Nason bakin al'adu a cikin al'adun Auren Hausawa," Mu}alar da aka gabatar a taron }ara wa juna sani na }asa da }asa kan ta~ar~arewa al'adun Hausawa. A Jami'ar Umaru Musa 'Yar Adua da ke Katsina. 2013, Shafi na 7-11.

wa]annan al'adu na waje ne ba na gida ba, sun yi nason gaske a cikin na Hausawa musamman a bukukuwan auren zamanin yau.

### 3.7.5 Nason Shaye-Shaye

Shaye-shaye kala-kala ne. Akwai na ruwa da kuma sandararre. Ban ce babu al'adar shaye-shaye a cikin al'adar Hausawa ba, sai dai ba}in al'adun shaye-shayen wasu al'ummu sun yi naso sosai ga rayuwarsu a lokutan bukukuwan aure. Ya dace a san da cewa, shaye-shayen da Hausawa ke yi ba domin bukin aure ne ko wani abu da ya yi kama da haka nan ba. Suna sha ne saboda wata bu}ata ta daban musamman wani aiki da ya kai wa mai shi gaya. Su kuma ba}in na yin shaye-shaye ne da nufin jin da]in rayuwa da kuma nuna wayewa. Idan aka dubi mawa}an waje irin Bob Marley da Michael Jackson da sauransu, suna sha ne domin jin da]in gudanar da aikinsu na wa}a. Sai dai kayya! Ganin wannan a cikin fina-finai ya sanya wasu Hausawa rungumar sa ba tare da wata fargaba ba. Sanin kowa ne cewa shaye-shaye aibi ne. Wasu na yin shaye-shaye ne domin samun raguwar damuwar rayuwa, suka manta da na}asar rayuwarsu da suka samu. Idan aka yi la'akari da cikin gida Nijeriya za a ga cewa Hausawa sun sami nason al'adun ba}in da ake tare da su kamar Yarabawa da Ibo da sauran }abilu ma}wabta. Nason ba}in al'adu ya sa shahararren maka]in nan Marigayi Alhaji Mamman Shata Katsina, a wa}arsa mai suna 'A sha ruwa' yake nuna irin holewar da aka saba da ita sanadiyar mu'amala da ba}i. Ga ka]an daga cikin wa}ar:

> Jagora: Ya bisimil ilahi,
> 'Y/amshi: Jalla ubangiji, sha ruwa,
> Jagora: Ka ji karatun masu bugun ruwa,
> Wa]anda ke zikiri a kuloniyal,
> 'Y/Amshi: Sha ruwa ba lahani ba ne,
> Jagora: A nan muke sallarmu ta jumma'a,
> 'Y/Amshi: A sha ruwa ba lahani ba ne
> ……………………………………..

Allah Ya ji}an rai! Wannan ya nuna ke nan wa]annan abubuwa sun faru ne sanadiyar nason ba}in al'adu, kuma yakan iya faruwa ga kowa domin tsaka mai wuyar sani ce.

### 3.7.6 Nason Gur~acewar Tarbiyya

Na yi }udurin bayyana irin ala}ar da ke tsakanin miji da matarsa da kuma iyayen miji da matar. A da, ba yadda za a yi a sami rashin kirki tsakanin surukai da sarukarsu, wato matar ]ansu, a bayyane kuma da gangan sai da aka fara samun nason ba}in al'adu. Idan aka yi la'akari da wannan ala}a a wannan zamani za a ga bambancin da ke akwai ba ka]an ba ne. Wula}anta iyaye al'adar mutanen banza ce. Haka kuma, Turawa na daga cikin wa]anda ke wula}anta iyayensu musamman idan sun cimma shekarun tsufa. Sai ga shi wannan al'ada ta yi naso cikin al'adun Hausawa na aure inda za a sami matar yaro ba ta san girman iyayen mijinta ba bale ta girmama su. Ko miji ya tarar da matarsa ta ci mutumcin iyayensa, ba zai yi wani bincike ba, sai ya fa]a iyayensa da fa]a wai su ke da

laifi musamman wasu ‘yan boko da ke barin iyayensu a }auyuka su koma birni suna kece raini da jin da]i iri-iri. An sha samun matsalar rashin ]a’a da matar miji ke yi wa iyayensa, wani lokaci ma har kotu matar ]a ke kai iyayensa domin ganin sun kula mata, suna damuwarta. A fahimtata ]an ne ya wula}antar da iyayensa ba matar ba. Ita kuma matar halin da ta nuna a gidan surukai ya tabbatar wa al’umma cewa ba a koyar da ita tarbiyyar kirki ba a gidansu. Duk wa]annan halaye da ake samu sun faru ne sanadiyar nason ba}in al’adu a cikin al’adun Hausawa na aure.

## 4.0 Kammalawa

A cikin wannan darasi an ga yadda Hausawa suke aiwatar da wasu muhimman al’adunsu na aure da kuma irin kutsen da zamani ya yi a cikin sha’anin nema da kuma bukukuwan auren Hausawa. Duk a cikin darasi an kawo fahimtar masana al’ada da zamantakewar [an Adam game da ma’anar aure.

## 5.0 Ta}aitawa

A ta}aice darasin ya mayar da hankali ne wajen fayyace al’adun aure a cikin zamantakewar Hausawa, inda aka fito da yadda al’ummar Hausawa suke neman aure da kuma al’adun da suke tattare da neman auren.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Mine ne Aure?

2. A wa]anne shekaru Hausawa suke aurar da ‘ya’yansu maza da mata?

3. Bayyana kutsen zamani a cikin al’adun auren Hausawa da ka sani.

## Manazarta


Abdullahi I.S.S (2008). “ Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al’adun Matakan Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa.”Kundin digiri na uku: Jami’ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria. Institute of Education.ABU Press.

Bunza, A. M. (2011) Al’adun Hausawa Jiya Da Yau; Ci Gaba Ko Lalacewa? Paper Presented at Kaduna State University.

CNHN (1981). Rayuwar Hausawa. Lagos. Thomos Nilson Nigeria Limited.

Rambo, R. A (2013) Jiya ba Yau Ba: Ta}aitaccen Nazarin a Kan Bikin Haihuwa a Al'adar Hausawa. *In Detorariation of Hausa Culture Conference Proceedings.* Zaria. ABU Press Ltd.

Umar M. B. (1980) *Al'adun Haihuwa A {asar Hausa.* Zaria. Hausa Publication Centre.

## KASHI NA 4: Al'adun Haihuwa

### 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna ne game da al'adun auren Hausawa ta fukar ma'ana da nema da kuma bukukuwa da shagulgulan da ke cikin shi, a nan kuwa za a tattauna ne dagane da al'adun haihuwa a zamantakewar Hausawa.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar darasin shi ne a }arshen darasi ]alibai su sami masaniya game da wasu al'adun haihuwa da Hausawa ke gudanarwa musamman a lokutan da suka gabata.

### 3.0 Ma'anar Haihuwa

Dangane da abin ya shafi ma'anar haihuwa kuwa, a nan ana iya cewa akwai ra'ayoyi daba-daban dangane da ma'anar haihuwa . Domin wasu sun ]auki ma'anar ne ta fuskar samun da wani ya yi na wani abu. Misali a ce 'yawan dariya barkatai na haifar da hauka' A nan haihuwa na matsayin musabbabi. Amma idan muka ce 'Aisha ta haifi Musa' A nan, wannan na nuna a sanadiyyar saduwa da Aisha ta yi da mijinta ta ]auki ciki har ta haifi Musa.

Ta wannan fuska, ana iya cewa, haihuwa tana nufin samuwar ]a namiji ko mace da mutane kan yi ta hanyar saduwa tsakanin namiji da mace musammam ta hanyar aure. Ga ka]an daga cikin abin da masana suka ce dangane da ma'anar haihuwa. Abdullahi ya rawaito Alhassan da wasu suna cewa '-----ya yin da miji da mata suka }aru da samun ]a ko'ya. Abdullahi (2008:225)

A ma'anar }amussan Hausa na C N H N an bayyana ma'anar haihuwa da cewa: 'samun ]a ko 'ya bayan mace ta yi ciki wata tara' ({amusan Hausa C N H N .2006:189) Haka kuma a wani ra'ayin cewa aka yi:

> {aruwa ce ta hanyar fitowar wani abu mai rai daga
> jikin wata halitta jinsin mace wanda ya ~oyu a wani
> wuri na musammam na wani }ayyadadden lokaci don
> samun kamanni ko siffa kwatankwacin na zuriyarsu,
> wanda ke aukuwa a sakamakon saduwa da jinsin namiji
> na wani halittar. Abdullahi, (2008:228)

Bisa ga wa]annan ma'anoni, ana iya fahintar haihuwa a wannan muhalli tana nufin irin }aruwar da mace kan samu na 'ya'ya musamman bayan sun yi aure. Domin a al'adar Bahaushe ana iya samun }aruwa ta haihuwa amma maimakon a yi farin ciki sai ya zama na ba}in ciki,wannan kuwa a fili yake idan aka dubi irin }yamar da ake nuna wa matar da ta haihu ba tare da miji ba, ma'ana samun ]an da aka haifa ba tare da aure ba[2].

## 3.1 Al'adu Kafin da Bayan Haihuwa

A nan za a tattauna ne a kan wasu fitattun al'adu da Hausawa suke aiwatarwa kafin da kuma bayan an haihu. Ka]an daga cikin ire-iren wa]annan al'adu kuwa akwai;

### 3.1.1 Al'adar Goyon Ciki

A }asar Hausa, ana da al'adar mayar da yarinya haihuwa a gidansu idan cikin ya kai wata bakwai, kuma galibi wannan na faruwa ne ga mace mai haihuwar fari. Wannan al'ada ana yin ta ne domin mai ciki ta sami kulawa ta musammam a gidansu. A wannan lokacin ana

---

[2] Irin wannan haihuwar ce ake yi wa la}abi da ]an shige ko shege.

kula da lafiyarta, kuma ana sanya mata wasu sharu]]a na hani ko horo ga aikata wasu ayyuka ko cin wani abu musammam wa]anda za su taimaka mata sauka lafiya.

Haka za ta ci gaba da zama gidansu har lokacin da na}uda ta taso mata. Na}uda ita ce wata alama da mai haihuwa za ta fara ji ko gani kamar ciwon mara da baya da fitar ruwa fari a gabanta (farjinta) . Lamarin na}uda wani abu ne mai matu}ar wahala .Wannan ya sa har wa}a aka yi mata kamar haka:

Wayyo na}uda ta tashi
Ciwon na}uda ya tashi
Kuma ciwon na}uda ya motsa
Yau kam babu zama zaure
Wayyo Inna ki cece ni
Wayyo na}uda ‘yar ziza
Ciwon na}uda bori ne
Ko ko na}uda hauka ce
Ke ‘yar nanAmshi ki ]an kur~a
Ba toka ce ba rubutu ne
Ko Allah nai maki sau}in ta

Yahaya da wasu (2001:99)

Ga al’ada, da zarar mace ta je goyon ciki iyayenta za su rin}a tanadin wasu kayan goyo. A ~angaren miji ma zai tanadi nasa kayan ,wani lokaci ana kai mace ne gidansu, wani lokaci kuwa iyayenta ne ke zuwa su ]auke ta. C.N.H.N ( 1981:17)

Kamar yadda aka ambata a baya, idan na}uda ta fara ana kiran wata tsohuwa a unguwa mai ]aukar bi}i (ungozoma). Ita ungozoma tana da masaniyar dabarun kar~ar haihuwa. Bayan an sauka lafiya ungozoma za ta yanke cibiyar abin da aka haifa, ta wanke jinjiri ta kuma taimaka wurin gyaran ]akin mai haihuwa. Tana kuma taimakawa da wasu ‘yan sa}e-sa}i wadanda za a ba jariri da uwarsa domin gyaran jiki da kariya ga wasu

cututtuka. Haka  za ta ci gaba da yi wa jariri da uwar jaririn hidima har sai bayan uwar ta gama wankan jego.

### 3.1.2 Kayan {auri

A al'ada ana kai kayan }auri ne bayan an yi kwana hu]u da haihuwa . Mafi yawa ana amfani da }afafun sa ko kai ko ]an akuya ha]e da kayan yaji kamar citta da kanunfuri da masoro da barkono da kanwa da hatsi da sauransu. A kwana na biyar za a yi rabon }aurin bayan an cire wa mai jego nata, inda za a ba ma}wabta da sauran dangi da abokan arziki. A lokacin wannan rabon }aurin,  ana ha]awa da kunun kanwa duk a raba wa ma}wabta. A  al'ada, duk namijin da matarsa ta haihu ba a yi bukin shan }auri ba, to wannan ya yi abin kunya a cikin  al'umma, wannan lamari ya yi sau}i kwarai a halin yanzu.

### 3.1.3 Bukin Suna

Kamar yadda sunan ya nuna , bukin suna wani yanayi ne da ake ha]a 'yan uwa da abokan arziki a ci a sha, kuma a yi annashuwa da raha. Ana aiwatar da bukin suna ne idan ranar da aka haifi jaririn ta zagayo; ma'ana bayan mako guda. Ranar suna, rana ce da za a ra]a wa jaririn da aka haifa sunan da za a ri}a kiran sa da shi. Galibi a }asar Hausa ana sanar da 'yan 'uwa da abokan arziki  tun ana gobe za a yi sunan domin su ha]u musammman da safe  domin gudanar da wannan al'ada. Ita ma wannan al'adar ta yi rauni a halin yanzu, saboda tasirin addinin Musulunci da mafi yawan al'ummar yankin ke bi.

A ranar suna, ana yanka rago a raba goro, liman ya yi wa jariri hu]uba galibi bayan kwana bakwai da haihuwa, duk da yake ana iya hu]uba tun ranar da aka haifi jinjiri a ra]a wa yaro suna sai dai ba za a bayyana sunan ba sai ranar suna. Galibi da yake Hausawa mabiya addinin Musulunci ne, don haka, ana za~en sunan ne daga cikin sunayen addinin Musulunci.

> Ranar ra]in suna, za a taru tsakanin dangin maihaihuwa da mijinta. Idan wa]anda duk ake jira sun taho, za a raba goro ga jama'a inda za a fara fitar da na malamai da

wanzamai da mata . Daga nan sai liman ya yi wa abin haihuwar addu'a da ita kanta mahaifiyar da uban da sauran jama'a baki ]aya

Yahaya da wasu . (2001:99)

Shi kuwa (Gusau, 2012:42) Yana da ra'ayin cewa:

> Zanen suna ko ra]in suna ana gudanar da shi ga abin da aka haifa, bayan mako ]aya da haihuwa. Zanen suna ko ra]in suna ya kasu kashi biyu, akwai zanen suna a gargajiyance, akwai kuma zanen suna a addinance.

Ta kowace fuska dai za a fahinci bukin zanen suna yana haddasa ha]uwar dangin mace da na namiji wuri ]aya domin taya juna murnar samun }aruwa ta haihuwar da aka samu.

### 3.1.4 Wankan Jego

Wankan jego wanka ne da mace mai haihuwa kan yi da tafasassun ruwa har na tsawon a }alla kwana arba'in bayan ta haihu safe da marece. Daga nan sai ta ci gaba da yi da safe ko da yamma kawai zuwa kwana sittin ko ma fiye. A lokacin wannan wankan, ana yin amfani da ganyen sabara ko na doka ko na geza ko darbejiya ko sanga-sanga. Ana amfani da wa]annan ganyayyaki ne saboda muhimmancinsu wajen samar da waraka daga cututtuka daban-daban. A al'adance mace mai haihuwa tana fara wankan jego ne tun daga ranar da ta haihu. Wannan wankan yana matsayin wata hanya ta jinyar raunin da ta samu lokacin haihuwa. A wannan lokacin ne ake ba jinjiri dauri domin kula da lafiyarsa.

A al'adance idan mai jego ta yi a}alla kwana arba'in tana yin wankan, har ]an }warya-}waryan buki ake yi, inda za a toya waina a ci a yi sadaka.

### 3.1.5 Kayan Gara

A }amussan Hausa, an bayyana ma'anar gara da cewa: *Kaya, musamman na abinci da iyayen amarya kan kai wa 'yarsu bayan an gama bukin aure ko haihuwa.* CNHN (2006:157).

A zahiri ana iya fahintar ana amfani da wannan kalmar ta gara a muhalli biyu ne lokacin bukin aure da haihuwa. Ana kai garar haihuwa a ranar suna , wato kayan toye-toye wani lokaci har da ku]i . Sannan ana kai gara lokacin da mai haihuwa za ta koma ]akinta bayan ta }are wankan jego. A nan, ana ha]a mata kayan abinci irin su shinkafa da dawa da mai da daddawa da gishiri gwargwadon }arfin iyayenta. Wani lokaci har maka]i ake kira ya raka su, ana tafe ana wa}e-wa}e kamar sabuwar amarya. Sai dai wannan al'adar ta kau a halin yanzu.

### 3.1.6 Renon Abin da aka Haifa

Bayan an ra]a wa jinjiri suna da sauran hidimomin al'ada kamar wankan jego da gara, al'ada ta gaba mai muhimmanci ita ce renon shi abin da aka haifa. Reno shi ne ci gaba da kulawa da shi, ta hanyar ba shi dauri da nono sau da yawa wannan yana faruwa har tsawon wata shida. Daga nan ne za a fara ba shi kunun hatsi yana sha, duk da yake ana yi mashi ]ure ne. A lokacin da jariri ya kai wata takwas zuwa tara ne za a fara bashi abinci , sannu a hankali har ya fara ci da kansa.

Haka a wannan lokacin ne ake koya wa jinjiri zama daga nan sai rarraife da ta-ta-ta (koyon tashi tsaye) daga nan ya fara koyon tafiya . Abin lura a nan shi ne, kusantar da jinjiri yake yi da uwarsa a lokacin reno. Wannan kuwa yana taimakawa wajen samun sha}uwa da soyayya a tsakanin jinjiri da uwarsa. Duk da yake, a }asar Hausa akwai al'adar ]an reno, inda uwar jinjiri tare da amincewar mai gidanta za su samo wata 'yar yarinya domin ta taimaka wa uwar wajen renon jinjiri musamman lokacin da take aiwatar da wasu ayyuka na gida. Bayan reno, abu na gaba ga abin da aka haifa shi ne yaye. za a cire jinjiri ne daga shan nonon mahaifiyarsa. Galibi ana kai yaron ne wajen kakanninsa zuwa wani lokacin da zai manta da nono. Daga baya sai a dawo da shi wurin iyayensa**.**

## 3.2 Matsayin Haihuwa a Al’ummar Hausawa

Haihuwa ga kowace al’umma ta duniya abu ce da ake girmama ta da kuma murnar samun ta. Dangane da haka, matsayin haihuwa ga Hausawa ya fi gaban a nanata, dalili kuwa shi ne Hausawa sun shahara wajen tara mata domin samun zuri’a mai ]orewa tun gabanin su ha]u da addinin musulunci. Bayan zuwan musuluncin ma an bu}aci mutum da idan yana da hali ya auri mace ]aya zuwa hu]u.

Wannan damar da al’ada da kuma addinin musulunci ya bai wa Hausawa ne sai suka sami }arfin guiwar tara mata da za su haifa masa ‘ya’ya da yawa domin su yi noma mai tarin yawa tare da ri}a masu sauran ayyukan yau da kullum. Don haka, Bahaushe ya ]auki haihuwa da wa]annan matsayi kamar haka;

### 3.2.1 Abin Alfahari

Haihuwa a wajen Hausawa wata kafa ce da ta samar da alfahari ga wanda Allah yah ore wa ‘ya’ya. Mutane sukan yi murnar samun }aruwar haihuwa a cikin gida da kuma dangin miji da matar domin sun san abin da ‘ya’yan kan iya zama a nan gaba bayan sun girma. Irin }wazonsu da amfaninsu ga jama’a kan ta’alla}a ne ga irin tarbiyyar da suka samu a kafin girmansu. Idan sun zama abin }warai ne al’umma kan yi alfahari da su, idan kuma aka sami sa~anin hakan, al’umma za su yi Allah wadai da su a kuma }yamace su.

### 3.2.2 Tausayi ga Wanda bai Samu ba

Al’ummar Hausawa sukan tausaya wa wanda duk Allah Ya jababta da rashin samun ‘ya’ya a rayuwarsa, irin wannan tausayin ne ya sa idan a cikin zuri’a aka sami mai irin wannan matsalar ta rashin haihuwa mace ko namiji, akan ba shi ri}on ‘ya’ya domin su rage masa ra]a]in damuwa. Bisa al’ad ba kasafai mutum kan ha}ura ga lalurar rashin haihuwa ba, sai an gama da neman magani ga malamai da bokaye da ma asibitocin zamani, sai idan an yi abin ya ci tura sai a dangana.

### 3.2.3 Hanyar [ebe Takaici

Haihuwa a wajen Bahaushe aba ce da akae kallon wata hanyar ]ebe ta}aici a cikin zamantakewar Hausawa. Ganin irin yadda Bahaushe ya bai wa tara iyali muhimmanci

wajen noma da tara amfanin gona mai yawa, ya sa Hausawa suka ]auki lamairin haihuwa da tara iyali abin ]ebe ta}aici. Dalili kuwa shi ne, yawan al'ummar mutum gwargwadon yawan gonakin da zai iya nomawa ya sami amfanin gona mai tarin yawa a }arshen damina,

Nabiyu akan raga wa mutum mai zuri'a da yawa a cikin zamantakewar Hausawa, ma'ana ba a cin mutuncinsa a bainar jama'a ko a wula}anta shi ko da kuwa ya yi laifi ne, saboda darajar jama'arsa akan yi masa afuwa. Don haka ne ma ake ganin cewa haihuwa kan ]ebe wa mutum takaici a wasu lokuta.

### 3.2.4 [ebe Kewa a Cikin Gida

Wannan lamari yakan faru ne idan a gida akwai tarin iyali na 'ya'ya da jikoki, sai a ga gidan ya rayu a kowane lokaci mutane suna shiga da fice a cikin gidan. Mata da suke zaune cikin gida su ne suka fi fahimtar hakan, domin su ke zaune da yaran musamman }anana daga cikinsu. Za a ga gida ana ta hayaniya a tsawata wa wannan a yi wa waccan fa]a har baki ya yi ciwo. Lokutan kawai da suke jin sau}is hi ne idan yaran sun tafi makaranta ko sun yi barci.

### 3.2.5 Hanyar Samun Kula a Yayin Tsufa

Al'adar Hausawa ta yi na'am da kula da tsofaffi tun gabanin bayyanar musulunci a }asar Hausa. Wannan ne ya sa suke bai wa lamarin gabaci muhimmanci da tausayawa tare da girmama tsofaffi a duk cikin harhokinsu na yau da kullum. Lamarin ya ci gaba da wakana har bayan da musulunci ya shiga zukatan Hausawa inda rayuwarsu da da al'adunsu gaba ]aya suka mazzaye su da na addinin musulunci.

Ganin addinin musulunci ya }ara bai wa lamarin kula da iyaye muhimmanci ne ya sa Hausawa suka ]auki haihuwa da matsayin hanyar samun kula bayan tsufa ya kama mutum. Rashin galhun mutum a zamantakewar Hausawa shi ne a ce ba ya da ku]i ko 'ya'yan da za su kula da shi bayan tsufa ya kama shi. Idan ko mutum yana da zuri'a da yawa, to ko da ya kasance ba ya da ku]i, 'ya'yan da jikokin za su zame masa gata wajen kula da bu}atunsa na yau da kullum har mutuwa ta zo masa.

## 4.0 Kammalawa

Kamar yadda aka ganin wannan darasi ya tattauna ne dangane da al'adun haihuwa a zamantakewar Hausawa an ga irin yadda al'umma Hausawa suka bai wa haihuwa muhimmanci tare da raya tad a al'adu iri daban-daban kama tun daga shigar ciki da goyon cikin da kuma yadda ake tarbon abin da aka haifa da kuma rainonsa zuwa girma tare da gina sa a bisa tarbiyya ingantatta. Duk a cikin darasin an fito da bayyanai da suka tabbatar da irin gurbi ko matsayin haihuwa ga Hausawa.

## 5.0 Ta}aitawa

A ta}aice darasin wata kafa ce da ]alibai ko masu karatu suka ilmantu da wasu fitattun al'adun haihuwa irin na al'ummar Hausawa. An fayyace al'adun da ake yi kafin haihuwa da kuma bayan haihuwa. An kuma gano irin matsayin da haihuwa ke da shi a cikin al'adun Hausawa.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Bayyana yadda Bahaushe ya ]auki lamarin haihuwa a cikin al'adunsa.
2. Kawo nuhimman al'adun Haihuwa da Hausawa suke aiwatarwa idan sun fahimci mace ta sami juna biyu da kuma bayan ta haihu.
3. Tattauna matsayin Haihuwa ga Bahaushe a jiya da yau.

## 7.0 Manazarta


Abdullahi I.S.S (2008). " Jiya ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa."Kundin digiri na uku: Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sokoto.

Alhassan da Wasu (1987) *Zaman Hausawa.* Zaria. Institute of Education.ABU Press.

Bunza, A. M. (2011) Al'adun Hausawa Jiya Da Yau; Ci Gaba Ko Lalacewa? Paper Presented at Kaduna State University.
CNHN (1981). Rayuwar Hausawa. Lagos. Thomos Nilson Nigeria Limited.

Rambo, R. A (2013) Jiya ba Yau Ba: Ta}aitaccen Nazarin a Kan Bikin Haihuwa a Al'adar Hausawa. *In Detorariation of Hausa Culture Conference Proceedings.* Zaria. ABU Press Ltd.
Umar M. B. (1980) *Al'adun Haihuwa A {asar Hausa.* Zaria. Hausa Publication Centre.

## KASHI na 5: Tarbiyya

### 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna al'adun haihuwa a cikin al'ummar Hausawa, a nan kuwa za a duba wata ga~a mai muhimanci bayan an haihu, ga~ar kuwa ita ce wadda ake kira tarbiyya. Ma'ana darasin kacokan zai yi magana ne dangane da yadda za a yi renon abin da aka haifa har ya zamo abin alfahari a cikin al'umma.

### 2.0 Manufar Darasi

Babbar manufar wannan darasi shi ne a }arshe ]alibi ya sami masaniya dangane da ma'ana da hanyoyin gina tarbiyya a Bahaushiyar al'ada. Bayan wannan kuwa ]alibi ko ]alibai su fahimci matsayin tarbiyya wajen gina al'umma ta gari.

### 3.0 Ma'anar Tarbiyya

Tarbiyya kalma ce ta Larabci, wadda take }unshe da ma'anar koyar da hali na gari da kyautata rayuwar al'umma da shiryar da su zuwa ga halaye da ]abi'u masu kyau da nagarta. Dangane da haka, duk al'ummar da ta kasance haka, za ta zama mai}ima da }warjini da ganin mutuncin abokan zama. Kazalika za ta rin}a ba kowa ha}}insa kamar yadda ya dace. Abraham (1946:853) ya bayyana tarbiyya da ilmi ko horo zuwa ga ]abi'u nagartattu.

Ta la'akari da wannan ne ya sa masana da manazarta suka himmatu wajen fayyace ma'ana da matsayin tarbiyya wajen gina al'umma. Alal misali Yahaya da wasu (1992: 78) da Tanko (1993) da kuma Sa'id (2001) duk sun yi ittaf}in cewa tarbiyya ta }unshi renon jikin ]an Adam da ruhinsa da kyawawan abubuwa masu kamala. Tarbiyya ta ha]a da kyautata hankalin ]an Adam domin ya sami nagartattar rayuwa da yadda za ta dace da yanayin al'ummarsa, hakan kuma tana kyautata al'adun al'umma su kasance kyawawa tare da inganta su.

## 3.1 Hanyoyin Tarbiyya a Al'adar Bahaushe

A al'adar Hausawa tarbiyya kan ginu ne a bisa tafarkin magabata. Magabatan nan kuwa sun ha]a da iyaye maza da mata da shugabanni wa]anda suka ha]a da masu unguwanni da hakimmai da kuma sarakuna da sauran shugannin zartarwa na masu mudafun iko. Dangane da haka, wasu daga cikin hanyoyin samar da tarbiyya ga 'ya'yan Hausawa sun ha]a da;

### 3.1.1 Hanyar Tatsuniya

Tatsuniya ita ce makaranta ta farko wajen raya da kuma inganta tarbiyyar 'ya'yan Hausawa. Wannan hanya ce kowa ke tasowa da sanin yadda rayuwa ke gudana, dalili kuwa a cikin tsarin bayar da labaran tatsuniya akan bai wa yara labarai masu ]auke da darussa daban-daban da ake iya koya domin samun nagartacciyar rayuwa. Galibi masu bayar da tatsuniya tsofaffi ne da suka san hikimomin rayuwar Hausawa a jiya da yau. Daga cikin darussan da yara kan koya su kuma tashi da su a cikin zukatansu sun ha]a da; juriya da kawaici da kauce wa kwa]ayi da son juna da sada zumunci da tsare gaskiya da ri}on amana da sauran nagartattun ]abi'u da halaye da aka san Hausawa da su.

### 3.1.2 Hanyar Iyaye Mata

Hausawa kan ce “Uwa ma ba da Mama” wasu kuma suka ce “ Uwa ma ba ]a nono” duk dai yake karin maganar yake a nan, ana son a nuna muhimmanci uwaye mata ne wajen tabbatar da tarbiyya ‘ya’ya a }asar Hausa. Uwaye mata su ne a sahun gaba wajen tarbiyantar da ‘ya’ya tun a matakin shayarwa. Sukan nuna wa yaransu wasu alamu na rashin amincewa da wasu ]abi’u da halaye da yaransu ke son tashi da su wa]anda suka sa~a wa al’adun Hausawa. Misali idan mace tana goye da yaronta ya ro}i alawa ga wani, a nan za ta Harare sa a wasu lokuta ma har takan buga. Hikimar hakan shi ne ka da yaro ya saba da yin ro}o a cikin rayuwarsa, domin al’adar ro}o abin }yama ce cikin zamantakewar Hausawa. A wasu lokuta iyaye mata sukan harari ‘ya’yansu ko su yi masu tsawa idan sun fahimci za su yi wani abin da ba daidai ba. Misali idan yaro zai ci abinci aka gay a sanya hannun hagu, za a ce masa ya cire sa a sanya na dama. Idan ya }i fitar da hannun za a iya bugun sa. Haka abin yake ga yanayin zaman cin abinci, dole yaro ya ri}e kwanon cin abinci kuma ya bar yawon surutu, idan aka }are cin abincin kuwa yaro ake bar wa ragowar abinci daga }arshe. Wannan wata tarbiyya ce da mata suke da alhakin kula da ita a nasu mataki na cikin gida. Idan kuma za a bai wa yaro wani abu, to dole ya sanya hannu biyu wajen amsar abin nan tare da fa]in na gode. Mata sukan koya wa yara tashi da girmama na gaba ta hanyar gaishe su da amsar masu kaya idan sun ha]u da su a kan hanya tare da kaya.

### 3.1.3 Iyaye Maza

Babbar tarbiyyar da iyaye maza ke iya bayar wa wajen ‘yan’yansu shi ne tun a mataki na farko su samar masu da sunaye masu kyau ta hanyar tsarkake su daga zargi na rashin tushe, wato su yanka masu dabbar suna. Wannan yana da matu}ar muhimmanci ga Bahaushe domin tan an ne ake sanin tushen mutum mai kyau ne ko marar kyau.

Bayan wannan ha}}in Uba namiji ne ya sanya ‘ya’yansa makarantar koyo addinin musulunci da kuma na bokon zamani, domin yaran su zama na gari a nan gaba. Yin hakan zai sanya ‘ya’yan su zama abin alfahari idan sun zama abin kwarai abin koyi bayan sun girma.

Wata hanyar gina tarbiyya ga Hausawa ita ce hanyar da za a sanya yara makarantu domin su sauya tunaninsu zuwa ga zama masu amfani ga kansu da kuma al'umma gaba]aya. A tsarin bayar da ilmin addinin musulunci da boko, ana gina mutum ne ga sanin Allah da ha}o}in zamantakewar mutane. Wannan ne ya sa ake iya rarrabe wanda ya je makaranta (mai ilmi) wanda bai je makaranta ba (maras ilmi). Dalili kuwa shi ne mai ilmi ne al'umma kan amfana da shit a fuskoki da dama, yayin da maras ilmi kan zama abin }yama a cikin jama'a. Wannan ya nuna irin tarbiyyar da ya samu ba mai kyau ba ce.

**3.1.4 Hanyar Ma}wabta**

Ma}wabta shi ne kusantar da mutum yake yi da wani ta gida ko wurin zama. C.N.H.N (2006:327) A irin wannan zama na muhalli ]aya yakan haifar da zaman tare da kula juna. Asali ma a zamantakewar Hausawa ma}wabtaka kan taimaka wajen gyara da kuma inganta tarbiyyar 'ya'ya musamman a jiya, ba yanzu da zamunanci da aron al'adun ba}i ya yi cikakken tasiri a kanmu ba.

A zamantakewar Hausawa, ma}wabci kan yi iya }o}arinsa na ganin ya inganta tarbiyyar 'ya'yan ma}wabtansa ta hanyar tsawata su idan sun yi abin da bai dace ba ko ma ya hkunta su idan sun yi wani babban laifin da ya sa~a wa al'ada. Wannan matakin kuwa yakan taimaka wajen gina tarbiyyar 'ya'yan Hausawa musamman a lokutan da suka gabata.

**3.1.5 Hanyar Shugabanni**

Wani kaso na wa]anda gina tarbiyya ya ta'alla}a kuwa su ne shugabannin al'umma. Wa]annan su ne mutanen da suke da alhakin kula da rayuwar mutane da dukiyoyinsu wajen samar masu da tsaro ingantacce. Yin sakaci ga ayyukan shugabanni yakan kawo barazana ga tarbiyyar matasa a duk inda suke, rashin ginanniyar tarbiyya ga matasa kuwa sakamakonsa ta~ar~arewar tsaro da zama lafiya da kuma samun cigaba mai ]orewa. Don haka, a }asar Hausa inda aka fito sarakuna da hakimai da masu unguwanni sukan yi aiki kafa]a-kafa]a wajen ganin sun inganta tarbiyyar matasa a kowane mataki. Yin hakan kuwa ya haifar da samun zama lafiya da lumana a fa]in }asar maimakon abin da yake faruwa a yau.

### 3.1.6 Sauran Al'umma

A nan zai kyautu mu san mene ne Al'umma? Wani Masani mai suna Hornby (1948) ya bayyana al'umma da cewa " [aukacin mutanen da suke zaune a wuri ]aya kuma suke da al'adu da ]abi'u iri ]aya." A ra'ayin masana ilmin zaman Jama'a kuwa (sociologist) ganin suke al'umma a matsayin }abila mai asali da yare ]aya da ra'ayin zaman duniya (falsafa) ]aya da kamanni kusan iri ]aya da kuma al'adun gargajiya iri ]aya.

Dangane da haka za mu iya ]aukar al'umma a matsayin taron mutane ko jama'a da suke zaune cikin aminci da fahimtar juna wanda hakan kan faru ne a dalilin nasabar jini ko auratayya da kume zamantakewar garuruwa da sana'o'i.

A nan darasin yana son ya nuna cewa bayar da tarbiyya ga yara da matasa aiki ne na jama'a baki ]aya. Don haka, ake son al'umma su himmatu wajen kula da wannan al'amari mai muhimmancin gaske. Yin saku-saku da sha'anin tarbiyya ne ke haddasa ayyukan rashin kunya da imani a fa]in }asar nan. Da jama'a sun yi abin da ya dace wajen renon tarbiyyar matasanmu da abubuwan da suke faruwa a kowane sa}o da lungu na }asar nan masu kama da ayyukan ta'addanci da ba su faru ba.

## 3.2 Matsayin Tarbiyya

Sha'anin tarbiyya abu ne da yake da muhimmancin gaske a kowace nahiya da al'ada. Dangane da haka lamarin tarbiyya wajen gina kowace al'umma abu ne da ke da babban matsayi.

Tarbiyya tana da matsayi wajen samar ilmin matasan kowace al'umma, samar da ilmin nan kuwa wani mataki ne na samar da al'ummar da za ta iya ri}e kanta ta hanyar dogaro ga kai da rashin yawaitar ayyukan ta'adanci da rashin aiki ke haifarwa. Wannan ne ya sa tun gabanin Hausawa su ha]u da ba}in al'ummu (kamar Larabawa da Turawa da sauran }abilun cikin }asa) suke ri}e da sana'o'insu na gargajiya masu kore masu zaman banza da rashin aikin yi. Mutane sun ginu a bisa tafarkin koyon sana'o'i da dogaro da kai, wanda tarbiyyar Hausawa ta tanadar a cikin al'adunsu na zamantakewa.

## 4.0 Kammalawa

Abubuwan da aka tattauna a wannan darasi sun fito muna ma’anar tarbiyya da hanyoyin inganta tarbiyyar ga‘ya’yan Hausawa tare da fayyace matsayin tarbiyya a cikin al’adun Hausawa.

## 5.0 Ta}aitawa

A dun}ule darasin ya fito da irin rawar da iyaye maza da mata za su iya takawa wajen gina tarbiyyar ‘ya’yansu. An kuma tattauna wasu hanyoyin gina tarbiyyar Hausawa da suka ha]a da tatsuniya da makarantu da ma}wabta da shugabanni da kuma sauran jama’a domin ganin an gima al’umma tabbatacciya mai nagarta.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Mene ne Tarbiyya?
2. Kawo hanyoyin da za su taimaka wajen gina tarbiyya a zamantakewar Hausawa.
3. Wane matsayi tarbiyya ke da shi wajen samar da zaman lafiyar al’umma?

## 7.0 Manazarta


Abdullahi, S. U . (1985) *Gasikiya Dokin {arfe*. Kano. Mainasar Printing Press.

Abraham R.C (1946) *The Dictionar of hausa Language.* London, Hodder and Stoughton.

Awobuluyi, O. (1976): *The New National policy on Education in Linguistic Perspective*. University of Ilorin Press.

Fafunwa, B (1989): *Education in Mother Tongue.* The Primary Education Research Project. Ibadan University Press Ltd.

CNHN (1981). Rayuwar Hausawa. Lagos. Thomos Nilson Nigeria Limited.

Gusau, S.M (2010): “Ilmi Garkuwar Al’umma”. Takardar da aka gabatar a taron }addamar da Gidauniyar Bun}asa Ilmi a Kaura Namoda, Jihar Zamfara.

Sa’id B. (2001) *Tarbiyya a Musulunci: Ha}}in ‘Ya’ya a kan iyaye da Ha}}in Iyaye a kan ‘Ya’ya.* Kano. Abba Press Nigeria Ltd.

Sam, O E, (2009) *Roadmap for the Nigerian Education Sector.* Published by Federal Ministry of Education Abuja.

Tanko, Y. (1993) *Tarbiyyar Yara a Musulunci.* Kano. Manafold Publishing Company Ltd.

UNESCO (1953) The Use of Vernacular Languages in Education. Report of the UNESCO Meeting of Experts, 1951, Paris, UNESCO.

Yahaya da Wasu (1992) *Darussan Hausa Don Manyan Makarantun Sakandare na 3* . Ibadan. University Press Plc.

## KASHI NA 6: Zumuncin Hausawa

### 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an yi bayani ne dangane da tarbiyya a zamanantakewar Hausawa, a nan kuma za a yi duba ne game da wata al’adar zamantakewa mai muhimmancin gaske, wato zumuncin Hausawa.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi a cikin wannan tattaunawar shi ne domin a fayyace wa ]alibai al’adun zumuncin Hausawa da rabe-rabensa da kuma matsayin da mamaye a cikin al’adun zamantakewa.

### 3.0 Ma’anar Zumunci

Bisa asalin kalmar ana ganin ta samu ne daga abin nan da Bahaushe ke kira “ Zo mu ci” wato zo mu ci tuwo ko wani nau’in abinci. Sannu a hankali sai kalmomin suka riki]e suka

zama guda wato “Zumunci”. A fahimtar Bahaushe, zumu ko masoyi ka]ai ake gayyata ga cin abinci.

A cikin }amusun Hausa (2006:479) an nuna cewa “*Kalma ce da ke nuna irin kyakkyawar dangantaka ta jini ko ta aure ko kuma ta abota ko mu’amula a tsakanin mutum da mutum.* A zamantakewar Hausawa zumunci yana taka muhimmiyar rawa wajen nuna son juna da kara a tsakaninsu da ‘yanuwan zamansu a kowane irin yanayi, wannan ne ma ya sa idan aka yi mutuwa akan yi zaman makoki, inda za a tarar da cewa wuri ne da ‘yan uwa na jini da abokan arziki ke ha]uwa domin jajantawa junansu irin rashin da aka yi, wanda a sakamakon hakan ya zama wani muhalli na bun}asa zumuncin Bahaushe. Idan kuma wani abin murna ya samu, hakan za a ga sun taru suna taya juna murna. Hakan ya haifar da bu}atar tattaunawa game da rabe-raben zumnucin Hausawa kamar haka;

## 3.1 Rabe-raben Zumunci

Al’adar Bahaushe abu ce da ta }arfafa Zumunta da neman sadar da ita a koda yaushe. A kowane irin yanayi ana son mutum ya zama mai ziyartar ‘yan’uwansa, ya kasance mai taimako da kyautata musu gwargwadon hali. Hausawa na cewa “ Zumunta a }afa take”wato zuwa wajen zumu domin sada zumunci ko gaisuwa ko aika sa}o. Don haka, zumunci ga Hausawa abu ne mai matu}ar muhimmanci wannan ne ya sa suke ba shi }arfi tun gabanin su }arbi addinin musulunci. Bayan da suka amshi musulunci kuwa, sai suka ga cewa addinin musulunci ya yi kira ga a rin}a aiwatar da zumunci, shi ken an suka ci gaba da }arfafa shi. Wannan ya haifar da samuwar rabe-raben zumuncin Hausawa zuwa rukuni-rukuni kamar haka;

### 3.1.1 Zumunci Auratayya

Wannan zumunci ne da ake samu a kowace al’umma ba Hausawa ka]ai ba. Ana gina wannan zumunci ne a dalilin aure, ko dai ya kasance mutum ya auro daga wani gida ko zuri’a ko kuma wani ya zo ya aura daga gare shi. Ana kiran wannan zumunci da suna “ Zumunci jini”.

Idan hakan ya faru, daga wannan lokaci da aka yi aure, an zama ‘yan’uwan juna na har abada musamman idan aka sami haihuwa a tsakanin ma’auratan. Sakamakon irin wannan zumuncin ne akan sami;

i. Surukai

ii. Kakannin mata ko miji

iii. Yannan mata ko miji

iv. {annan mata ko miji

v. ‘Ya’ya

vi. Jikoki

**3.1.2 Zumunci Unguwa**

Zumuncin unguwa ana samun sa ne idan mutane suka fito a unguwa ]aya. Ma’ana ya kasance suna ma}wabtaka da juna a muhallansu ko gidajensu. Wannan zumunci an fi aiwatar da shi idan aka fita wajen unguwa, musamman idan mutum ya ga za a ci ma wani ]an unguwarsu mutunci, zai tsaya ya ga cewa ba a ci masa mutunci ba saboda sun fito a unguwa ]aya. A tsarin wannan zumunci ba dole ya kasance akwai zumuntar jini a tsakaninsu ba.

**3.1.3 Zumunci Gari**

Wannan zumunci ne da ake samu inda mutane za su zamo ‘yan gari ]aya. Babu Bahaushen da zai so garinsu ya zama baya, kowane so yake a ce garinsu yana gaba musamman a lamurrran da suka shafi ci gaban }asa da bun}asarta. Irin wannan kishin na ci gaba shi ke haifar da }arfafar wannan zumunci. Mutanen duk da suka fito gari ]aya sukan taimaki junansu idan bu}atar hakan ta taso, irin wannan bu}atar ke haifar da ayyukan gayya na gyara hanya da ma}abarta da gajiyyayi da sauransu.

**3.1.4 Zumuncin Sana’a**

Wannan nau’in zumunci ne  da ya shafi sana’o’in al’umma. Idan mutane suna aiwatar da sana’a iri ]aya za su ]auki kansu tamkar ‘yanuwan juna. Wannan matsayin da suka ]auka

a tsakaninsu, shi ke sanya duk wani abu ya faru na murna ko ba}in ciki, za a ga cewa sun halarta domin nuna murnarsu ko akasin hakan. A cikin zamantakewar Hausawa akwai nagartattun sana'o'insu da suka tashi cikinsu ana aiwatarwa tun kaka da kakanni. Irin wa]annan sana'o'in ne suka haifar da samuwar wasu unguwanni a biranen }asar Hausa. Misali akwai unguwanni irin su ma]inka da majeme da marina da masa}a wa]anda ake samun mutane masu aiwatar da sana'a iri ]aya sun kafa unguwa 'ya'ya da jikoki. A wannan zumuntar sukan taimaki juna idan an sami bukin aure ko suna da sauransu. A dalilin }arfin irin wannnan zumnucin ne ya haifar da samuwar wasannin barkwancin sana'o'i kamar yadda za a tattauna su a nan gaba.

### 3.1.5 Zumuncin Addini

Zumuncin addini wani nau'in zumunci ne da ake samu a cikin al'ummar Hausawa. Akan gudanar da shi ne a cikin sha'anin da ya shafi ayyukan ya]a addini ko kuma a ce }ungiyanci da a}idanci a cikin ayyukan addini. Yadda ake gane irin wannan zumuncin sai an dubi yadda kawunan Hausawa suka rarraba ga sha'anin a}ida inda ake samun 'yan izala da 'yan ]arika da dangoginsu. Wannan kason da aka }ir}iro a cikin zamantakewar Hausawa yakan haifar da zumunci a tsakanin magoya bayan a}idun su rin}a ]aukar junansu a matsayin ma}iya musamman wa]anda a}idunsu suka sa~a wa juna. Sai dai duk da hakan, sukan ]auki duk wani ]an }ungiyarsu a matsayin ]an'uwa kuma masoyi. Don haka, za su ci gaba da mutunta juna da taimaka masu idan bu}atar hakan ta taso.

## 3.2 Dalilan Zumunci

Hausawa kamar sauran al'ummun da ke a doron }asa suna da dalilan da suka haddasa masu yin zumunci har aka sami rabe-rabensa da aka tattauna a sama. Ka]an daga cikin dalilan zumuncin Bahaushe sun ha]a da;

i. Dangantakar jini ta fuskar auratayya.

ii. Dangantakar muhalli na unguwa ko gari.

iii. Dangantakar sana'o'i.

iv. Dangantakar ayyukan }ungiyoyin addini.

## 3.4 Matsayin Zumunci

Matsayin zumunci ga Hausawa ya fi gaban a maimaita, dalili kuwa shi ne ginshi}in samar da ci gaba da fahimtar juna. Hausawa suna ]aukar zumunci a matsayin wata kafa ta }arfafa dankon zaman tare da fahimtar juna da tausayin juna da kuma kishin ci gaban juna. Don haka, da ba domin Hausawa sun ]auki zumunci da muhimmanci ba da yanzu rarrabuwar kawunan Hausawa ta kai inda ta kai, domin ai }o}arinsu na kyautata zumuncin ne ya haifar da samar da wasannin barkwanci a tsakaninsu da wasu }abilun da aka yi zama na rashin jittuwa ko ya}i. Sarkin Gulbi (2016:8).

## 4.0 Kammalawa

A cikin wannan darasi an tattauna game da zumunci Hausawa ta la'akari da yadda ake samar da shi da rabe-rabensa da kuma yadda zumuncin kan taimaka wajen samar da zaman lafiya da fahimtar juna a cikin al'umma. Darasin ya fito da dalilan zumunci tare irin matsayinsa a cikin zamantakewar Hausawa.

## 5.0 Ta}aitawa

A ta}aice dai darasin yana }unshe da muhimman batutuwan da suka shafi ma'anar zumunci da rabe-rabensa da dalilan aiwatar da shi da kuma gurbin zumunci a cikin al'adun zamantakewar Hausawa.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Mene ne Zumunci?
2. Kawo rabe-raben zumuncin Hausawa kamar yadda al'ada ta tanada.
3. Wane matsayi ne ke ga zumunci a zamantakewar Hausawa?

## 7.0 Manazarta


CNHN (2006). *{amusun Hausa*. Zaria ABU Press.

CNHN (1981). Rayuwar Hausawa. Lagos. Thomos Nilson Nigeria Limited.

Sarkin Gulbi, A. (2015). “Traditional Title Holders: The Ambassadors of Peace in Mara]i Region.” Paper presented at the international Symposiun tagged Mara]i kwalliya 2015, at [andikko [ankulodo University, Mara]i. 13-16 Dec, 2015.

Sarkin Gulbi, A (2016). “Sulhu A Gargajiyance: Darasi Daga Daular Sakkwato Da Kabi”. Takardar da aka gabatar  a taron }ara wa juna sani na }asa da Tsangayar Fasaha da Nazarin Addinin Musulunci ta Jami’ar Usmanu Danfodiyo ta shirya daga ranakun 1-3 ga Watan Maris, 2016.

Umar, M.M. (2014) Zumuntar Bahaushe a Zamanin GSM. *in Garkuwan Adabin Hausa. A festschrift in Tribute to Abdul}adir [angambo.* Zaria. ABU Press.

# FASALI NA 2: SULHU A ZAMANTAKEWAR HAUSAWA

## KASHI NA 1: Sulhu da Sasantawa a Zamantakewar Hausawa

### 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna dangane da zumuncin Hausawa da rabe-rabensa da kuma matsayinsa, a nan kuma za a dubi wata al’adar zamantakewa mai muhimmanci wato al’adun sulhu a zamantakewar Hausawa.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar darasin shi ne domin a }arshen darasin ]alibi ya sami masaniya game da dabarun sulhu da sasantawar gargajiya irin na Hausawa wajen kawo zaman lafiya da lumana.

### 3.0 Ma’anar Sulhu

Wannan kalma ta sulhu Balarabiya ce da ta shigo cikin harshen Hausa mai nufin samar da daidaito a tsakanin masu jayayya da juna a kan wata matsalar rayuwa. Kalmar sulhu kan yi shige da fice a cikin magangannun Hausawa na yau da kullum ba sai a fagen warware rikicin fa]a ba, a’a ana amfani da kalmar domin a  sasanta masu cikini a kasuwa. Misali akan ce “Na sulhunta cinikin.” Ma’ana, an sasanta masu sayen wani abu.

Dangane da haka, sulhu ya sami fassara daga bakin masana da manazarta kamar yadda za a gani a cikin wannan bayani;

> *Sulhu wata hanya ce ta tattaunawa domin warware wata matsala a tsakanin mutum da mutum. Misali akan sasanta a tsakanin mata da miji idan wata matsala ta faru, ko a tsakanin aboki da aboki ko maigida da yaronsa ko ma}wabci da ma}wabci ko kuma al'umma da al'umma.*[3]

*Jeong (2000: 127) ya* ce: "*Sulhu wata hanya ce ta cimma matsaya a tsakanin al'ummu biyu da suke jayayya da juna*."

A cikin www.Wekipedia 2008 kuwa, an bayyana sulhu da cewa: *"Wata hanya ce ta tattaunawa da ake yi da nufin magance fitina tare da samar da wata yarjejeniyar zaman lafiya da fahimtar juna."*

Idan aka yi la'akari da bayanan da suka gabata za a ga cewa, sulhu ya }unshi duk wata hanyar tattaunawa da za a yi amfani da ita domin shawo kan wata matsalar ya}i ko tarzoma ko bijerewa ko tawaye a tsakanin masu jayayya da nufin samar da zaman lafiya mai ]orewa.

## 3.1 Sulhun Gargajiya

Wannan dabaru ne da al'ummar Hausawa ke amfani da su wajen magance rikici da fitina a cikin al'umma tun gabanin su sha}u da wasu ba}in al'ummu. Irin wannan sulhu Bahaushe ya gade shi ne tun kaka da kakanni bai samo tasiri daga wasu al'ummu ba. Dama akwai irin wannan al'ada a cikin ]abi'un Bahaushe na zamantakewa, kafin Musulunci ya zo ya }arfafa shi.

## 3.2 Rabe-raben Sulhu

Masana ilimin zaman lafiya da sasantawa sun kasa sulhu gida biyu (2) Sulhun ruwan sanyi da lumana da kuma Sulhun fafatawa.[4] Inda suka tafi a kan cewa shi sulhun ruwan sanyi, sulhu ne da ake yi a farkon rikici kafin shiga ya}i a tsakanin ~angarora guda biyu. Masu shiga tsakani kan shiga su warware matsalar ba tare da ~ata lokaci ba. Yayin da sulhun Fafatawa yake nufin irin sulhun nan ne da ake yi bayan ~arna da zubar da jini

---

[3] Jonah, Onuaha; Nigotiation and Mediation Process: in Peace Studies and Conflicts Management in Nigeria. UNN, 2009, page 110.

[4] Jonah, Onuaha; Violent and Non Violent Methods of Negotiation. Nigotiation and Mediation Process: in Peace Studies and Conflicts Management in Nigeria. UNN, 2009, page 130.

(ya}i). A irin wannan sulhun wa]anda aka rinjaya za su nemi aje makamai domin a sasanta. Dangane da haka wannan nazari ya kalli sulhun gargajiya zuwa gida biyu muhimmai kamar haka;

### 3.2 .1 Sulhun Cikin Gida

Wannan nau'i ne na sulhun gargajiya ana yin sa ne a tsakanin mutane da ke zaune a muhalli ]aya, suke kuma gudanar da rayuwarsu tare da al'adunsu iri ]aya. Bisa ga al'adar Bahaushe, idan aka sami wani rashin jituwa ya faru a tsakanin mutum da mutum akan sanya magabaci (maigida) domin ya shigo ciki ya sasanta lamarin. Idan ya fi }arfinsa ne yakan kai ga mai unguwa ko Hakimi domin ya sulhunta lamarin. Shi kuwa mai unguwa ko Hakimi yakan kai matsalar a gaba idan ta }i ci ta }i cinyewa.

Daga cikin matsalolin da ke bu}atar sulhun cikin gida akwai sulhun;

- Zamantakewa a cikin gida;

i. Mata da Miji.
ii. Kishiya da kishiya.
iii. [a da Mahaifinsa ko Mahaifiyarsa.
iv. Wa da {anensa.
v. Matan wa da }ani.
vi. Matan ]iya da mahaifan maigida.

- Zamantakewar Yau da Kullum;

i. Maigida da Yaronsa.
ii. Ma}wabci da Ma}wabci (ma}wabcin gida ko gona ko rumfar kasuwa).
iii. Hakimi da Talakawansa.
iv. Limami da Mabiyansa.
v. Masu sana'a iri ]aya (masunta, da manoma da mahauta da ma'aska da magina d.s).

### 3.2.2 Sulhun Waje

Wannan nau'i ne na sulhu wanda ake yi a tsakanin al'umma da wata al'umma da suke da mabambantan ra'ayoyi ko a}ida ko sana'a. Irin wannan sulhu an fi samun sa bayan an fafata da gwada }arfin tuwo da na iko. Daga cikin ire-iren wannan sulhu kuwa sun ha]a da;

i. Sulhun }abila da }abila.
ii. Sulhun daula da daula.
iii. Sulhun }asa da }asa.
iv. Sulhun Manoma da Makiyaya.

## 3.3 Rikice-Rikicen da ke Haddasa Sulhu

Akwai abubuwa da dama da ke haifar da rikice-rikice a cikin al'umma wa]anda ke bu}atar zaman sulhu kamar haka;

i. Ya}i.
ii. Rikicin Aure.
iii. Rikicin addini.
iv. Cinikin gona da gida da filaye.
v. |arnar Fulani a gona.

## 3.4 Dalilan Sulhu

Al'umma kan bu}aci sulhu ne idan ]ayan wa]annan dalilan suka faru kamar haka;

i. Idan wani sashe na al'umma ya cuci wani.
ii. Idan ana tsoron kai wa ga abin kunya.
iii. Idan ana tsoron a ce kuna kallo aka yi ~arna.
iv. Idan ana tsoron ka da rikici ya kawo a gareka/ku.
v. Idan ana tsoron ka da a zalunci mai gaskiya ko marar }arfi.
vi. Idan ana tsoron zumunci ya lalace.
vii. Idan ana tsoron ~arnata dukiya da rayuwa.
viii. Don kaucewa wata ~oyayyar manufa, misali tattalin arziki daga mai yin sulhun.

## 3.5 Sigogin Sulhu

Sulhu yana da sigogin da ke tabbatar da samuwarsa a cikin al'umma. Wa]annan sigogin kuwa sun ha]a da;

i. Sulhu na bu}atar masu shiga tsakani domin warware matsalar.

ii. Sulhu na bu}atar samar da wata manufa ta musamman.

iii. Dole a bayyana tare da tattauna manufar a tsakanin ~angarorin da ke rikici ko jayayya.

iv. Bayan tattaunawar, akwai bu}atar samar da wata yarjejeniyar zaman lafiya.

v. Sulhu na bu}atar mutunta yarjejeniyar tare da kare ta a kowane irin yanayi ba tare da karya ta ba, ko da kuwa ]ayan ~angaren zai cutu da sakamakon.

vi. Masu sulhuntawa su kasance 'yan ba ruwanmu a zahiri.

## 3.6 Muhimmancin Sulhu a Zamantakewarmu ta Yau

A nan darasin zai dubi matakan sulhu da zaman lafiya da Bahaushe yake da su a jiya tare da kallon yadda za su taimaka wajen magance rikice-rikicen da }asar nan take ciki a yau. Daga cikin darussan da za a koya a matakan tsaro da kariyar Bahaushe a yau sun ha]a;

i. Tattaunawa tsakanin gwamnati da tsagerun Nija Delta da }ungiyar Boko Haram da kuma 'yan ta'adda wa]anda ke garkuwa da mutane da kawo barazana ga zaman lafiya da tattalin arzikinmu. Wannan matakin jihar Zamfara ta fara ganin amfaninsa, jihar katsina ma ta fara irin wannan yun}urin na sasantawa da Fulani.

ii. Samar da yarjejeniyar zaman lafiya mai ]orewa kamar yadda ya faru a tsakanin daular Sakkwato da ta Kabi, kuma yake faruwa a yanzu da wasu Fulani 'yan tada zaune tsaye.

iii. Ya}ar cin hanci da rashawa tare da ]ebe kwa]ayin abin duniya da mutane suka sanya a gaba a yau.

iv. Sanya ci gaban }asa da bun}asar tattalin arzikinta bisa ga abin da mutum zai samu na ganimar siyasa, kamar yadda masu jihadi suka ya}i sauran daulolin }asar Hausa da nufin fa]a]a daular da a}idojinta.

v. Sadaukar da rayuwa wajen sasantawa da tabbatar da samun zaman lafiya mai ]orewa, kamar yadda aka sami yarjejeniyar zaman lafiya a tsakanin daular Sakkwato da Kabi musamman a zamanin Sarkin Musulmi Ahmadu [an Rufa'i.

## 4.0 Kammalawa

A wannan darasi an nazarci dabarun sulhu wajen rage ra]a]in gaba da }iyayya a cikin al'umma musamman a zamantakewar Hausawa, da kuma irin darussan da za a iya koyo daga wannan sulhun. Darasin ya tafi a kan bayyana ma'ana da rabe-raben sulhu da sigoginsa da dalilan da ke haifar da yin sulhu da matakan da ake bi wajen samar da sulhu.

## 5.0 Ta}aitawa

Wannan darasi kamar yadda aka gani ya dubi lamarin sulhu ne a gargajiyance tare da gano irin matakan da Hausawa suka bi wajen samar da zaman lafiya a tsakaninsu. Dangane da haka, darasin ya nuna cewa duk yadda al'amurra suka rinca~e, idan aka koma kan teburin shawara ana iya shawo kan matsalar. A cikin darasin duk an tattauna matakan sulhun gargajiya da wa]annan al'ummu suka yi amfani da su domin ]inki ~arakar da ke a tsakaninsu. Amfani da irin wa]annan darussa ne mafita ga matsalolin da }asar nan take ciki na rashin tabbas ga tsaro musamman a zamantakewarmu ta yau.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Me ake nufi da sulhu a gargajiyance?
2. Kawo rabe-raben sulhu da ka sani
3. Wa]anne dalilai ne ke haifar da bu}atar sulhu?
4. Bayyana sigogin sulhu a zamantakewar Hausawa

## 7.0 Manazarta

Alkali, M.B. (1969) A Hausa Community in Crisis: Kebbi in the Nineteenth Century." M.A. Dissertation, A. B. U. Zaria.

Gummi, M.F 2015: "Sarkanci a Lardin Sakkwato." Kundin Neman Digiri Na Uku. Jami'ar Usmanu [anfodiyo Sakkwato.

Gusau, S.M. 2015: *Fulanin Zamfara-Katsinar Laka Da Tasirinsu a Daular Sakkwato.* Century Research and Publishing Ltd. Kano.

Harris, P.G. (1938) "Sokoto Provincial Gazetteer."

Jonah, 2009; Nigotiation and Mediation Process: in *Peace Studies and Conflicts Management in Nigeria*. University of Nigeria Nssuka,

Last, M. 2009: *Daular Sakkwato.* Ibrash Islamic Publication Centre. Lagos.

Mc, A. 1909: *The Rise of Sokoto Fulani*.

Onigu, O. 1999: *Community Conflicts in Nigeria.* Spectrum Books Ltd. Ibadan.

Sarkin Gulbi, A. 2015: "Traditional Title Holders: The Ambassadors of Peace in Mara]i Region." Paper presented at the international Symposiun tagged Mara]i kwalliya 2015,at [andikko [ankulodo University, Mara]i. 13-16 Dec, 2015.

www.Wekipedia 2008.net

## KASHI NA 2: Taubasantaka

### 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna ne dangane da sulhu a zamantakewar Hausawa, yanzu kuma za a yi duba ne a kan zumuntar taubasantaka a cikin zamantakewar Hausawa. Ta la'akari da ma'anarta da yanaye-yanayenta.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi shi ne daga }arshen tattaunawar darasin ]alibi ya sami haske game da wannan al'adar zamantakewa ta taubasantaka a cikin zamantakewar Hausawa.

### 3.0 Ma'anar Taubasantaka

Akwai wuraren da aka ba da ma'anar kalmar taubashi da cewa, kalma ce mai nuna sunan namiji. Ita kuma mace, ana kiran ta taubashiya. Idan kuma aka ha]a su wuri ]aya, sunansu taubassai ko taubasai. Taubashi na nufin ]an mace da ]an namiji, watau ]an wa da ]an }auna, ko ]an ya da ]an }ane.[5]

A cikin }amus na Bargery an ce,

> Taubashi na nufin 1. *Cousins, but only children of a brother and sister, not of two brother or sister. Those so 'related' are called* abokan wasa, *and one who abuse or steal from the other and no offence be taken. On the 10th day of Muharram, a desendant from the sister can demand gifts from a decendant of the brother. (Vide* shara *iv;* abokin wasa)[6].

A cikin {amus na sama cewa aka yi, taubasantaka na nufin "*The state of being a* taubashi.[7] A wani wuri kuma cewa aka yi, taubasantaka na nufin dangantakar ]an mace da ]an namiji.[8]

## 3.1 Dalilan Taubasantaka

Dalilan taubasantaka suna da yawa, ka]an daga cikin su sun ha]a da;

i. Asalin zuri'a wadda kan samu a dalilin auratayya.

ii. Dalilin ya}i a tsakanin }abilu.

iii. Dalilin dangantakar sana'o'i

## 3.2 Rabe-raben Taubasantaka

---

[5] A dubi Kamusun Jami'ar Bayero, Kano wallafar Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, 2006, shafi na 423.

[6] A dubi Kamusun Bargery, shafi na 1008.

[7] Daidai da lamba ta 2.

Taubasantaka ta kasu rukuni-rukuni dangane da abin da ya haifar da ita. Wata a dalilin ha]a zuri'a ce wata kuma a dalilin saana'a ko ya}i da sauransu. Danagane da haka, wannan darasi ya dubi rabe-raben taubasantaka a zamantakewar Hausawa kamar haka;

### 3.2.1 Taubassan Bahaushe na Jini

Ana samun dangantar jini tsakanin mutanen da suka ha]a kakanni da iyaye iri ]aya. Akwai taubassan Bahaushe a sashen uwa da sashen uba, wato mahaifiya da mahaifi. A ~angaren uwa Bahaushe da taubassansa gefen yannenta maza da kuma }annenta maza, amma babu taubassaka tsakanin ]iyan ya da na }anwa (mata zalla). Haka kuma akan sami taubashi ta ~angaren mahaifi. A nan, dukkan ]iyan yanne da }annen mahaifin mutum mata ka]ai, su ne taubassansa da suka ha]a dangantakar jini. Ga bayanin taubassan Bahaushe ta sashen mahaifiya.

### 3.2.2 Taubassan Bahaushe na |angaren Uwa

Idan mace na da yanne maza da }anne maza da suka ha]a uwa ]aya uba ]aya, ko kuma wa]anda suka ha]a uba ]aya a matsayin dangantakar jini, kuma ita }anwar ko yar na da 'ya'ya maza da mata ko maza zalla ko mata zalla, duk dai yadda hali ya samar, su kuma yannenta da }annenta maza suna da ]iya kamar yadda take da su, to, ]iyansu sun zama taubassan juna. Sai dai kuma, ]iyan mace ke kar~ar dukiyar shara ga ]iyan yanne da }annenta baki ]aya. Haka kuma 'ya'yan }anne da yanne mace su ne masu gidan 'ya'yan }anwa ko ya mace. Wannan ne ya sa ake jin kalmar maigida da yaro tsakanin taubassan Bahaushe.

Bayan haka idan aka sami uba na da mata fiye da ]aya na aure a }ar}ashin kulawarsa, aka sami akwai 'ya mace a ]ayan ]aki kuma ya kasance sauran ]akunan uban akwai ]iya maza, su ma ]iyan (maza da mata) taubassan ]iyan matar da ta ha]a uba da ]iyan sauran ]akunan can ne. Haka kuma ]iyan wa]ancan yanne ko }annen wa]ancan ]akuna su ne masu gidajen ]iyan macen da suka ha]a uba.

### 3.2.3 Taubassan Bahaushe na |angaren Uba

Idan aka sami mahaifin mutum na da yanne da }anne mata da suka ha]a uwa ]aya kuma uba ]aya, ita ma dangantaka jini ce. [iyan yannen da }annen, mata da maza su ne taubassan ]iyan uba namiji. Idan akwai ]iyan wani ]aki na yanne ko }annen uba mata kawai, to ]iyan matan ma taubassan ]iyan uba namiji ne. [iyan mata ke kar~ar dukiyar shara ga ]iyan maza. [iyan namiji ne masu gidajen ]iyan mata, yanne da }anne baki ]aya.

### 3.2.4 Kaka da Jika

Hausawa na cewa, "Jika wanda ya fi ]an ciki da]i". Ba shakka biri ya yi kama da mutum. Za a fahimci haka idan aka yi la'akari da soyayyar da kakanni ke nuna wa jikokinsu na ~angaren 'ya'yansu maza da mata. Kakanni kan nuna matu}ar ~acin ransu idan mahaifansu sun doke su, ko kuma tsananta fa]a gare su ko da laifi suka yi. A wasu lokuta ma, kaka kan ce wa mahaifan jikansa "ban yafe maka ba idan ka doke shi", ko "Allah ya la'ani wanda bai doke shi ba". Wa]annan matakai ne na hana wa iyaye dukar 'ya'ya a gaban kakanninsa. Idan suka furta haka, jika ya ku~uta daga duk abin da mahaifa ke da niyyar yi masa. Soyayyar da ke tsakanin jika da kaka ba }arama ba ce, shi ya sa kaka mace ke ce wa jikanta, "mijina". Shi kuma kaka namiji ya ce wa jikanyarsa mace "matata" saboda wasan jika da kaka da ke tsakaninsu. Za a gaskata haka ga kakanni Hausawa, musamman wa]anda suka yi lokaci da kakanninsu da wa]anda kakanni suka yi renon su ko suka yaye su, matu}ar dai jika ya tashi ya tarar da kakanninsa. Wani lokaci kakanni na wasa da mai sunan jikokinsu da takwarorin jikokinsu, kamar yadda su ma jikoki ke jan masu sunan kakanninsu da wasa. Ga al'ada duk mai sunan taubashinka abokin wasanka ne.

### 3.2.5 Taubassan Bahaushe ta Fuskar Al'ada.

Al'ada a samar wa Bahaushe abokan wasa da ba na jini ba saboda wa]ansu abubuwan da suka gudana ko ke gudana na yau da kullum. Taubassan da al'ada ta samar wa Bahaushe sun ha]a da:

i.Taubasantakar Bahaushe ta fuskar aure.

ii. Taubassaka tsakanin Hausawa zallarsu.

iii. Taubassaka tsakanin Hausawa da wasu }abilu.

iv. Taubassaka tsakanin masu sana'a.

## 4.0 Kammalawa

A cikin wannan darasi an ga yadda taubasantakar Hausawa kan samu a tsakaninsu da juna da kuma wasu }abilun da suke ma}wabtaka da su. An ga yadda suke samar da wasanni a tsakaninsu tare da }ir}irar labarai domin su fito da wani tarihi a cikin zamantakewarsu.

## 5.0 Ta}aitawa

A dun}ule darasin ya fito mana da yadda Hausawa sukan bun}asa zumuntarsu a haujin taubasantaka, yin hakan kan fito da asalinsu da wararen zamansu da kuma sana'o'insu a fili.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Mene ne taubasantaka?
2. Kawo rabe-raben taubasantaka a zamantakewar Hausawa.
3. Wa]anne dalilai kan haifar da taubasantaka?

## 7.0 Manazarta


Abdul}adir M.S. (1981) "Ha]eja's External Relations 1863-1960 From the death of Buhari to the coming of the British'. Kundin Digiri na Biyu. Kano. Department of History, Bayero University.

Adamu M. 1975 The Hausa Factor in West African History, NNPC Zaria.

Alhassan, H da Wasu (1980) Zaman Hausawa Zaria, Longman Plc.

Augi, A.R. (1984) The Gobir Factor in the Social and Political History of the Rima Basin. Kundin Digiri na Uku, Zaria, NNPC.

Auta, L. A. (1983) Jima Sana'ar Sarrafa Fata da Muhimmancinta a {asar Kano. Kundin Digiri na Farko, Kano. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Aminu S. (1986) Sana'ar Su a {asar Hausa. Kundin Digirin Farko, Kano. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Azare B.U. (1981) British Rule in Katagun Emirate 1903-1960. Kundin Digiri na Biyu, Kano.Department of History, bayero University.

Bagudu M.I. (1974) *History of the Land of Zazzau,* Zaria. Gaskiya Corporation.

Bargery, G. P. (1993) *A Hausa English Dictionary adn English-Hausa Vocabulary with* Skinner , A. N. *Some Notes on the Hausa People and their Language. D. Westermann and Suppliment*. Zaria:Ahmadu Bello University Press,.

Bunza, D.B ( 2015) Taubassan Bahaushe: Wani Mashigi na Tantance Asalinsa da Zuriyarsa. Takardar da aka gabatar a taron }ara wa juna sani na }asa da }asa a Jami'ar Jihar Kaduna daga ranar 22th -25th March, 2015, a ]akin taro na cikin Jami'ar.

## KASHI NA 3: Ma}wabtaka

## 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna ne dangane da taubasantaka da al'adun da ke tattare da ita na wasanni wajen bun}asa zumuncin Hausawa, a nan kuwa za a duba wata al'adar zamantakewa da ake kira ma}wabtaka.

## 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi shi ne domin a }arshen darasin ]alibai su iya sanin yadda zamantakewar Hausawa take game da al'adar ma}wabta da dangoginta da dalilanta da kuma matsayinta.

## 3.0 Mene ne Ma}wabtaka?

Wannan kalma ce da take nuna rayuwar zaman tarena mutane a dalilin muhallin gida ko gona ko wata masana'anta. Ma}wabci namiji tilo, ma}wabciya tamace tilo, yayin da ma}wabta ke nuni da jam'i Bargery (1934:760). Ma}wabtaka kuwa tana bayyana rayuwar zamantakewar al'umma ne da zumuncin kusanci gida ko wurin aiki ko masana'anta ta ha]u su har suka ]auki kansu a matsayin 'yanuwan juna.

A rayuwa irin ta ma}wabtaka a zamantakewar Hausawa, zama ne mai ban sha'awa inda kowa ya ]auki ]an uwansa a matsayin abu ]aya kuma ake mutunta juna wajen kula da lamurransu na yau da kullum. A zamantakewar Hausawa musammman a lokutan da suka gabata, ma}wabci kan iya hukunta 'ya'yan ma}wabtansa idan sun yi ba daidai ba. Ma}wabta sukan ci abinci tare a kofar gidansu, sukan sanya 'ya'yansu kaciya a tare, sukan sanya 'ya'yansu makaranta idan sun isa a sanya su, ma}wabci kan ha]a yaransu mata aure ko kuma a ha]a bukinsu a tare, a wasu lokuta ma ma}wabci kan biya wa ma}wabcinsa ku]in haraji ko na makarantar yaransa ko ma wutar lantarkin da ya sha ko ruwan da sha.

Duk wa]annan abubuwan sukan nuna irin dan}on zumuncin da ma}wabtaka kan haifar a zamantakewar Hausawa. A wasu lokuta ma}wabci kan yi wa ma}wabcinsa abin da ko ]an'uwansa na jini ba ya iya yi masa saboda da]in zamantakewar da ke a tsakaninsu.

Sannu a hankali sai wa]annan al'adun kula juna suka ]auki sabon salo, inda ake ta samun rigingimu da rashin jituwa a tsakanin ma}wabta. Wa]annan abubuwan sukan faru ne a dalilin yanayin sauyin rayuwar da Hausawa suka ci karo da ita ne na rungumar ba}in al'adu da suka koya muna al'adar zaman ka]aici da rashin kula juna, sai aka wayi gari kowa ta kansa yake da iyalansa, ma}wabci bai damu da matsalar ma}wabcinsa ba, hasali ma har son yake ya ji ma}wabcinsa na cikin wata matsalar rayuwa ya yi masa dariya da Allah }ara.

A yau ma}wabci kan yi }arar ma}wabcinsa a kotu ko ga hukumar 'yan sanda ko wata hukumar tsaro a dalilin ya ~ata masa 'ya'ya ta hanyar lalata da su, ko tilasta su aikata wata ~arna da dangoginta. A yau sai ka ji matan ma}wabta ba su ga maciji a dalilin 'ya'yansu, wata }ila 'ya'yan sun yi fa]a ne ko makamancin hakan. Dangane da haka, wa]annan abubuwan sababbin lamurra ne da suka fara samuwa a zamantakewar

Hausawa, ba su cikin nagartattun al'adun Hausawa da suka taso a cikinsu a lokutan da suka wuce.

### 3.1 Dalilan Ma}wabtaka

Dalilan da suka haifar da ma}wabtaka a zamantakewar Hausawa sun ha]a da;

**i. Zama a gida ]aya:** A nan mutane kan zama ma}wabtan juna a dalili zaman su a gida ]aya. A gidajen Hausawa akan sami mutane da dama a cikin gida ]aya suna tafiyar da rayuwarsu ta yau da kullum cikin zaman lafiya da taimakon juna. A irin wannan zama, za a ga cewa dukkan harkokinsu suna tafiya ne a tare musamman abin da ya shafi nomansu da cin abincinsu da sauran lamurran da suka ji~inci sauran ~angarorin rayuwarsu. Hausawa a wannan matakin zamantakewa ta 'yan'uwantaka ba su bari wani abu ya shiga tsakaninsu da zai haifar masu a rarrabuwar kawuna ko rashin jituwa da tashin hankali, idan ma an sami wata matsalar rashin fahimtar juna babba daga cikin gidan zai ja hankalin sauran jama'a da a zauna lafiya tun wani daga waje bai san an yi ba. Wannan aikin ma}wabtakar cikin gidan Bahaushe ken an a zama irin na gandu (maigida da iyansa).

**ii. Zaman gidajen mutane a kusa da juna:** A tsarin wannan zamantakewa za a tarar cewa gidajen Hausawa sukan ha]a ginarsu ne wata a jikin wata. Wani lokaci ma}wararar ruwan ma}wabci takan bi ta gidan ma}wabci ne ruwan su fice zuwa wajen gida. A wannan tsarin zamantakewa Hausawa sukan yi hakurin zama da junansu da mutunta junansu da ha]uwa a kashe kunya idan buki ya samu a tsakaninsu.

**iii. Zaman kasuwancin mutane a kusa da juna:** Idan aka sami mutane suna aiwatar da kasuwanci ko shagunansu a kusa da juna, to a nan ma}wabataka ta ginu. Wannan ma}wabtaka takan sanya mutane su fahimci junansu tare da mutunta juna. Akan yi zumuntar sayarwa juna kaya idan na mutum sun }are ko ba ya da nau'in kayan da ake bu}ata, sai ya amso daga ma}wabcinsa ya sayar masa. Wani zumunci a irin wannan ma}wabtaka akwai yi wa juna canjen ku]i ko aro wani lokaci ma har adashen ku]i suke yi. Wannan ya nuna nauyin hul]a da fahimtar juna da ke akwai a tsakaninsu.

**iv. Zaman sana'o'in mutane iri ]aya:** Idan mutane suna aiwatar da sana'a iri ]aya a kasuna ne ko a unguwa, za a ga cewa ma}wabtaka ta shiga ke nan a dalilin gudanar da kasuwanci iri ]aya. Abin lura a nan za a ga cewasun ]auki kansu a matsayin 'yanuwan juna, a wasu lokuta ma sukan kafa }ungiya da sunan sana'ar, a irin wannan hali ya samar da }ungiyar 'yan tumatir ko }ungiyar 'yan nama ko }ungiyar 'yan shinkafa ko ta 'yan doya da sauransu. A wajen tafiyar da ayyukan wa]annan }ungiyoyin kuwa sukan yi iya }o}arinsu su kawo sauyi ga tsarin tafiyar da kasuwancinsu musamman a kana bin da ya shafi }ayyade farashin kaya. Don haka, wannan ma}wabtaka takan haifar da zumunci mai }arfi ta fuskar tallafawa ga wanda jarinsa ya yi rauni ko buki ya same sa a yi masa ajo a tara masa ku]i.

**v. Zama a unguwa ]aya a gari:** Ma}wabtakar zama unguwa ]aya wata kafa c eta sada zumunta a cikin zamantakewar Hausawa. Mutane sukan ]auki kansu abu ]aya musamman idan sun ha]a a wajen unguwar ko ma garin baki]aya, misali idan Bahaushe ya ha]u da ]an'unguwarsu a wata unguwa ko wani gari, zai tsaya su gaisa su kuma tambayi labarin juna. Idan kuma ya gan sa a cikin wata matsala, zai tsaya ya warware masa ita bakin }o}arinsa. Wannan ya nuna irin yadda al'adar ma}wabtaka ke taimakawa wajen ha]in kai a zamantakewar Hausawa.

**vi. Ma}wabtakar {abilanci**

{abilanci shi ne mutum ya ]auki harshensa da addininsa da sana'arsa da sauran al'adunsa da }ima fiye da sauran da ba nasa ba. Wannan nau'in ma}wabtaka ce da ta shafi al'umma baki ]aya. Bahaushe duk inda ya ha]u da ]an'uwansa Bahaushe zai ji  ya ga ]an'uwa. Irin wannan zumuncin yakan faru ne idan aka ha]u a wajen }asar Hausa. Hakan ya haifar da kafa zango-zango na Hausawa a manyan biranen kudancin Nijeriya da sauran }asashe ma}wabta da Hausawa ke zuwa neman abin masarufi. Samar da zango-zangon nan shi ya haifar da samun sarautar sarkin Hausawa a wajen }asar Hausa. A irin wannan ha]uwa sukan aiwatar da zumunci a tsakaninsu musamman idan wani ya sami }aruwar aure ko haihuwa ko kuma shari'a ta same shi da 'yangida, Hausawan da ke wurin za su yi tsaye su ga cewa ba a cuce sa ba.

### 3.2 Matsayin Ma}wabtaka

Ma}wabtaka tana da babban matsayi a cikin al'adun zamantakewar Hausawa. Wannan ne ya sa Hausawa suke ba ta muhimmancin da ya dace da ita tun gabanin bayyanar musulunci a }asar Hausa. Bayan zuwan musulunci kuwa sai suka fahimci cewa addinin Islama ya yi kira ga mutum ya kyautata wa ma}wabcinsa idan yana da cikakken imani. Sai suka }ara ba al'adar ma}wabataka muhimmanci.

Dangane da haka, za a iya cewa matsayin ma}wabtaka a rayuwar Hausawa sun ha]a da;

i. Wata kafa ce ta raya zumunci da bun}asa shi.

ii. Wani kaso ne na umurnin Allah daya yi kira ga a kyautata wa ma}wabci.

iii. Wata hanya ce ta samar da zaman lafiya da fahimtar juna.

iv. Wata kafa ce ta taimakon juna.

Wata hanya ce da ke kawo ha]in kai da ci gaban al'umma.

### 4.0 Kammalawa

A cikin wannan darasi an tattauna ne dangane da ma}wabtaka a zmantakewar Hausawa, an kuma yi nasarar fito da bayanai da suka fayyace yadda Hausawa suke amfana da al'adun ma}wabtaka a cikin zamantakewarsu ta yau da kullum. Darasin ya fito da dalilai da kuma matsayin ma}wabtaka a cikin al'adun Hausawa.

### 5.0 Ta}aitawa

A ta}aice darasin kacokan ya yi bayani ne a kan ma}wabtaka da al'adun da ke tattare da aiwatar da ma}wabtakar Hausawa a jiya da yau.A cikin bayanin an lura da dalilan da suka haifar da ma}wabtaka da kuma matsayin ma}wabtaka a zamantakewar Hausawa.

### 6.0 Auna Fahimta

1. Mene ne ma}wabtaka?

2. Wa]anne dalilai ne suka haifar da samuwar ma}wabtaka?

3. Kawo matsayin ma}wabtaka a zamantakewar Hausawa.

## 7.0 Manazarta

Adamu M. (1975) *The Hausa Factor in West African History*, Zaria. NNPC Zaria.

Alhassan, H da Wasu (1980) *Zaman Hausawa*. Zaria, Longman Plc.

Augi, A.R. (1984) The Gobir Factor in the Social and Political History of the Rima Basin. Kundin Digiri na Uku, Zaria, NNPC.

Auta, L. A. (1983) Jima Sana'ar Sarrafa Fata da Muhimmancinta a {asar Kano. Kundin Digiri na Farko, Kano. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Aminu S. (1986) Sana'ar Su a {asar Hausa. Kundin Digirin Farko, Kano. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Bagudu M.I. (1974) *History of the Land of Zazzau*, Zaria. Gaskiya Corporation.

Bargery, G. P. (1993) *A Hausa English Dictionary adn English-Hausa Vocabulary with*

Skinner , A. N. *Some Notes on the Hausa People and their Language. D. Westermann*

*and Suppliment*. Zaria:Ahmadu Bello University Press,.

Bunza, D.B ( 2015) Taubassan Bahaushe: Wani Mashigi na Tantance Asalinsa da Zuriyarsa. Takardar da aka gabatar a taron }ara wa juna sani na }asa da }asa a Jami'ar Jihar Kaduna daga ranar 22th -25th March, 2015, a ]akin taro na cikin Jami'ar.

## KASHI NA 4: Ayyukan sa kai a Zamantakewar Hausawa

## 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna ne dangane da al'adar ma}wabtaka a zamantakewar Hausawa, a wannan darasi kuwa za a mayar da hankali ne game da abin da ya shafi ayyukan sa kai da nau'o'insu a cikin al'adun zamantakewar Hausawa.

## 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi shi ne a }arshen tattaunawar darasin ]alibai ko masu karatu su sami masaniya game da ayyukan sa kai da al'ummar Hausawa ke aiwatarwa domin ci gabansu.

## 3.0 Ma'anar Ayyukan sa Kai

Wa]annan wasu ayyuka ne da al'umma kan sanya kansu aiwatarwa domin ci gaban kansu ba da nufin samun ku]i ko ladan aikin ba ga wa]anda aka yi wa. A cikin kowace al'umma akan sami wasu rukunin mutane ko }ungiyoyi da suke ]aukar nauyin gudanar da ayyukan sa kai ga al'ummar da suke. Hausawa ma ba a bar su a baya ba wajen aiwatar da irin wa]annan ayyukan jin}ai a cikin al'adun zamantakewarsu.

## 3.1 Dalilan Ayyukan sa Kai

A cikin al'adun zamantakewar al'umma akwai abubuwa muhimmai da suke tasowa da kan haifar da bu}atar neman taimakon mutane domin a yi maganin matsalar. Samuwar wa]annan bu}atun ne a wasu lokuta kan sa mutane nemar wa kansu mafita, a kan haka, ]aya daga cikin dalilan da sukan sa bu}atar ayyukan sa kai a cikin al'ummar Hausawa sun ha]a da;

**i. Ta~ar~arewar tsaro**: Mutane kan yi wa kansu mafita idan suka lura da cewa ana yi wa rayuwar barazana ga rashin isasshen tsaro, a irin wannan yanayi ne suke }ir}iro wa kansu dabarun kare kansu ta hanyar samar da 'yan tsaro na sa kai domin tsaron rayukansu da dukiyoyinsu. Misali abin da ke faruwa ke a jihohin zamfarada Katsina da Borno domin su tallafa wa hukumomin tsaro na gwamnati da ake da su.

**ii. Rashin lafiya:** Ga al'adar Hausawa idan aka sami wani mutum ba ya da lafiya, sukan yi iya }o}arinsu na ganin cewa sun samar masa da magani ta hanya yi masa asusun neman taimako domin ya sami abin lura da kansa a wurin jinya. Wannan al'ada ce da ake

girmamawa domin tausayin wanda duk Allah ya jarabta da wata cuta, a wasu lokuta ma akan shirya yi masa gayyar aikin gona idan har ga damina ne ya kamu da cutar rashin lafiya.

**iii. Matsalar rashin matallafi ko galihu:** A cikin zamantakewar Hausawa sukan aiwatar da ayyukan sa kai ne domin a tallafa wa wani ko wata da ke cikin matsalar rashin galihu ta fuskar abinci ko sutura ko kuma muhalli. A wasu garuruwan }asar Hausa, akwai }ungiyoyin kula da maras galihu da marayi wa]anda aikinsu shi ne su nemar wa maras galihu tallafi daga hannun jama'a domin su warware masu matsalar da ke damun su cikin sau}i.

**iv. Kasawar gwamnati wajen samar da bu}atun mutane:** A yau jama'a sun fahimci cewa gwamnatoci a mataki daban-daban sun kasa wajen biyan bu}atun mutanensu. Wannan matsalar ta taimak wajen zaburar da Hausawa }ir}iro ayyukan sa kai domin maganin wasu daga cikin matsalolin da suke addabar su. A sakamakon irin wa]annan ayyukan ne gina makarantu da rijiyoyi da ma samar da magunguna a asibitoci domin amfanin jama'a.

**v. Bu}atar ci gaba mai ]orewa:** A kowace irin al'umma akan samu wasu mutane da suke da kishin ganin yankinsu ya ci gaba, a tunanin wa]annan mutane a kodayaushe bai wuce gano hanyar da za su bi wajen kawo ci gaba mai ]orewa ba a yankin da suka sami kansu. Don haka, irin wannan bu}atar ta samar da abubuwan ci gaba ga yanki kan haifar da su }ir}iro da wani aiki na sa kai domin samar da mafita.

## 3.2 Rabe-raben Ayyukan sa Kai

Ayyukan sa kai a zamantakewar Hausawa kamar sauran al'ummu musamman a irin }asashe masu tasowa suna da yawa. Ana gudanar da wa]annan ayyukan ne saboda dalilai mabambanta kamar yadda za a gani a bayanan da suke biye kamar haka;

### 3.2.1 Aikin Gayya

Wannan yana ]aya daga cikin rabe-raben ayyukan sa kai da Hausawa suke gudanarwa idan bu}ata ta samu. Aikin gayya shi ne ha]uwar da mutane ke yi domin su yi wani aiki

CNHN (2006:163). Akwai wasu ayyuka da Hausawa kan ha]u su gayya domin a tallafawa wani ko wata a cikin al'umma. Irin wannan aiki galibi ba wata ladan aikin ake nema ga wanda aka yi wa ba, a'a ana dai yi ne domin a taimaka a kawo sau}i ga wanda ake yi wa, shi ya sa ma ake kiran ]aya daga cikin ayyukan sa kai da Hausawa suke aiwatarwa a cikin al'adun zamantakewarsu. Wa]annan ayyukan gayya kuwa sun ha]a da;

### 3.2.1.1 Gyaran Hanya

Aikin gayya irin na gyaran hanya ko titi aiki ne da Hausawa suke yi domin kawo sau}in sufurin mutane da kaya a kowane sa}o da lungu na }asar Hausa. Kasawar gwamnati ne ya haifar da irin wa]annan ayyukan jin}ai a cikin mutane. Irin wannan aikin a wasu lokuta ba kan hanya ka]ai abin ke tsayawa ba har da magudanun ruwa jama'a kan yi gayya domin a gyara hanyoyin da ruwa ke wucewa domin a kaucewa faruwar ambaliya musamman a cikin damina. Galibi an fi samun irin wannan aikin gayya a karkara da }auyuka inda ci gaba bai kai ba.

### 3.2.1.2 Gyaran Ma}abartu

Gyaran Ma}abartu da samar da kayan aikin kula da su kamar itace da ciyawa da ruwa da biyan masu gadin ma}abartun duk ayyuka ne na sa kai da al'umma ke gudanarwa domin a kawo sau}i a cikin sha'anin bizne mamata (gawa )da kula da ita. Wa]annan ayyukan ba al'ada ka]ai ta yi masu tanadi ba, addinin musulunci ma da Hausawa ke bi, ya umurce su da kula da 'yanuwanmu matatu da aka bizne a ma}abartu da cewa mu zan ka ziyartar su da kuma kula da }aburburansu wajen rufe ramuka idan da akwai da dangoginsu.

### 3.2.1.3 Gayyar Noma

Gayyar noma aiki ne da ake ha]uwa a gonar sarakuna ko surukan mutum domin a rage masu hawalar kula da gonakkinsu. A fahimtar Abdullahi (2008:113) ya ce

> Gayya na nufin jama'a su taru su yi wa wani daga cikinsu aiki, musamman noma ko gini ta yadda za a sauwa}a masa ba tare da an yi jingar abin da za a biya masu aiki ba. Wato ganin dama c eta tara mutane a yi wa mutum aiki kyauta.

A bisa al'ada, Hausawa kan yi gayya noma a matsayin toshi ko wata hanya ta nuna so ga mace, akan samu cewa a wasu lokuta saurayin da ya shahara a noma zai dubi gonar wani dattijo ya kai masa gayya. Da farko zai fara gayyatar samari cewa akwai noma a gonar wane, zai tabbatar da cewa dattijon da za a yi wa gayyar noman bai sami labarin noman ba bale ko da ruwa ya kai ma masu noman. A irin wannan gayya za a ga cewa sha'awa ce da }auna ko jin}ai  kawai na haifar da a yi masa noma.
Galibi idan ranar noma ta zo, samari za su ha]u da yammaci a nufi gonar da dare a kwana a can ana ta noma har gari ya waye, idan aka }are aiki, mai gonar zai tambayi jama'a cewa wane ne ya sa a yi gayyar, idan ya gano wanda ya sa aka yi aikin yakan bad a tukuicin ]an akuya ko tunkiya ko ma ]an maraki (shanuwa) ga jama'ar da suka yi aikin, su kuma sai su yanka su ci nama.
Wata gayyar kuwa a gonar sarakuna ake yin ta. Ana gudanar da gayyar ne shekara-shekara zuwa }arshen damina. Yadda ake yin gayyar, idan za a yi akan raba goron gayyata a cikin gari da }auyuka ma}wabta da cewa an sa rana kaza domin yin noma a gonar sarki. Tun ana kwana ]aya kafin wasan, gari zai yi harama da ba}i masu halartar wasan. Idan safiya ta yi  da misalin }arfe tara na safe, sai jama'a su fita zuwa gonar sarki inda za a gudanar da wasan. Wurin zai cika da mutane da mawa}a da maka]a da samari da 'yanmata.
Gayyar noman tana ha]a dan}on zumunci a tsakanin mutane kwarai da gaske, domin a irin wannan ha]uwar ce ake samun abokai na har abada, musamman ba}in da suka zo da kuma 'yan gari masu saukar da ba}i. A ]ayan ~angaren kuwa, 'yanmata sukan sami mazajen aure a dalili da gayyar noma, domin aikin 'yanmata a wajen gayyar noma shi ne bai wa mazaje ruwan sha da kuma shafe masu gumi (zufan jiki) idan suna noman ana yi masu ki]a. Ba wai sai yarinya ta san mutum ba take ba shi ruwa ya sha, a'a 'yanmata sukan bai wa manoma ruwa ne idan sun birge su a fagen noman.

### 3.2.1.4 Taimakon Gajiyayyi da Maras Lafiya

Wannan ]aya ne daga cikin ayyukan jin}ayi da Hausawa suke gudanarwa a cikin zamantakewarsu ta yau da kullum. Taimako irin wannan ana bayar da shi ne ga tsofaffi

maras lafiya ko galihu ko matallafi. Hanyoyin da ake bi a tallafa masu sun ha]a da ba su abinci ko ku]i ko magani ko kuma mahallin zama (gina ]aki ko gida). Hanyar samun ku]in aiwatar da wa]annan ayyukan sa kai kuwa , shi ne ta hanyar neman tallafi ga jama'a masu hali (ku]i) da ke cikin al'umma. A wasu lokuta kuwa da yake aikin ya shafi }ungiyar taimakon gajiyayyi ne sukan tunakari gwamnatin yanki da neman a tallafa wa aikin da suke na jin}ai.

A wani lokaci kuwa idan suka sami wani maras lafiya sukan ]auki nauyin jinyarsa a asibiti har ya sami lafiya. Wannan ya nuna muna yadda al'ummar Hausawa suka shahara wajen ayyukan sa kai da suka ji~inci jin}ayi.

### 3.2.1.5 Ayyukan Samar da Tsaro

Tsaro na nufin shirya ko gyara ko jera wani abu domin samar da wata kariya daga ~arna. Sarkin Gulbi (2015:7) Samar da tsaro ya kasu kashi biyu a cikin zamantakewar Hausawa, kashi na farko shi ne wanda ya shafi dabarun tsaro irin na gargajiya. Kashi na biyu kuwa shi ne ya shafi tsaro irin na hukuma ko hukumomi. Wa]annan dabarun tsaron sukan tafi ne kafa]a-kafa]a da juna idan ana son a yi nasarar samar da shi. To me ake son a tsare? A bisa al'ada akan samar da tsaro ne a mataki biyu kamar haka;

i. **Tsaro na jiki**: Wannan tsaro ne da ya shafi dabarun kariyar kai daga cuta, misali akwai magungunan tsari irin su; Baduhu da layar zana da sagau da shashatau da kuma magungunan tauri da makamantansu wa]anda ake tanada domin samun kariya daga cuta ko ~acin rana.
ii. **Tsaro na gari**: Wannan nau'in tsaro ana yin sa ne domin samar da kariya ga gida da dukiya da gari ko yanki. Daga cikin matakan wannan tsari na tsaro sun ha]a da; kafin gida ko gona ko mata da katanga ko darni ko ]aurin gari ko ha}o ko ganuwa ko }ofa ko kura waje da sauransu. Akan yi amfani da wa]annan nau'o'in tsaro ne a gargajiyance domin a samar da tsaro ga gida ko gari ko kuma yanki ko wata dukiya.

Shigar al'umma ga sha'anin tsaro wani sakaci ne daga gwamnatoci, domin da ba su yi sake da dabarun tsaro da jami'ansu suke da shi ba aka siyasantar da lamarin tsaro, da

babu bu}atar samar da wasu }ungiyoyin sa kai ga tsaron }asar Hausa. Wannan ne ya haifar da samuwar }ungiyoyin banga a fa]in }asar Hausa.

### 3.3 Matsayin Ayyukan sa Kai

Ayyukan sa kai kamar yadda sunan ya nuna ayyuka ne da suka danganci ji}ai ga al'umma ba tare da niyyar samun wata ladan ku]i ko yabo ba daga wa]anda ake yi wa. Ayyuka ne na sadaukar da rayuwa wajen bayar rayuwa da jini mutum wajen aiwatarwa, domin Allah ka]ai ya sa iya mutanen da suka rasa rayuwarsu a dalilin irin wa]annan ayyuka.

## 4.0 Kammalawa

A cikin wannan darasi an tattauna ne dangane da al'adar ayyukan sa kai na jin}aid a al'ummar Hausawa kan aiwatar a bisa dalilai mabambanta. An yi nasarar fayyace ma'ana da dalilai da kuma rabe-raben ayyukan sa kai a cikin al'ummar Hausawa. Darasin ya fito mana da matsayin wa]annan ayyuka a al'adance.

## 5.0 Ta}aitawa

A dun}ule darasin ya tafi ne a kan tattauna muhimman batutuwa da suka shafi ayyukan sa kai da Hausawa suke aiwatarwa domin ci gabansu ta fuskar tattalin arziki da walwala da kuma tsaro.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Mene ne ayyukan sa kai a zamantakewar Hausawa?
2. Kawo dalilan da suka haifar da bu}atar samar da ayyukan sa kai.
3. Fayyace rabe-raben ayyukan sa kai da ka sani a }asar Hausa.

## 7.0 Manazarta

Abdullahi I.S.S. (2008) "Jiya Ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan

Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa.” Kundin Digiri na Uku. Jami’ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.

Bunza A. M. (2013) “Death in Hausa:  A Folkoric  Perspectives.” A paper presented

 at the International Conference on Folklore. In Hounor of Professor [andatti Abdul}adir, Bayero University, Kano.

Bunza A. M. (2011) *Al’adun Hausawa Jiya Da Yau: Ci gaba Ko Lalacewa?*  Kada

Journal of Liberal Arts Vol.5.

C.N.H.N. (1981) *Rayuwar Hausawa.*Thomas Nelson Publishers Lagos.

C.N.H.N (2006) *{amusun Hausa.* Jami’ar Bayero, Kano.

Sarkin Gulbi, A.  (2015) “Dabarun Tsaro A {asar Hausa: Bin Diddiginsu A MasarautarKasar Hausa”. Takardar da aka gabatar a taron }ara wa juna sani na }asa  da }asa. Wanda }ungiyar Masana Harshen Hausa ta shiyar da ha]in guiwar Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya na Jami’ar Jihar Kaduna.  A mazaunin Jami’ar Jihar Kaduna. Ranar 22-25 ga watan Maris 2015.

## KASHI NA 5: Ayyukan Dole a Zamantakewar Hausawa

### 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna ne game da ayyukan sa kai wa]anda ake aiwatarwa bisa ganin dama ba tare da an tilasta mai yi ba ko kumasa rai ga samun wani abu na ku]i ko ladan aiki ga wanda aka yi wa. A nan kuma za a tattauna ne dangane da ayyukan da suka wajaba ga mutane a cikin zamantakewar Hausawa ta yau da kullum.

### 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi shi ne a }arshen tattaunawar ]alibai su sami fahimtar ayyukan da suka zama dole a kan al’ummar Hausawa a cikin tsarin zamantakewarsu.

## 3.0 Ma'anar  Ayyukan Dole

Wa]annan wasu ayyuka ne da suka wajaba ga al'umma ta hanyar samawar kansu mafita ga matsalolin da ke iya tasowa a zamantakewarsu ta yau da kullum. Irin wa]annan ayyuka har kullum za a ga cewa wani ba zai iya ]auke wa wani ba, ma'ana dole ne jama'a su tashi tsaye wajen neman abin da za su tafiyar da rayuwarsu cikin sau}i.

## 3.1 Rabe-raben Ayyukan Dole

Ayyukan dole a cikin zamantakewar Hausawa suna da yawan gaske, sai dai muhimmai daga cikinsu sun ha]a da;

### 3.1.1 Neman Abinci

Masana da manazarta na ta kai-kawo a kan ma'anar kalmar abinci misali:

Bargery (1934) cewa ya yi "*Duk cimaka shi ne duk wani abu na cimaka ko kuma wanda za a tauna.*"

Koko (1986)  ya ce: *"Abinci shi ne duk abin da in mutum ya ci shi, ya yi masa amfani a jiki"*.

Kamusan Hausa (2006) a cikinsa an yi bayanin abinci da cewa "*Duk abin da ake ci don maganin yunwa"*.

Abinci yana nufin wani abu da ake ci domin maganin yunwa ko }walama. Abincin Hausawa kuwa yana iya ]aukar ma'anar duk wani abu da suke ci a al'adance domin gujewa yunwa ko domin marmari ko  }walama.

Hanyoyin samun abinci suna da yawa kamar yadda al'ada ta tanada, wasu sukan sami abinci cikin sau}i, wasu kuma sai an wahala fiye da zato. Duk dai yadda abin ya kasance, Hausawa sun shahara wajen kazar-kazar ga abin da ya shafi renon tattalin arzikinsu tun a lokaci mai tsawo. Wannan ne ya sa neman abinci ya zamo ]aya daga cikin ayyukansu na

dole. Misali mu dubi sana'ar noma mu ga yadda Hausawa suka ]auke ta da daraja har ta zamo babbar sana'ar da take ri}e da tattalin arzikin }asar Hausa.

### 3.1.2 Koyon Sana'o'i

Koyon sana'a yana ]aya daga cikin ayyukan dole ga al'ummar Hausawa musamman daya yaro ya fara tasowa a na son ya tashi da irin sana'ar da ake yi a gidansu ko unguwarsu. Misali bari mu duba sana'ar gini mu ga yadda maginan Hausa kan yi wajen tsarin koyar da fasahar tsara gine-gine da ginasu ta hanyar barance. Ma'ana, mutum ya bi wanda ya iya abu ya ri}a taya shi yin abun har dai sannu-sannu shi mabiyin ya cimma iyawa da kansa ba tare da tallafin maigidansa ba.

A }asar Hausa akan koyi sana'a ta hanya biyu, ko ta gado ko kuma ta haye (shigege). Kashin farko su ne wa]anda suka gaji sana'ar daga iyaye da kakanni ko kuma suka zamo bayin mai sana'ar. Su ne wa]anda sana'ar ta zamantowa dole, sai in sun bijire sun }i. Kashi na biyu kuma su ne wa]anda suka yi }aura zuwa wata al}arya ko don cirani, ko don neman karatu, ko don gudun abun kunya[9]. Har ila yau, akwai wasu da suke wa sana'ar shigege saboda ta}adarai ne, watau Allah ya yi musu baiwa game da wannan sana'ar.

To a bisa tsarin gargajiya a kan koyi sana'a ta hanyar barance ka]ai domin }a'idojin kowace sana'a babu su a littattafai, suna nan a kan masu sana'ar ne kawai. Da]inda]awa, gini sana'a ce ta *a yi a }ware-a-bari-a-sangarce*, domin haka bata koyuwa sai an du}a.

Yaro kan fara barancen koyon gini yana ]an shekara bakwai (7) ko takwas (8). Za a ri}a zuwa dashi fagen gini yana kallon yadda manya suke aikin gini daga farkonsa har }arshensa, misali ha}a }asa, kwa~ata, cu]ata kuma a mulmulata ya zuwa tubali. Yaron zai ga yadda ake jefa }asa da yadda ake ca~e ta sannan a maka ta tsakankanin tubala. Ba a sa

---

[9] Misali asalin shahararren mawak'in-fada Mu'azu D'an Alalo d'an malamai ne, yayi wa wak'a shigege. Don haka yayi kaura daga kasarsa Katsina ya koma Damagaram(Niang 2005: 68;Tidjani Alou 2008:6**)**.

yaro wani aiki face ya yi kallon abin da ake yi ko ya yi wasansa da }asa har akan }arfafa shi ya yi tankar gini }arami da hannunsa.

Idan yaron ya kai kamar shekara goma-sha-uku (13) zuwa shekara goma-sha-biyar(15) sai a fara sa shi }ananan ayyuka, kamar ]ebo ruwa, yanko ciyawa ko cu]a }asa gwargwadon }arfinsa, yana aiki ana cin gyaransa. Yana da]a girma da wayo yana da]a samun }wari a kan fasahar gini, ana da]a sa shi wasu ayyukan kamar gyaran bango har sai ya kai munzalin mutum mai kamar shekara goma-sha-takwas (18) zuwa shekara ashirin (20). Daga nan sai a fara sa shi manyan ayyuka kamar tayar da bango ko rufin *kate-kate*[10]. Za a da]a samun shekaru biyar (5) zuwa shekaru bakwai (7) kafin maigidansa ya sakar masa wani }aramin gini ya ja baya yana kallo. Da haka ne har ya kai an yabi hankalinsa, da fahimtarsa da hazakarsa kafin tura shi aiki wata unguwa ko wani gari shi ka]ai. Idan ya gama ginin sai maigidansa yaje ya gani, in da gyara a nuna masa.

### 3.1.3 Neman Ilmi da Inganta Tsarin Bayar da Shi

[10] Wannan shi ne mafi saukin rufi.

**Ilmi babban jigo ne a rayuwar mutum da al'umma baki ]aya. Masana irin su Aristotle (322-384 BC) da Aurobindo (1872-1950) da Bargery (1934: 475) da Henry Smith (1962) da Lepage (1964) da kuma Gusau (2010) duk sun tafi a kan cewa ilmi wata hanya ce da mutum yake amfani da ita domin ya amfani kansa da al'ummar da yake rayuwa tare da su. Dangane da haka, za a iya cewa ilmi ya kasance mabu]i ga samun abinci ta hanyar kyautata noma da sana'o'i da fasaha da tattalin arziki da sauran abubuwan da suka ji~inci jin da]in rayuwa. A wani ~angaren kuwa ilmi yakan zamo tamkar wata kafa ta kyautata al'adu da ha]a kan al'umma da nufin samar da manufa ko al}ibla guda**

**Neman ilmin addini da na zamani abu ne daga cikin ayyukan dole ga al'ummar Hausawa, dalili kuwa shi ne da ilmi ne al'umma kan ci gaba har ta tsere wa tsara. Kowace al'umma tana bugun gaba da yawan masu ilmin da take da su.**

Dangane da haka, a }asar Hausa akwai tsarin ilmi guda uku muhimmai da muka tashi cikin su. Wajen gane wannan kason kuwa sai an lura da zamunnan da wa]annan al'ummu suka sami kansu (wato gabanin da kuma bayan zuwan addinin Musulunci da Turawan mulkin mallaka). A bisa kula da wannan zamunnan ne sai ake ganin akwai rabe-raben ilmi a }asar Hausa kamar haka;

i. Ilmin Gargajiya (tatsuniya, da koyon fasahohin sana'o'inmu)
ii. Ilmin Addinin Musulunci
iii. Ilmin Boko

**3.1.3.1 Ilmin Gargajiya (Tatsuniya, da Sana'o'inmu)**

Wannan ilmi ne da al'umma suka tashi da shi tun fil azal, wato tun kafin su sadu da wasu al'ummu kamar Larabawa da Turawa. Irin wannan ilmi ya shafi dabarun zaman duniya da ake tsinta ko koyo a cikin tatsuniya da kuma koyon fitattun sana'o'in al'umma na gado da aka tashi cikinsu kamar noma da wanzanci da gini da su (kamun kifi) da fawa da sa}a da sassa}a da sauransu.Wani abin sha'awa a cikin sana'o'in za a tarar da cewa al'umma sun dogara ga sana'o'in wajen tafiyar da rayuwarsu ta yau da kullum.

**3.1.3.2 Ilmin Addinin Musulunci**

Ilmin addinin Musulunci shi ne ilmin da yake ]auke da yadda mutum zai san addininsa na musulunci da kuma yadda ya kamata ya bauta wa Allah mahalicci. Sanin haka kuwa, ba zai yiyu ba sai an bi wasu matakai na kaiwa ga nasarar samun ilmin. Wannan ne ya sa kowane irin neman ilmi ake da tsarin da ake bi wajen samar da shi. Don haka, ilmin addinin Musulunci a }asar Hausa bai samu ba sai bayan da al'ummar yankin suka yi na'am da kiran da addinin Musulunci ya yi na jama'a su nemi ilmi da kyautata aiki da shi. Wannan kira da addini ya yi ne ya sa neman ilmin ya zama ]aya da cikin ayyukan dole ga namiji da mace.

### 3.1.3.3 Ilmin Boko

Ilmin boko shi ne ilmin da ya zo wa al'umma bayan ha]uwarsu da Turawan Misham da 'yan Mulkin mallaka[11]. Turawan misham sun yi }o}arin cusa wa 'yan }asa ilmin boko ne domin su ji sau}in cusa manufofinsu na ya]a addinin Kiristanci ga jama'a. Su kuwa Turawan mulkin mallaka sun yi hakan ne domin 'yan }asa su ilmantu don su taimaka masu wajen gudanar da mulki. Da aka samu 'yan }asa masu ilmin boko sai aka }ir}iro da hukumomin en-E -en- E (*Native authority*).

**Tsarin bayar da ilmi musamman ga yara almajirai masu karatu a makarantun allo yana bu}atar kwaskwarima. Domin rashin kyautata tsarin bayar da shi ga almajirai shi ne }ashin bayan samun yawaitar }aurace-}auracen malamai da almajirai daga }auyuka zuwa birane da niyyar neman ilmin addinin Musulunci.**

Dangane da yadda za a kyautata tsarin bayar da ilmin kuwa, abu ne da ke bu}atar taimakon gwamnati da kuma al'umma musamman masu hannu da shuni (masu ku]i).

A ~angaren gwamnati ya kamata ta kafa kwamitin da zai zagaye ya }ididdige yawan makarantun allo da na Islamiyya a kowane sa}o da lungu na }asar da }u]urin kyautata yanayin tafiyar da tsarin bayar da ilmi ga ]imbin almajirai da ]aliban da ke karatu a wa]annan makarantu. Bayan an gano sakamakon binciken, abu na farko da ya kamata a yi shi ne, fitowa da hanyar ciyar da almajirai a makaratun allo da kuma samar wa da

---

[11] Yahaya I.Y *Hausa A Rubuce* NNPC 1995, shafi *23.*

malamai ]an alawus a kowane }arshen wata domin rage ‘yan matsalolinsu na yau da kullum. Haka kuma a samar wa almajiran gona }atuwa da za su rin}a noma abincin da za su ci a shekara, tare da samar masu da ingantaccen iri da takin zamani da kuma magungunan }wari domin samun amfanin gona mai kyau. Yin hakan zai }ara sa himma ga aikin koyo da koyarwa.

### 3.1.4 Biyan Harajin  Kasuwa

Biyan haraji a }asar Hausa ya samu ne bayan da Turawan mulkin mallaka suka yi nasarar shimfi]a salon mulkinsu a fa]in }asar. Gabanin zuwan Turawa babu wani tsari na biyan haraji ga gwamnati, sai dai akwai tsarin }ar~ar zakka da raba ta ga mabu}ata wadda ake tanadi a baitulmalin musulunci. Bayan Turawa sun yi nasarar rusa tsarin }ar~ar zakka da wa}afi a hannun mutane, sai suka }ir}iro da hanyar }ar~ar haraji da jangali ga mutanen }asar Hausa da nufin wai su gina }asa. Tilasta biyan haraji da aka yi ga mutane ta hanyar sarakuna shi ya haifar da zaman sa ]aya daga cikin ayyukan dole da ake sa ran al’ummar }asar Hausa su ri}o da su. Misali, mu dubi irin yadda ake }ar~ar haraji a kasuwanni na kayayyakin da ake kai wa a kasuwa a fa]in }asar Hausa, wannan misalin ya isa ya tabbatar muna da yadda aka ]auki biyan haraji da muhimmanci a }asar Hausa.

## 4.0 Kammalawa

Bayanan da suka gabata a cikin wannan darasi, sun tafi ne a kan fayyace ayyukan da suka wajaba ga al’ummar Hausawa a cikin zamantakewarsu ta yau da kullum. A cikin tattaunawar kuwa an ga ma’ana da rabe-raben ayyukan dole.

## 5.0 Ta}aitawa

A ta}aice darasin yana magana ne dangane da yadda al’umma kan aminta da aikata wasu abubuwa da suka zamar masu wajibi ko dole, wasu daga cikin ayyukan dole ]in nan al’ada ce ta tanade su, wasu kuma sun samu daga matsin lamba na Turawan mulkin mallaka kamar yadda aka gani cikin tattaunawar darasin.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Mene ne ayyukan dole a zamantakewar Hausawa?
2. Tattauna a kan rabe-raben ayyukan dole a zamantakewar al'ummar Hausawa.

## 7.0 Manazarta


Awobuluyi, O. (1976): *The New National policy on Education in Linguistic Perspective*. Uinversity of Ilorin Press.

Gusau, S.M (2010): "Ilmi Garkuwar Al'umma". Takardar da aka gabatar a taron }addamar da Gidauniyar Bun}asa Ilmi a Kaura Namoda, Jihar Zamfara.

Fafunwa, B (1989): *Education in Mother Tongue.* The Primary Education Research Project. Ibadan University Press Ltd.

Koko, H.M (1986). Ire-Iren abincin Hausa da yadda ake yin su a Jihar Sakkwato. Kundin Digiri na [aya, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya UDUS.

Sam, O E, (2009) *Roadmap for the Nigerian Education Sector.* Published by Federal Ministry of Education Abuja.

UNESCO (1953) The Use of Vernacular Languages in Education. Report of the UNESCO meeting of experts, 1951, Paris, UNESCO.

Yahaya I.Y (1995). *Hausa A Rubuce.* Zaria . N.N.P.C


# FASALI NA 3: AL'ADUN MUTUWA DA BARKWANCIN HAUSAWA

## KASHI NA 1: Al'adun Mutuwa

## 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna ne game da ayyuka dole ga al'ummar Hausawa. A nan kuma za a yi bayani ne game da al'adun mutuwa, ta la'akari da ma'anarta da sunayenta da dabarun gane afkuwarta.

## 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce a }arshen tattaunawar ]alibai su sami masaniya game da yadda al'adun mutuwa ke gudana a al'ummar Hausawa musamman gabani da bayan zuwan musulunci a }asar Hausa.

## 3.0 Ma'anar Mutuwa

Kalmar mutuwa ba}uwar kalma ce da aka aro daga harshen Larabci watau "Al Mawt." A Larabci tana nufin }arewar rayuwa ko amfanin wani abu. A harshen Hausa kuwa, kalmar tana nufin rasuwa[12] ko }arshen ran mutum ko dabba ko duk wani abu mai rai[13]. Don haka, babu yadda za a yi a sami zaman makoki ba tare da an sami sanadin mutuwa ko rasuwa ba. Asali ma al'ada da addinin Bahaushe duk sun aminta da faruwa mutuwa a kan kowace rayuwa da ke a doron }asa. Mutuwa kan riski mutum ta hanyoyi daban- daban, wani rashin lafiya, wani hatsari wani lokaci kuma haka kurum idan kwana ya }are.

A ra'ayin Abdullahi (2008:309) ya ce:

> "Rasa rayuwa ko barin aiki ga abu mai rai ko marar rai,
> mutum ko dabba ko tsiro ko wata halitta ko kuma wani
> abu mai amfani ta yadda ake ganin alamun ba zai ta~a dawowa
> yadda yake a da ba kafin }addarar rasa rayuwar ta auka masa."

A nawa hange kuwa, mutuwa ita ce }arewar abu mai rayuwa ko lalacewar abu maras rayuwa, ya zama ba za a iya sake wani amfani da shi ba kamar yadda aka saba a da face sai an gyara abin nan, misali mota da sauran injiman na'ura.

## 3.1 Sunayenta

[12] Dubi Abdullahi I.S.S "Jiya Ba Yau Ba:Waiwaye a kan Al'adun Matakan Rayuwar Maguzawa Na Aure Da Haihuwa Da Mutuwa. Kundin Digiri na uku UDUS, 2008, Shafi na 297-303. Dangane da sunayen Mutuwa na asali a cikin Harshen Hausa, kamar rasuwa, raguwa, fakuwa, kaura, kasawa, wucewa, shukuwa, rigaya, ya kau, karewa, dogon kwana/barci da sauransu sai a duba wannan shafin da aka ambata.

[13] Dubi *Kamusun Hausa* domin karin bayani 2006 CSNL, Kano, shafi na 354. Da Bunza AM "Death in Hausa: A Folkoric Perspectives" 2013, A paper presented at the international conference on folklore. B.U. Kano.

Bahaushe yakan yi amfani da kalmomi da dama wa]anda kan maye gurbin sunan mutuwa. Sai ga dukkan alama kalmomin sukan ji~inci rasa rayuwar mutane ne ko dabba.

Ka]an daga cikin kalmomin da suke wa}iltar sunan mutuwa ga Hausawa kamar yadda Abdullahi (2008:297-306) ya fa]a sun ha]a da;

i. Rasuwa

ii. Raguwa

iii. Fakuwa

iv. {aura

v. Kasawa

vi. Tafiya

vii. Dogon Barci/kwana

viii. Wucewa

ix. Shukuwa

x. Rigaya

xi. Ya kau

xii. {arewa

xiii. Shurewa

xiv. Rai ya yi halinsa

xv. Babu shi

xvi. Kwanta dama

xvii. Wafati

xviii. Halaka

xix. Ya sa kai

xx. Ya shuri bokiti

## 3.2 Dalilan faruwar Mutuwa

A imanin Bahaushe mutuwa kan faru ne bisa ga dalilai mabambanta, duk da yake yana da ya}inin faruwar mutuwa irin ta ba zato ba tsammani, wadda ake ganin mutum kawai ya

yanke jiki ya fa]i. Irin wannan tunanin ne ya biyo har zuwa ga Hausawan yau, inda za a ga da an sami sanarwar mutuwa sai ka ji ana tambayar “Rashin lafiya ne ko hatsari.”

Dangane da haka, wasu daga cikin dalilan da kan haifar da samuwar mutuwa a Bahaushen tunani sun ha]a da;

i. Tsufa

ii. Rashin Lafiya

iii. Hatsari

iv. Maita

v. Camfi

vi.Annoba

vii. Tsafi

viii. Fa]e/baki

ix. Tsoro

x. Rantsuwa

xi. Ya}i

xii. Shan guba

xiii. Farmakin dabba

xiv. Tsotsayi

### 3.3 Alamomin Fitar Rayuwa

Hausawa suna da wasu fitattun alamomin da suka aminta da cewa idan sun bayyana ga mutumin da yake fama da jinyar rashin lafiya,to ana kyautata mai zaton zama kusa da barin duniya. Wa]annan alamomin kuwa Abdullahi (2008:319-321) da ya kawo sun ha]a da;

1. Tsananin sanyin jiki ko zafin jiki.

2.Farin ido ko rashin }ibtawarsu

3. Bu]ewar baki

4. Rufewar Idanu

5. Karyewar harshe na rashin iya magana mai ma’ana

6. Sha}uwa

7. Yi wa ‘ya’ya da dangi wata muhimmiyar magana (wasiyya)

8. Sandarewar jiki ko ga~a.

### 3.4 Tabbatar da Faruwar ta

Hausawa suna da hikimar tantance faruwar mutuwa gabanin su yanke hukunci an mutu ko bayar da sanarwar mutuwa tun zamani mai tsawo. Hikimar hakan shi ne domin su kaucewa bizne mutum da sauran rayuwarsa ko banza ma akwai abin da suke kira doguwar sumainda mutum zai suma kamar ya mutu ne daga baya a ga yana numfashi. Dangane da haka, daga cikin dabarunsu na gane rai ya yi halinsa ( an mutu)sunha]a da;

i. Fesa ruwa a jikin maras lafiya, yin hakan zai sanya idan yana da sauran rayuwa a gay a motsa,

ii. Motsa babbar yatsar }afarsa

iii. Bugun hannu a }asa kusa ga kansa, a nan za a bugi hannu a}alla sau uku.

iv.  Za a kira sunansa a gani ko za ya motsa.

v. Akan zuba yashi a }irjinsa a gani ko zai motsa.

Idan duk an yi wa]annan dabarun aka ga bai motsa ba to daga nan za a yanke hukuncin rayuwarsa ta fita sai a dangana. Daga nan sai fa]ar mutuwa ga dangi da abokan arziki.

### 3.5 Bizne Mamaci

Hausawa sukan bizne mamaci da tun a ranar da ya mutu, sai fa idan tsakiyar dare ne akan bari sai da safe a bizne gawar. Duk da yake akwai masu ra’ayin cewa wasu maguzawan Hausawa sukan bar gawa har bayan kwana uku  Ibrahim (1982:232). Akasarin Hausawa sukan bizne gawa ne tun ranar da aka yi rasuwa, wannan al’adar kuwa ana gudanar da ita ne tun gabanin bayyanar musulunci ga Hausawa. Yanayin ha}ar ramen da za a bizne gawa kuwa  akwance ne akan sanya gawa. Kuma akan sanya mutum da kayan aikinsa kamar warki ko makamansa a cikin }abari, idan kuma mace ta akan sanya ta da kayan aikin gida da saba amfani da su. {ananan yara kuwa sai a shafa masu shuni a fuska wai idan sun je su ba mutuwa tsoro kar da sake dawowa ta ]auki wani.

Bayan zuwan musulunci sai abin ya sauya, inda kafin a bizne mamaci sai an yi masa wanka an sanya masa turare da kuma sutura. A yi masa sallah sa'annan a kai shi }abarinsa.

## 3.6 Al'adun Mutuwa Gabanin Musulunci

A nan darasin zai karkata ne zuwa fayyace wasu fitattun al'adu Hausawa kan yi game da sha'anin mutuwa tun gabanin zuwan musulunci a }asar Hausa. Wa]annan al'adun kuwa sun ha]a da;

- Amfani  kwarya wajen wanka tare da kife su da zarar an gama. Ba za buɗe ba sai ran uku.
- A cika kwaryar da hatsi da kayan mamaci na sawa a ba wa mai wankan gawa, sai kuma a ba wa matar mamaci sanda ta rika yawo da ita wai ko da zai dawo mata ta doke shi.
- Zubar da ruwan randa zarar an yi mutuwa tare da kife randunan da zummar cewa wai ba za a yi amfani da ruwan ba, tun da ba a san da wacce mutuwa ta wanke wu}arta da shi ba. In ma da rijiya a gidan akan yi ƙoƙarin kwarfe ruwan mai tarin yawa a zubar, dan cewar wata}ila da wannan ruwan mutuwar ta wanke wu}ar.
- Sanya wa yara toka a zagaye musu ido, idan ba a sami toka ba sai a zagaya musu bakin tukunya wai don kar su yi mafarki da wannan mamacin.
- Sanya ko ]ora faifai ko takobi ko dutse ko kuma takobi a kan cikin mamacin da daddare, da zimmar cewa wannan shi zai hana cikin ya kumbura kafin wayewar gari.

## 4.0 Kammalawa

A wannan darasi an fito da wasu fitattun al'adun Hausawa game da mutuwa gabanin bayyanar musulunci a }asar Hausa. Darasin ya fito mana da ma'anar mutuwa da dalilan faruwarta da alamominta da dabarun tabbatar da faruwarta da kuma yadda ake bizne gawa.

## 5.0 Ta}aitawa

A ta}aice dai darasin ya fayyace mutuwa da al’adun da ke tattare da sha’anin ta, an kuma yi nasarar fayyace wa ]alibai sanin yadda ake aiwatar da al’adun mutuwa a can da ta la’akari da al’adun da suka yi takin sa}a da na addinin musulunci da ake aiwatarwa a yau.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Wa]anne al’adu ne Hausawa suke yi kafin su tabbatar da faruwa mutuwa?
2. Bayyana fitattun sunayen mutuwa da Hausawa suka samar a maimakon amfani da kalmar mutuwa.
3. Kawo dalilan da Hausawa suke ta’alla}antawa da cewa su ne musabbabin faruwar mutuwa.

## 7.0 Manazarta


Abdullahi I.S.S “Jiya Ba Yau Ba:Waiwaye a kan Al’adun Matakan Rayuwar Maguzawa Na Aure Da Haihuwa Da Mutuwa. Kundin Digiri na uku UDUS, 2008

Bunza AM (2013) “Death in Hausa: A Folkoric Perspectives” A paper presented at the international conference on folklore. B.U. Kano.

C.N.H.N (2006) *{amusun Hausa.* Jami’ar Bayero, Kano.

Ibrahim, S.M (1982) “ Dangantakar Al’ada da Addini: Tasirin Musulunci Kan Rayuwar Hausawa”. Kundin Digiri na biyu, Jami’ar Bayero, Kano.


## KASHI NA 2: Zaman Makoki

## 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an dubi al’adun mutuwa a al’ummar Hausawa ta la’akari da dalilan faruwar ta da sunayenta da al’adun da ke tattare da ita har zuwa bizne mamaci. A nan kuma za a tattauna ne game da zaman makokin Hausawa da gudunmawarsa wajen bun}asa zumuncin Hausawa.

## 2.0 Manufar Darasi

Manufar darasin shi ne domin ]alibai su sami masaniya game da wasu al'adun zaman makokin Hausawa daga }arshen darasin.

## 3.0 Ma'anar Zaman Makoki

Makoki kalma ce da ta samo asali daga jam'in suna makoka (masu kuka a sanadiyar rashin mutum ko ba}in cin rasa rayuwarsa). Wannan wani wuri ne da mutane kan zauna suna kar~ar gaisuwa bayan an yi rasuwa. Dalilin hakan ne ake yi wa abin la}abi da zaman makoki[14].

Zaman makoki, zama ne da ake yi bayan an binne mamaci, sai duk jama'a su taru a gidan da aka yi mutuwar a ]an zauna na 'yan wasu lokuta ana yi wa 'yan uwansa gaisuwa na nuna juyayin rashin da aka yi. Daga nan sai wasu su watse, sai a bar 'yan uwa na jini da abokan arziki su ci gaba da zaman makokin. A tsarin irin wannan zaman maza kan zauna ne a kofar gida suna kar~ar gaisuwar, yayin da mata ke cikin gida domin kar~ar gaisuwar mata 'yan'uwansu. Hikamar yin hakan ba }arama ba ce, ta la'akari da irin taka- tsantsan da musulunci ya yi na ha]uwar maza da mata a bagire ]aya. A }a'idar wannan zaman akan kwashe a}ala kwana uku ana kar~ar gaisuwar. Wasu kuwa sukan yi kwana bakwai ne, idan wani mutum mai muhimminci ya mutu a cikin zuri'a, ta la'akari da irin jama'ar da ke zuwa daga kusa da nesa. A bisa bayanan da suka gabata, za a ga cewa dukkan bayanan sun tafi a kan cewa zaman makoki ana yin sa ne domin juyayi na rashin da aka samu na mutuwar wani daga cikin al'umma.

## 3.1 Zaman Makoki Kafin Bayyanar Musulunci

---

[14] Dubi Muhammad, S.I Dangantakar Al'ada da Addini Tasirin Musulunci kan Rayuwar Hausawa". Kundin digiri na biyu, Jami'ar Bayero, Kano, 1982, Shafi na 233-245.

Gabanin Bahaushe ya sadu da addinin musulunci akwai al'adar makoki a cikin tsarin rayuwarsa. Watau zama na 'yan wasu kwanaki bayan mutuwar mamaci don a yi juyayin rashin da aka yi da kar~a gaisuwa daga mutanen da ke ziyartar wurin. Akan yi hakan ne domin taya dangin mamaci ba}in ciki ko murnar[15] abin da ya faru. Kwanakin da akan ]auka ana yin makoki sun bambanta daga wuri zuwa wuri, wasu sukan kwashe kwanaki uku ne, wasu kuwa su yi hu]u yayin da wasu kan share kwana bakwai ana amsar gaisuwa musamman idan babban mutum ne ko datijo. Bayan wannan kuma akwai bukin arba'in da na juya kafa]a da ake yi wa mamaci bayan ya cika shekara da mutuwa.

Galibi 'ya'yan mamaci da 'yan'uwansa su ke tsayawa kar~ar gaisuwar da mutane kan zo yi. Dangane da haka ne akan bar duk wani aiki a tsawon wa]annan kwanaki domin a jajantawa juna. Ma}wabta na kusa da na nesa kuwa sukan taimaka da abinci a gidan da aka yi rashin. Dangin mamaci sukan zo da nau'o'in abinci iri daban-daban domin gudunmawa,wasu sukan zo da giya, ko kaji, ko hatsi ko 'yan awaki domin a yankawa mamacin a }abarinsa. Wannan ya nuna cewa zaman makoki, al'ada ce da ke }ara dan}on zumunci, tun a lokacin gargajiyar Bahaushe.

## 3.2 Zaman Makoki Bayan Zuwan Musulunci

A Musulunce zaman makoki abu ne da aka karhanta, inda hadisai suka nuna cewa bidi'a ce wadda aka }yamata.[16] Saboda haka, zaman makoki ba dole ba ne, abin da aka so shi ne, bayan an bizne mamaci kowe ya je wajen harkokinsa, ko sana'arsa, idan mutum ya ga dama ya same sa can wajen sana'arka ya yi masa ta'aziyyar rashin da ya same sa. An yi haka ne ta la'akari da irin matsalolin da ke cikin lamarin, kama da jidalin ciyar da masu zuwa ta'aziyyar, da kuma yawan tunani da juyayin mamacin da za a yi ta yi a lokacin zaman. Wannan al'adar ta ci gaba da bun}asa har bayan da addinin musulunci ya kafu a }asar Hausa. Duk da cewa addinin Musulunci ba }aramin tasiri ya yi ba a rayuwar

[15] Jikokin mamaci a wajensu murna ce, domin suna amfani da makokin ne domin su yi wa mamacin shakiyanci da nuna kasawarsa da raggancinsa a lokacin da yana raye.

[16] Dubi Muhammad Nasir. ***Ahkamul Jana'iza wa Bidi'uha*** 1992, K.S.A, Riyard. Shafi na 205-212.

Hausawa, wajen fa]a da miyagun al'adu da gyara halayen al'umma. Wannan bai sanya al'adar zaman makoki ta kau ba. Illa dai an sami 'yan sauye-sauye na barin ]abi'ar yanke-yanke na dabbobi a kan }aburburan mamata da shan giya da kuma ka]e-ka]e a wurin makokin, face ka]an daga cikin al'ummar wa]anda suka rage a cikin rayuwar maguzanci, wanda yake su ma daga baya abin ya kau. Faruwa hakan ba zai rasa nasaba da kiran da addinin Musulunci yake ba a kan barin aikata wa]annan haramtattun ayyuka.

Maimakon hakan, sai aka sami sauyi a wajen lafuzzan gaisuwar ta'aziyyar inda ake danganta faruwar mutuwar a matsayin wani hukunci daga Allah Ma]aukaki Sarki, wanda yake a can da, ana ganin cewa ai kasawar mutum ce, ko rashin juriyarsa.[17] Don haka tun a lafuzzan gaisuwar, za a fahimci cewa ana cikin wata rayuwa ce da ta gabaci samuwar addinin Musulunci a cikin al'umma.

Bayan da addinin musulunci ya bayyana a }asar Hausa, sai mafi yawan al'ummar suka kar~i addinin, kuma suke gudanar da rayuwarsu a }ar}ashin koyarwarsa gwargwadon hali. A dalilin hakan ne lafuzzan gaisuwar suka canza zuwa wani abu da ke da nason addinin Musulunci.[18] Wanda ta fuskar lafuzzan ka]ai ya isa a gane cewa cike suke da tasirin addinin musulunci da nuna tauhidi.

## 3.3 Zaman Makoki da Bun}asar Zumuncin Bahaushe

---

[17] Ana amfani da lafuzzan "Ashe wane bai jure ba?" Ko "Ai wane ya yi kasala." Da sauransu.

[18] Sai aka sauya lafuzzan kamar haka:

"Ashe wani ikon Allah ya faru!"

"To Allah ya jikan sa"

"Ya sa ya huta"

"Y a kuma kyautata tamu in ta zo," da makamantansu.

Zaman makoki ya ci gaba da zama wata kafa ta raya da kuma bun}asar zumuncin Bahaushe tun a jiya da kuma yau. Wannan zancen kuwa haka yake, idan an yi la'akari da irin yadda 'yan'uwa da abokan arziki daga wurare da dama kan ha]u a wajen jajanta wa juna a dalilin mutuwar. Ka]an daga cikin rawar da makoki kan taka wajen bun}asa zumuncin Bahaushe sun ha]a da;

### 3.3.1 Ha]a kan Dangi na Jini

Wannan zumunci ne da ya danganci zumuntar dangin Uwa ko Uba. Galibi idan aka samu rashi ko }aruwa  a cikin dangi za a tarar da cewa an sanar da duk mai ha}}in a sanar da shi domin a taru a jajanta wa juna ko a yi murna.

A sakamakon  irin wannan ha]uwar ce akan }arfafa zumuncin da ke a tsakaninsu. Hikimar wannan shi ne, za a ga cewa 'yan'uwa daga wurare da dama na kusa da nesa sun halarta domin a taya juna ba}in cikin abin da ya faru. A wasu lokuta 'yan Uwan kan yanke shawarar yadda za a taimaka wa marayun da aka bari ta hanyar tallafa masu da abinci ko sutura ko kuma karatunsu. A wasu lokuta kuwa akan rarraba 'ya'yan ne a tsakanin dangi, musamman idan babu babba a cikin yaran da aka bari. Idan kuwa mace ce ta mutu ta bar yara, idan akwai masu }arfi a cikin danginta su ma sukan yi irin wannan taimakon ga yaranta. Faruwar hakan ko shakka babu, wani mataki ne na bun}asa zumunci a tsakanin dangi.

### 3.3.2  Raya Zumuncin Auratayya

Wani babban abin da kan haifar da zumunci na jini shi ne auratayya. Wannan zumunci ne da ke faruwa a sakamakon aure a tsakanin wannan dangi da wancan dangi na rukunin al'umma. Auratayya a }asar Hausa ba sai a cikin }abila guda kawai ake yin ta ba, ana yin auratayya  a tsakanin }abilu daban-daban.

Idan auratayya ta kafu a tsakanin dangi da dangi, to an sami tushen kafa  ginuwar zumunci irin na jini. Samuwar kafa wannan zumuntar ta jini kuwa, yakan sa idan abu ya faru na da]i ko ba}in ciki, mutanen kan yi }o}arin taya juna murna ko jajen abin da ya

faru. Yin wannan murnar ko jajen yana ]aya daga cikin abin da ke }ara dan}on zumuntar da ke a tsakaninsu. Don haka, zaman makokin Bahaushe kan ha]a dangi na ~angaren Uwa da na Uba a waje ]aya domin su jajantawa junansu a kan abin da ya faru. Kuma a irin wannan ha]uwar ce akan fahimci juna. Wata}ila kafin wannan ha]uwar wasu daga cikin dangin ba su san yadda dangantakarsu ta zumunci take ba, ko da suna ha]uwa a wasu harkoki na daban. Daga nan sai a zafafa zumuncin  a kuma ci gaba da biya juna, tare ]aukar kansu abu ]aya. Faruwar hakan ya zama wata hujja ta tabbatar da bun}asar zumunci a dalilin zaman makoki.

### 3.3.3 Kyautata Dangantaka a Tsakanin Ma}wabta

Wannan yanayi ne na zamantakewa inda ake samun jama'a daban-daban da ke zaune a unguwa ko gari ko }auye ]aya suna gudanar  da rayuwarsu ta yau da kullum. A al'adar irin wannan zama za a tarar da cewa, zama ne na 'yan 'uwantaka  a dalilin ma}wabtakar da ke a tsakaninsu. Tasirin  da zamani ya yi a zamantakewar  Hausawa dangane da ma}wabtaka bai kai a }auyukan }asar Hausa ba, abin ya fi }arfi a birane. Idan an ce mutum ma}wabci ne ga mutum, to lallai za a ga cewa ya dage wajen kariyar mutuncinsa da zuri'arsa idan bu}atar hakan ta taso. Duk da yake zamunanci ya so ya yi tasirin gaske ga lamarin zamantakewar Hausawa a yau, ma}wabtaka kan taka muhimmiyar rawa wajen bun}asa zumuncin Hausawa, musamman idan lamarin mutuwa ya gita. Wannan ba zai rasa nasaba da kiran da addinin Musulunci ya yi ba a kan kyautata wa juna a cikin zamantakewar al'umma mai  cewa:

> "Wanda ya yi imani da Allah da ranar
> lahira, to, ya girmama ma}wabcinsa." [19]

Da zarar wani mutum ya mutu a unguwa ko gari musamman a }auyukan }asar Hausa, za a ga mutuwar ta shafi kowa a garin ko }auyen. Mutane kan nuna alhininsu na rashin da aka yi, da su za a yi fa]i-tashin ganin cewa an bizne mamacin da kuma zaman makokinsa

[19] Sheikh Shu'aib 2002: *Hadisai Arba'in da Sharhin a Harshen Hausa.* Riyadh Saudi Arabiya. Hadisi na 15, shafi na 45

ko da ba zumuntar Uwa bale ta Uba. Ba don komai ba sai don zama unguwa ko }auye ]aya da mamacin (Ha}}in ma}wabtaka). Ba zaman makokin ka]ai ake da su ba har taimakon abinci da tabarmi/shimfi]u sukan bayar domin a tarbi ba}in da ke zuwa. Idan ko haka abin ke faruwa a cikin al'ummar Hausawa a dalilin zaman makokin Bahaushe, to ke nan sai mu ce, zumunci ya bun}asa. Dalili kuwa shi ne, akan sami kaiwa }arshen rashin jituwa a tsakanin mutum da mutum a dalilin jajantawa juna da ake yi a sanadiyar zaman makoki[20].

### 3.3.4 {ara Dan}on Zumunta a Tsakanin Masu Sana'a

Zaman makokin Bahaushe kan taimaka wajen bun}asa zumunci a tsakanin mutane masu aiwatar da wasu sana'o'i iri ]aya[21] a cikin al'umma. Idan mutane suna aiwatar da sana'a iri ]aya za su ]auki kansu tamkar 'yanuwan juna. Wannan matsayin da suka ]auka a tsakaninsu, shi ke sanya duk wani abu ya faru na murna ko ba}in ciki, za a ga cewa sun halarta domin nuna murnarsu ko akasin hakan. A sanadiyar ha]uwarsu wajen makokin abokin sana'arsu ko aikinsu sukan fito da shawarar yadda za a taimakawa 'ya'yan mamacin da ku]i ko sutura ko wani abu daban musamman idan babu dangin jini da za su ]auki nauyin yaran. A dalilin rawar da abokan aiki ko sana'ar mamacin suka nuna, sai zumuncin ya ]ore da 'yanuwan mamacin, saboda irin taimako da tausayin da suka nuna wa zuri'arsa.

### 3.3.5 Kara da Gudunmawa

Zaman makokin Bahaushe wuri ne da 'yan'uwa da abokan arziki kan nuna kara da gudunmawa wajen taimakawa da abinci ko abin sha domin tarbon ba}in da ke zuwa wajen gaisuwar ta'aziyyar. Irin wannan kara da gudunmawa da mutane kan kai yana

---

[20] Na shaidi yankewar wata tsohuwar gaba a tsakanin wasu matasa biyu da suka dade ba su yi wa juna magana, sai bayan da aka yi wa dayan rasuwa, bai yi tsammanin abokin gabarsa zai yi masa ta'aziyya ba. Amma da ya zo masa ta'aziyyar daga nan sai suka shirya.

[21] Akwai sana'o'i irin na ma'aska da ma}era da majema da magina da marina da ma'aikatan gwamnati da sauransu wa]anda suka ]auki kansu 'yan'uwan juna a dalilin suna aiwatar da sana'a iri daya. Don

taimakawa ainun wajen }arfafa zumunci da }yautata zamantakewa a tsakanin dangin mamacin da kuma masu kai gudunmawar daga ko'ina suke.

## 3.4 Zaman Makoki a Yau

Zaman makoki a yau cike yake da nason gargajiya da addinin Musulunci da kuma tasirin zamunanci. Don haka, takardar za ta kalli zaman makoki ta wa]annan fuskoki guda uku. A nason gargajiya da aka ce idan an lura za a ga cewa, al'ada ce da ta samo asali tun a rayuwar maguzanci kuma aka ci gaba da aiwatar da ita har ya zuwa yanzu.

A gargajiyance akan kwashe a}alla kwanaki uku ana gudanar da shagulgulan makoki, wasu maguzawan kuwa sukan yi kwana hu]u ko bakwai ko arba'in akan kuma yi bikin shekara, Abdullahi (2008 : 322). A zaman makokin Bahaushe na yau, za a tarar da cewa akan yi kwana uku, sa'annan a yi taron addu'ar bakwai da ta arba'in da kuma shekara. Wanda hakan ya samo asali ne daga Bamagujen makoki, sai 'yan bambance-bambancen da ake samu na aiwatar da addu'o'i maimakon ka]e-ka]e da shaye-shaye da yanke-yanken da ake yi na dabbobi domin a zuba jini a kan }abarin mamaci a can da.

Ta fuskar addini kuwa, za a ga cewa akan yi addu'o'i ne na neman gafara ga mamaci da karance-karancen ayoyin Al}ur'ani. Wa]annan addu'o'i da karance-karancen suna nuna muna irin naso da tasirin addinin Musulunci a sha'anin makokin Hausawa a yau. Duk da yake cewa wasu bidi'o'i ne aka }ir}ira aka danganta da addinin.

A zamunance kuwa, sai a ce, zamunanci ya yi cikakken tasiri a lamarin makokin Bahaushe a yau. Za a iya fahintar hakan ne tun daga yanayin sanar da rasuwar, da kuma yadda aka mayar da zaman tamkar wani buki na murna. Zamani ya kawo sau}i a hanyar sanar da sa}on mutuwa a cikin al'umma da sauran lamurran rayuwa. A halin yanzu akan sanar da sa}on mutuwa ne ta hanyar wayar hannu da gidajen radiyo da na talibijin da jaridu da kuma aikakken sa}o ta wayar hannu da aka fi sani da GSM.[22] Abin ya kai har wasu }e~a~~un lokuta akan ke~e a gidajen radiyo da talibijin domin isar da sa}on

[22] Wasi}u ne da aka aikawa ta amfani da wayar hannu, maimakon a takarda da aka sani a da.

ta’aziyya idan wani babban mutum ya rasu. Inda ake bayyana irin }wazonsa a fannin da ya }ware a lokacin da yake raye.Idan kuma an dubi yanayin zaman makokin kuwa, sai a ga cewa ana kafa rumfuna da shirya kujeru na alfarma da kuma shimfi]u, domin tarbon ba}in da kan zo gaisuwar.

Ta ~angaren shirya abinci kuwa, sai mutum ya yanke hukuncin cewa wani bukin murna ne ake yi, domin irin abincin da ake shiryawa a wajen musamman idan gidan masu ku]i ne, Hakan ya sa mutane musamman maras aikin yi suke marmarin a sami mutuwar babban mutum a cikin unguwa domin su kece raini a wajen abinci. Faruwar hakan, ba zai rasa nasaba da yanayin tattalin arzikin da }asar take ciki ba na rashin abin masarufi a hannun mafi yawan al’ummar. Dangane da haka, zaman makoki a yau ya ha]e gargajiya da nason addini da kuma zamunanci.

### 3.5 Matsalolin Zaman Makoki a Yau da Hanyoyin Magance su

Duk da yake a tattaunawar an mayar da hankali ne a kan nazartar fa’idar da ke tattare a cikin zaman makokin Bahaushe ta fuskar raya zumuncinsa da bun}asa shi. Wannan bai hana a hango irin matsalolin da ke tattare da al’adar ba. Ka]an daga cikin matsalolin sun ha]a da;

1. Wuri ne na tattauna magangannun tsegumi.

2. Wuri ne na kallon matan mutane tare da tantance kyawonsu.

3. Ya zama bagire da maro}a da mabarata kan she}e ayarsu wajen ro}on mutanen da ke zuwa wajen ta’aziyyar, musamman manyan ‘yan siyasa.

4. Wata maha]a ce da marar harkar yi ke ha]uwa domin su sami abincin da za su ci, don su a wajensu wata kafa ce ta samun abinci a sau}a}e.

5. Zaman kan sa mutum tunanin yadda zai yi wajen ciyar da ]imbin jama’ar da ke zuwa ta’aziyyar da kuma masu taya sa zaman makokin.

6. Wata kafa ce ta ya]a manufofin siyasa da tallata kai ga ‘yan siyasa masu neman a za~e su a wasu mu}amai[23].

## 3.6 Hanyoyin da Za a Magance Matsalolin

A nan, takardar ta hango wasu daga cikin hanyoyin da za su taimaka wajen magance ko rage matsalar da zaman makoki kan haifar. Wasu daga cikin hanyoyin da za su taimaka kuwa sun ha]a da;

i. Al’umma su yi ri}o da karantarwar addinin musulunci, wanda ya fayyace yadda ya kamata a yi gaisuwar ta’aziyya ko da a wajen sana’ar mutum ne. Ba sai a gidansa ba.

ii. Rage bai wa al’adar }arfi, musamman a sha’anin makoki.

iii. Kamata ya yi a bar shirya abinci kamar ana bikin murna a wajen taron makoki. Don wasu cin abincin kawai ke kai su wurin.

## 4.0 Kammalawa

Wannan darasi kamar yadda aka gani, darasi ne da ya yi nazarin irin alfanun da ke tattare da al’adar nan ta zaman makoki a cikin al’ummar Hausawa musamman wajen raya da bun}asa zumuncinsu. Nazarin ya gano irin hikimar da ke cikin lamarin makokin Bahaushe wajen ha]a kan dangi da raya zumuncin auratayya da kyautata ma}wabtaka da ha~~aka zumuncin sana’a da kuma irin rawar da kara da gudunmawar Hausawa kan taka wajen kulla dan}on zumunci, musamman a dalilin zaman makoki.

## 5.0 Ta}aitawa

A }arshe darasin ya fayyace matsayin zaman makoki a zamantakewar Hausawa a yau, tare da nazarin irin matsalolin da ke tattare da al’adar zaman makokin Hausawa da kuma yadda za a magance ta.

[23] Wani yawon kai ta’aziyya da ‘yan siyasa ke kai wa, suna yi ne kawai domin su ya]a manufofinsu ga jama’a domin a ce suna da kula ga abin da ya shafi mutanensu.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Mene ne zaman makoki?
2. Kawo alfanun da ke tattare da zaman makokin Hausawa.
3. Bayyana matsalolin da zaman makokin Hausawa kan haifar

## 7.0 Manazarta


Abdullahi I.S.S. (2008) "Jiya Ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al'adun Matakan Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa." Kundin Digiri na Uku. Jami'ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.

Bunza A. M. (2013) "Death in Hausa: A Folkoric Perspectives." A paper presented at the International Conference on Folklore. In Hounor of Professor [andatti Abdul}adir, Bayero University, Kano.

Bunza A. M. (2011) *Al'adun Hausawa Jiya Da Yau: Ci gaba Ko Lalacewa?* Kada Journal of Liberal Arts Vol.5.

C.N.H.N. (1981) *Rayuwar Hausawa.*Thomas Nelson Publishers Lagos.

C.N.H.N (2006) *{amusun Hausa.* Jami'ar Bayero, Kano.

Ibrahim, S.M (1982) " Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci Kan Rayuwar Hausawa". Kundin Digiri na biyu, Jami'ar Bayero, Kano.

Muhammad N. (1992) *Ahkamul Jana'iza wa Bidi'uha*, K.S.A Riyard.

Sarkin Gulbi, A . (2013) Zaman Makokin Bahaushe: Sinadarin Bun}asar Zumunci. *In Detorariation of Hausa Culture Conference Proceedings.* Zaria. ABU Press

Sheikh Shu'aib (2002) *Hadisai Arba'in da Sharhin a Harshen Hausa.* Riyadh Saudi Arabiya.

Tambuwal, M.S. (2001) “Mutuwa a Idon Bahaushe: Nazari daga Wasu {agaggun Labaran Hausa.” Kundin Digiri na [aya. Jami’ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.

## KASHI NA 3: Rabon Gado

### 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna game da al’adun mutuwa a cikin zamantakewar Hausawa, a wannan darasin kuwa za a yi tsokaci ne dangane da gurbin gado a cikin al’adun Hausawa.

### 2.0 Manufar Darasi

Babbar manufar wannan darasi ita ce a }arshen darasin ]alibi ya sami wata masaniya game da al’adun da ke tattare da lamarin gado bayan rasuwar mamaci a }asar Hausa.

### 3.0 Ma’anar Gado

Gado shi ne ainihin dukiya da mamaci ya bari. A wani }aulin kuma ya }unshi mu}ami ko hali ko sifa ko kaya da mutum ya gada. CNHN (2006:149). Don haka, gado wani kaso ne mai cin gashin kansa daga cikin al’adun Hausawa tun gabanin zuwan musulunci ga Hausawa da kuma bayan musulunci, sai kafin zuwan musulunci ga Hausawa ba su da wani takamammen tsari na bai ]aya da suke bi wajen rarraba gadon mamatansu.

### 3.1 Dalilan Rabon Gado

A bisa tsari na gargajiyar Bahaushe sukan mutum kan rarraba dukiyarsa ga ‘ya’yansa musamman idan ya ga ya tsufa da tunanin ya yi kusa ban kwana da mutuwa. Sai duk da haka akan raba gado ne bisa dalilai da dama kamar haka;

i. A dalilin abkuwar mutuwa a cikin gida ko dangi.

ii. Idan mutum ya tsufa yakan raba dukiyarsa ga ‘ya’ya da masoya.

iii. Ana raba gado ne domin kaucewa rikici bayan an mutu.

iv. Hausawasukan raba gado ne domin cika umurnin Allah musamman bayan da suka kar~i addinin musulunci

v. Domina kaucewa cin ha}}in juna.

vi. Domin kowa ya tsaya ga iyakar rabonsa.

## 3.2 Matsayin Gado

A zamantakewar Hausawa musamman a can lokutan da suka shu]e babu wani tsari na musamman da suke amfani da shi wajen rarraba abin da mamaci ya bari a tsakanin ‘ya’yansa ko dangi. Abdullahi (2008:345). Wannan kuwa ba zai rasa nasaba da ganin cewa a can da Hausawa maguzawa ba su cika tara dukiya ba bale a gade su, ]an abin da sukan bari bai wuce gonaki da hatsi da dabbobi ba, wa]anda sukan aje domin tsaron lalurarsu ta yau da kullum.

Wasu Hausawan a waccan lokaci idan sun ga alamar tsufa ya kama su, sukan kira ‘ya’ya da duk wanda yake da ha}}i a cikin dukiyarsu su raba masu ita, wai a nasu tunani, idan sun mutu sun warware rigima a tsakanin ‘ya’yan. Idan kuma aka sami mutum ya mutu bai sami raba dukiyarsa ba, akan ]auki lokaci mai tsawo ba a raba dukiyar ba. wasu ma ko rabawar ma ba za a yi ba har abada, sai dai babban ]a daga cikin ‘ya’yan wanda ya fi kowa yawan shekaru shi ne zai kula da dukiyar sai yadda ya ce ake yi da ita, Abdullahi (2008:346).

Shi wannan babban ]a shi ne zai maye gurbin mahaifin wajen jagorancin gida da kula da }annensa wa]anda mahaifin ya bari, shi zai ciyar da su ya tufatar da su idan sun isa aure kuma shi ne zai yi masu aure. Irin wannna ]awainiyar ce ya sa Hausawa kan cewa “ Babban wa mahaifi”

A ~angaren mata kuwa, Hausawa gabanin addinin musulunci ba su ba mata muhimmanci wajen raba gado, sai a wasu lokuta akan ba su }ananan dabbobi kamar awaki da tumaki domin su yi kiwo. Gonakki kuwa, na ‘ya’ya maza ne komai yawansu. Matsayin mata a

fagen gado yana bayyana ne kawai idan iyayensu mata suka mutu, to , a nan su ne za su gade kayan ayyukansu da ‘yankomatsan da suka bari na kayan ]aki.

Idan kuma ‘ya’yan mamaciyar sun yi aure, akan rabe kayan ne ga mutanen gida kamar kishiyoyi ko matan ‘ya’ya. Wasu kuma sukan bar kayan ne sai ‘ya’yan mamaciyar sun zo su za~i wa]anda suke so, kuma wannan al’ada ta rashin ‘ya’ya mata gado ta bi wasu Hausawa har yanzu da addinin musulunci ya yi tasiri a zukatanmu, musamman a }auyukka inda jahilci ya yi wa mutane kanta.

Gado ga Hausawa wani abin alfahari ne musamman dangane da gadon wasu kayan tarihi ko na bajinta da iyaye ko kakanni suka bari. Irin wa]annan kaya sun ha]a da walki ko wasu magunguna na tsafi ko kayan noma ko fa]a. Abdullahi (2008:347). Misali idan iyaye sun yi fice wajen amfani da ire-iren wa]annan kayan, to ‘ya’yan za su su gadi irin kayan saboda tunanin cewa mamatan sun sihirce kayan, don haka ko da sun mutu ayyukansu na magani da waibuwa yana a nan. Kwa]ayin da suke da shin a sanya gadon wa]annan kaya bai wuce su sami tubarakin masu kayan ba wajen waibuwa da sihirce-sihircensu.

## 3.3 Muhimmancin Gado

Lamarin gado abu ne da ake da ~ir~ishinsa a tsakanin Hausawa tun gabanin zuwan musulunci ga Hausawa, da musulunci ya zo kuma sai ya }ara ba da }arfi ga Hausawa wajen bayar da gado ga mai ha}}i. Wannan ya sa Hausawa suka ]auki lamarin gado da muhimmancin gaske.

Dangane da haka, ka]an daga cikin muhimmancin gado a zamantakewar Hausawa sun ha]a da;

i. Hanya ce ta farfa]o da tattalin arzikin ‘ya’yan da aka bari.

ii. Gado kan fito da asalin mutum a cikin al’umma.

iii. Gado kan fito da matsayi da darajar mutum a cikin al’umma.

iv. Rabo gado a tsakanin magada yana haifar da zaman lafiya mai ]orewa a tsakanin masu ‘yan uwa da dangi.

v. Wasu kan sami sana’ar yi a dalilin gado, musamman game da abin da ya shafi magani da warkarwa.

## 4.0 Kammalawa

Abubuwan da aka tattauna a cikin wannan darasi sun bayyana muna matsayin gado a cikin al’adun Hausawa, an kuma ga yadda bayani ya gabata game da ma’ana da dalilan gado da kuma matsayinsa tare da muhimancinsa ga al’ummar }asar Hausa.

## 5.0 Ta}aitawa

A dun}ule idan an lura darasin ya yi tsokaci ne dangane da al’adar gado bayan an mutu a cikin dangi, inda aka ga yadda fasalin gado yake ga Hausawa musamman kafin bayyanar musulunci. An lura da yadda ake nuna wa mata bambancin wajen rabon gado a can da.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Mene ne Gado?

2. Wace hanya Hausawa suke amfani da ita wajen raba gado?

3. Fayyace matsayin gado a cikin zamantakewar Hausawa.

4. Tattauna muhimmancin gado

## 7.0 Manazarta

Abdullahi I.S.S. (2008) “Jiya Ba Yau Ba: Waiwaye a Kan Al’adun Matakan

Rayuwar Maguzawa na Aure da Haihuwa da Mutuwa.” Kundin Digiri na Uku. Jami’ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.

Bunza A. M. (2013) “Death in Hausa: A Folkoric Perspectives.” A paper presented

at the International Conference on Folklore. In Hounor of Professor [andatti Abdul}adir, Bayero University, Kano.

C.N.H.N (2006) *{amusun Hausa.* Jami'ar Bayero, Kano.

Tambuwal, M.S. (2001) "Mutuwa a Idon Bahaushe: Nazari daga Wasu {agaggun Labaran Hausa." Kundin Digiri na [aya. Jami'ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.

**KASHI NA 4: Barkwanci a Zamantakewar Hausawa**

## 1.0 Gabatarwa

A darasin da ya gabata an tattauna ne game da al'adun gado a zamantakewar Hausawa, a nan kuwa za yi bayani ne a kan barkwancin Hausawa, ta la'akari da ma'anarsa da rabe-rabensa.

## 2.0 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce ana sa ran cewa a }arshen tattaunar darasi ]alibi ya san ma'ana da rabe-raben barkwancin Hausawa da gudunmawarsa wajen sada zumuntar jini da ta sana'a.

## 3.0 Ma'anar Barkwanci

Akwai ra'ayoyi mabambanta game da abin ake kira barkwanci, [angambo (1984:36) yana da ra'ayin cewa

> *Barkwanci zantuka ne na raha dawasu mutane, wa]anda Allah ya hore wa iya raha da magana da ban dariya ke yi wa jama'a".* Wasan barkwancin wasa ne da mutane ke gudanarwa ta hanyar zantuttuka a tsakaninsu da suka ha]a da bayar da 'yan gajerun labarai da suak ta~a faruwa ko aka }ir}ire su da nufin da]a]awa ko tsokana don a yi dariya. Wannan ya sa yawanci wasannin barkwanci ga Hausawa suka ji~inci raha da nisha]i da annashuwa.

Shi kuwa Brown 1954 ya ce " *Barkwanci wata dangantaka ce da al'ada ta yarda da wanzuwarta a tsakanin mutum biyu ko al'ummu a duk inda suka ha]u sai sun zolayi juna ba tare da an sami wani sa~ani a tsakaninsu ba.*

A ra'ayin Tukur (1999: 12) cewa ya yi *" Barkwanci zantuttukan raha ne da ban dariya da mafi yawan al'ummu suka amintu da wanzuwarsu don adana tarihinsu da yau}a}a zumunci."*

Dangane da wa]annan ra'ayoyi na masana da manazarta kuwa, a tawa fahimta barkwanci zai iya ]aukar wasannin zolaya da tozarta juna da mutane kan yi domin ko dai a zafafa zumunci ko a rage ra]a]in gabar ya}i da ya wakana a wasu lokuta da suka shu]e, ana yin irin wannan barkwanci ne domin a wasantar da wani raki ko wauta da wasu rukunin mutane suka yi tare da adana tarihin wanzuwar abin.

## 3.1 Rabe-raben Barkwanci

Kamar yadda aka yi bayanin dalilan barkwanci a sama, akwai dalilai da dama da suka haifar da karkasa barkwanci zuwa gida-gida kamar yadda za a gani a nan gaba.

### 3.1.1 Barkwanci ta Fuskar Aure da Ya}i

Bayan nau'o'in taubassan Bahaushe da aka gani ta dangantakar jini, akwai taubassaka ta fuskar aure da ya}i. Ga taubassan Bahaushe ta fuskar aure da ya}i da misalansu maasu zuwa kamar haka: .

### 3.1.2 Barkwancin Gobirawa da Yarbawa

Gobirawa da Yarbawa barkwancinsu na auratayya ne. Gobirawa suka ba Yarbawa aure lokacin da suka iso Gobir kan hanyarsu ta neman mafaka bayan sun baro gidan asali. Duk lokacin da Gobirawa da Yarbawa ke wasa, za ka yi tsammanin fa]a suke yi saboda rigimar da ke yi. Yarbawa suna cewa Gobirawa bayinsu ne da suka gudo. Su kuma Gobirawa su ce Yarbawa su dai je su nemi bayinsu wani wuri ba dai su ba. Gobirawa na tsarguwar Yarbawa da yawan raki da }azanta da tsoro. Misali an ce wata rana wasu ~arayi sun shiga ]akin wani Bayarbe mai girman jiki domin su yi sata. Kafin shiga ]akin

Bayarben na farke, amma sai ya yi shuru yana kallon su har suka shiga ]akin. Da shigarsu sai suka fara kwasar kaya. Duk abin da ke gudana cikin duhu ne domin ~arawo ba ya son haske bale ya zo da shi. Da suka kwashe kayan ]akin, sai suka ci gaba da lalube cikin duhu. |arawo ya kai hannunsa ga jikin Bayarben. Jin girman Bayarben ya sa ya tambayi abokan satarsa mutum ne ko dila? Da jin haka sai Bayarbe ya bu]a baki ya ce "Dila ne".Wannan misalin wasan barkwancin da ke gudana tsakanin Gobirawa da Yarbawa a inda Gobirawa ke tsarguwar Yarbawa saboda tsananin tsoron da ke gare su.

**3.1.3 Barkwancin Katsinawa da Kabawa**

Katsinawa taubassan Kabawa ne ta fuskar al'ada. Barkwancinsu a kan auratayya ne. Katsinawa suka ba Kabawa aure. An ce Sarkin Katsina mai suna Tsaga-Rana ne wanda ya yi sarauta tsakanin 1751-1764 ya ba sarkin Kabi na wancan lokaci auren 'yarsa, ta haifi 'ya'ya masu yawa, to shi ya sa wasa irin na ]an namiji ya shiga tsakaninsu tun daga wannan lokaci har zuwa yau. Wasan Barkwanci da ke gudana tsakaninsu, ba su yi wa juna wani kirari sai dai zantuttukan ban dariya da yi wa juna sha}iyanci, ba na cin zarafi ba. A lokacin kar~ar shara kuma, Kabawa ke ba Katsinawa dukiyar shara saboda Katsinawa su ne 'ya'yan mace. Duk da haka, tare da canzawan lokaci, a halin yanzu duk wanda ya fi }arfi, shi ke badawa.

**3.1.4 Barkwancin Katsinawa da Ha]ejawa**

A wata majiya an ce Barkwanci Katsinawa da Ha]ejawa ta jini ce. A wata da ba wannan ba wasu na ganin cewa, Barkwancisu ta auratayya ce ba ta jini ba. An yi auratayyar ne a zamanin Sarkin Katsina Bawa [anguwa (1804-1805), Sarkin Ha]eja na wannan lokaci ya auri wata Bakatsina 'yar uwar Sarkin Katsina mutunmiyar Kurkujan ta }asar Musawa suka haifi 'ya'ya masu yawa. Daga cikin 'ya'yan da suka haifa ne wani ya yi sarautar Ha]eja. Saboda wannan har yanzu ana yi wa Sarakunan Ha]eja kirari da 'Kurkujan garin maza'. Da wannan dalili ne Sarakunan Ha]ejawa tun daga wannan lokacin suka yi wa Katsinawa kallon dangin uwa, kakanninsu kuma 'yan taubassai; duk shekara Katsinawa na ba Ha]ejawa kyautar dukiyar shara. Bayan wannan akwai wata majiya da ba ta inganta

ba dangane da cewa Barkwanci da ke tsakanin Katsinawa da Ha]ejawa ta ya}i ce. Sam! Ba a ta~a yun}urin ya}i ba bale a ce an gwabza tsakanin wa]annan taubassai. Majiyar da ke da madogara mai }arfi ita ce, Barkwanci Ha]ejawa ta auratayya ce ba ya}i ba. Ga misalin maganganun da Katsinawa ke takalar Ha]ejawa da su a lokacin wasansu:

“Ha]ejawa na Sambo ungulai.
An ci kasuwa da ku kun koma kala,
Ha]ejawa yaushe za ku fanshi kanku?
Ko sai mun ‘yanta ku da kanmu?
Gimsau birnin dawakin da maita tai yawa kuka cinye”.
Su kuma Ha]ejawa  na mayar wa Katsinawa da martani kamar haka:
“Ina maza suke? Duk sun zama mata!,
Katsina ]akin kara a da,
Yanzu kuwa ]akin kara,
Bakatsine mai kan }warya,
Na Dikko ]akin fara (ta’adi) maimakon kara,
In kuna gida sai gaba”.

### 3.1.5 Barkwancin Kanawa da Daurawa

Akwai barkwanci a  tsakanin zuriyar Kanawa da Daurawa inda wasu masana suka ce ya}i ne dalilin Barkwancisu. Wasu kuma sun ce ala}ar jini ke tsakaninsu. Kanawa ‘ya’yan Bagauda ne, Daurawa kuma ‘ya’yan Garori ne. A kan wannan dangantaka ne aka ce wasan jika da kaka ke tsakaninsu.

Ningawa an ce barkwancisu ta faru ne a kan ya}in da suka yi tsakaninsu. An kuma ce auratayya ne sanadin Barkwancisu. Ba wannan ka]ai ba, an ce jikoki da kakanni ne.

Haka kuma, barkwanci da ke gudana tsakanin Kanawa da Zazzagawa an ce ya}i ne kai tsaye babu musu. Suna takalar juna da cewa, kai ne bawana, matsoraci da sauransu.

Barkwanci da ke tsakanin Kanawa da Zamfarawa cewa ta auratayya ce da kuma karin harshe. Auratayyar ba ta jini ba ce. Karin harshe kuwa da aka ce ya haddasa wasan taubassaka tsakanin Kanawa da Zamfarawa ba komi ba ne sai bambancin kalmomi da furcin su. Kanawa na ganin  Zamfarawa ba su da kyakkyawar Hausa kamar su. Su kuma Zamfarawa na yi wa Kanawa wannan kallo cewa Hausarsu ba daidaitacciya ba ce. Haka suke zolayar juna kan rashin amfani da daidaitacciyar Hausa. Babu ~ata rayuka, sai dai a yi wasa da dariya kowa ya kama gabansa.

### 3.1.6 Barkwanci Ha]ejawa da Katagumawa

Asali dangin juna ne. An ce Auyo da jihadin }arni na goma sha tara sai aka sami wa]annan dangogi suka sami rabuwa gida biyu. A wannan lokaci Auyo ta kasance cikin yankin Ha]eja, Shira da Tashena kuwa, suka koma yankin Katagun. Duk da rabawar da jihadin ya haddasa bai sa hul]arsu  yankewa ba. Ha]ejawa na taimaka wa Katagumawa duk lokacin da ya}i ya samu tsakaninsu da wasu al'ummu. Barkwanci da ke tsakanin Ha]ejawa da Katagumawa ta gori ce, inda Ha]ejawa ke ce wa Katagumawa ~arayi da mayu da raggaye da matsorata. Su ma Katagumawa abin da suke gaya ma Ha]ejawa, don nuna fifiko kan juna.

### 3.1.7 Barkwanci Hausawa da Wasu {abilu

Bayan Barkwanci da ke tsakanin Hausawa zallarsu, akwai wadda ke tsakanin su da zama ya ha]a su wuri ]aya, ko kuma saboda wani dalili. Kasancewar taubassaka tsakanin Hausawa da }abilu na daban, za a yi bayanin yadda Barkwanci take. Ga abin da aka nazarto na Barkwanci Hausawa da wasu }abilu kamar haka:

### 3.1.8 Katsinawa da Nufawa

Wa]annan }abilu mabambanta da aka sami taubassaka tsakaninsu dalilin ya}i da auratayya ne. Wasu sun ce auratayya ce sanadiyar Barkwancisu. Wasu kuma sun ce ya}i ne. Duk da yake an kawo dalilai biyu da suka haddasa taubassaka tsakaninsu, dalilin ya}i ya rinjaya a inda aka ce, lokacin da ya}i ya ~arke tsakaninsu an fatattaki Katsinawa gaya.

Kafin a kama su matsayin ganima sai Katsinawa suka sami dabarar amfani da fitilar hannu suna haska wa Nufawa a fuska da dare. Shakkar makirci, sai Nufawa suka tsorata da hasken da ake haska musu, suka rin}a gudu lokacin ya}in. Daga nan sai Katsinawa suka ci gaba da yi wa Nufawa gori da cewa raggaye ne kuma matsorata.

### 3.1.9 Katsinawa da Barebari

Katsinawa taubassan Barebari ne kuma ya}i ya haddasa ta. Bayan fatattakar Katsinawa, an yi sulhu daga bisani. Sulhun da aka yi tsakaninsu shi ne, Katsinawa su rin}a kai wa Borno wasu kayayyaki da kuma bayi domin neman fansa. Wannan kuwa, ya yi sanadiyar Barebari na ce wa Katsinawa bayi. Duk wanda aka rinjaya a wurin ya}i shi ke neman fansa ga maigidansa ga al’ada. Don haka, Katsinawa ne yaran Barebari ba tare da ka-ce-na-ce ba ta fuskar Barkwanci al’adar Bahaushe.

### 3.1.10 Katsinawa da Gobirawa

Taubassan juna ne kuma ya}i ya haddasa wasansu. Wannan ya faru a zamanin Sarkin Katsina Janhazo (1740-1770), Gobirawa suka kai ya}i Katsina. Lokacin Sarkin Katsina ba ya nan, ya je rangadi. Ga al’ada ba a ya}ar gari idan shugaba ba ya nan. Ganin haka sai suka ~alle }yauren {ofar Guga suka tafi da shi Gobir. A wata majiya kuma cewa aka yi, Sarkin Gobir Ibrahim Babari (1737-1764) ne ya aurar ma ]ansa ‘yar Sarkin Katsina Janhazo. Bayan an yi auren, aka rabu ba tare da an ]auki lokaci mai tsawo ba. An ce wannan rabuwa da aka samu ta yi sanadiyar rashin jituwa tsakanin Katsinawa da Gobirawa. Saboda wannan sai Gobirawa suka kai wa Katsinawa ya}i. Da suka kai ya}in ba su tarar da Sarkin Katsina gida ba, sai suka ~alle }yauren }ofar Guga suka zo da shi Gobir. Katsinawa na takalar Gobirawa da maganar da Sarkin Gobir ya yi ta cewa, “Ar, a mazaya a mai da iri gida”. Duk lokacin da aka gaya wa Bagobiri wannan sai ya tunzura, ya yi hargagi saboda rashin jin da]i amma, ba a fa]a. Yin fa]a da abokin wasa don wata maganar da ya gaya wa abokin wasa, abin kunya ne, kuma abin fa]i.

### 3.1.11 Barebari da Fulani

Barebari taubassan Fulani ne. Fulanin da ake nufi su ne da suka }addamar da jihadin }arni na goma sha tara, kuma jihadin ne ya yi sanadin Barkwancisu. Suna takalar juna da ce ma juna raggo da bawa da matsoraci ko kuma ~arawo da sauran maganganun da suka yi kama da haka. Saboda shaharar Barkwanci Barebari da Fulani, har wa}a [anmaraya Jos ya yi musu. Ga abin da [anmaraya ya ce:

> "Barebari, Fulani,
> Manyan abokanku wasa,
> Wasanku ba doke-doke,
> Wasanku ba zage-zage,
> Sai dai ko }arin zumunta"

### 3.1.12 Barkwanci Hausawa da Buzaye

Barkwanci da ke tsakanin Hausawa da Buzaye ba ta ya}i ba ce , kuma ba ta auratayya ba ce. Hausawa na jan Buzaye saboda wautarsu da rashin hankalin da suke nunawa cikin abubuwan da suke gudanar da ma'amalarsu da mutane. Saboda abubuwan wauta da Buzaye ke aikatawa ana yi musu dariya ya sa Hausawa suka ]auke su abokan wasarsu na zamantakewa kawai, ba na jini ba ko }abila ko sana'a. Duk da haka, Buzaye an san su da sana'ar gadi da gyartai, wato masu ]inkin }warya da sauran abubuwa. Hausawa na yi wa Buzaye wasa da abin da wani Buzu ya yi. An ce wani mutum ne ya gina gidansa, amma ba a kammala ba. Buzun ya mayar da gidan mutumin wurin bahayarsa. Yau da gobe mai gidan ya damu da kashin da Buzun ke yi masa cikin gida, sai ya nemi shawarar yadda zai yi. Aka ce masa, ya bari sai ranar da Buzun ya je wajen yin kashin ya same shi. Idan ya sami yana yin kashin, ya bari ya }are. Idan ya tashi sai ya ce, alhamdu lillahi yau na gode ma Allah da ya ba ni sa'ar samun kashin Buzu ]anye. Da ma na yi ta nema domin ha]a wani magani ban samu ba sai yau. Buzu na jin haka sai ya kada baki ya ce "Ba ka samu ba ]an uwa, ba ka samu ba". Buzu bai tafi ba sai da ya kwashe kashin da ya yi duka a cikin gidan, yana kwasa yana cewa "Ba ka samu ba ]an uwa, ba ka samu ba". Da irin

wa]annan abubuwa ne da Buzaye ke aikatawa Hausawa na yi musu sharri a kansu har wasa ta kasance tsakaninsu. Haka kuma akwai wata takala da ake yi wa Buzaye dangane da sabawa da suka yi da cin da}uwar aya. Wani Buzu ne ya sayi da}uwar aya ya ci ya ji da]i. Ana nan wata rana ya ga mai tokar sha na talla, sai ya kira ya saya, tsammanin da}uwa ce. Fara cin da}uwar ke da wuya, sai Buzu ya fahimci ba irin da}uwar da ya saba ci ba ce. Yana ci baki na kunfa, sai ya ce "Kai! Wannan dakuwa ba irin na jiya ne ba. A ci dai kar kudi shi baci" Tun daga wannan lokaci duk abin da bai gami Bahaushe ba wanda ya shafi abinci matu}ar ya zama dole a yi amfani da shi, za ka ji ya ce "A dai yi na Buzu, a ci dai kada ku]]i su ~aci".

**3.1.13 Barkwanci Hausawa da Ibo**

Ibo sun yi fice da nuna son ku]i sosai da kuma }yamar ciwon kuturta da dangoginta. Saboda wannan nuna son ku]i ya sa Hausawa ke kiran su dodannin ku]i. A al'adance idan Bahaushe ya yi hamma yakan sa hannu ya rufe bakinsa tare da yin sallama ta hanyar furta kalimar shahada. Ana nan wata rana wani Igbo na kusa ga wani kuturu bai sani ba, sai hamma ta zo masa. Da kuturu ya ga Igbo ya wangame baki bai sa hannu ya rufe ba kuma bai yi salati ba, sai kuturu ya sa dungun hannunsa cikin bakin Igbo ya rufe sai ya ce "Shege kafiri, kana hamma ba salati kuma ba rufe baki" Daga wannan lokaci sai abin ya koma wasa tsakanin Hausawa da Igbo saboda Igbo ba su san ana rufe baki ko yin sallama lokacin da ake hamma ba. Haka kuma akwai wani labari da aka bayar na wani mai gidan haya da wasu Igbo. Mai gidan ya bu}aci Inyamuran su tashi su ba shi gidansa suka }i tashi. Ana nan maganar ta kai kotu har sau biyu. Al}ali ya hukunta Igbo su tashi cikin wani lokaci da aka yanka musu. Lokacin tashi ya yi duk dai Igbo ba su tashi ba. Ganin haka sai mai gidan ya je wurin Sarkin kutare ya gaya masa abin da ake ciki, tare da neman kutare su zo su tare a harabar gidan har sai sun tashi a kan wata ijara da zai ba su. Haka kuwa aka yi. Kutare suka tare a gidan suka kwana ]aya ba su fita ba, Inymurai sai kwasan kaya suka bar gidan dole. Wannan ya faru ne saboda }yamar da Igbo ke yi wa kutaru. Har gobe idan Igbo na yi wa mutum rainin wayo, ya ce zai ha]a shi da kuturu zai daina, saboda canfa kuturu da aka yi cewa, duk wanda gari ya waye ya fita neman abinci

kuma bai fara ha]uwa da kowa ba sai kuturu, to babu nasara cikin wannan al'amari. Wannan ne ya sa Igbo na }yamar kuturu.

### 3.1.14 Barkwanci Zamfarawa da Dakkarawa

Zamfarawa da Dakkarawa taubassan juna ne ta fuskar zamantakewa a wuri ]aya kawai. Ba su da ala}ar jini, kuma ba su yi ya}i ba. A zamanin da, zamfarawa da Dakarkari wuri ]aya suke. Halinka da manomi da mafarauci, kullum ya fi son ya sami yalwa a kowane ~angaren rayuwa. Ganin }asar noma ta fara raguwa ya sa Dakarkari suka tashi daga wurin da suke zaune cikin Zamfara suka koma wani daji mai }asar noma sabuwa cikin Jihar Kebbi suka zauna suka ci gaba da rayuwarsu ta noma da farauta. Zaman Zamfarawa da Dakkarawa ya yi kyau sosai har zumunta ta }ullu tsakaninsu. Za a ga haka a cikin wa}ar Umaru ]an Bazamfare da ya yi wa Dakkarawa. Ga misalin abin da ya ce:

Ummaru: Ni ne Ummaru ]an Bazamfare,
Kuma Ummaru ]an Bazamfara,
Amshi: Yeye yeye ye Badakkare
Ummaru: Ni Ummaru in ina ki]i,
Ina iya gane farin Badakkare,
Kuman ina iya gane ba}in Badakkare.
Amshi: Yeye yeye ye Badakkare
Ummaru:Wanda kai mun kyauta in muna ki]i.
Shi muka ce ma farin Badakkare.
Amshi: Yeye yeye ye Badakkare
Ummaru: Wanda kai muna rowa in muna ki]i
Shi muka ce ma ba}in Badakkare .

Zaman da Zamfarawa suka yi da Dakkarawa ya sa Ummaru ya ]auki wasa da su har ya yi musu ki]i. Su kuma Dakkarawa suna jin da]in wa}ar domin har rawa suke yi lokacin wa}ar. Don haka Barkwanci zama tare ta yi kyau matu}a tunda dan}on zumunci ya }aru.

## 3.2 Barkwancin Hausawa ta Fannin Sana'a

Abubuwan al'ada abubuwa ne da ke gudana kullu yaumin, ba sai an dogara ga rubutun wani ba duk da yake rubutun na taimakawa. Akwai Barkwanci da ake samu tsakanin Hausawa masu sana'a da ma wasu da ba Hausawa ba.Barkwanci mafi yawan masu sana'a ta fara ne da kishin juna da ganin fifiko a kan juna. Haka kuma akwai taubassaka tsakanin masu sana'a saboda kyakkyawar hul]a da ke tsakaninsu. Daga cikin masu sana'an da ke taubassaka da juna su ne:

### 3.2.1 Masunta da Mahauta

Ganin abin da masunta ke samu kamar banza ne ya sa mahauta yin kishin masunta tare da }yashin su. Ko yaushe zaune suke a wuri ]aya, ba mai korar wani. Suna takalar juna da maganganun zolaya. Mahauta na ce wa masunta ga ku]insu a ba su fata da kayan ciki saboda sanin kifi ba ya da fata da kayan ciki kamar dabbobin da suke yankawa. Haka kuma sukan ce wa masunta duk wari suke yi. Masunta su ce wa mahauta marikita, kuma masu cin amanar jama'a saboda yawan cin bashi da }in biyan sa. Wani lokaci masunci ko mahauci kan sayi sana'ar juna don kawai su yi wannan wasa. Barkwanci da ke tsakaninsu ba ta jini ko }abilanci ba ce.

### 3.2.2 Mahauta da Majema/Makiyaya

Akwai taubassaka irin ta masu sana'a tsakanin mahauta da majema da kuma makiyaya saboda ala}ar da suke da tsakaninsu ta fuskar sana'o'insu. An ce wata 'yar mahauta ce ta auri wani majemi suka hayayyafa sosai, sai ]iyan ]iyar mahauta suka rin}a zuwa gidan kakanninsu mahauta har aka koya musu sana'ar gyaran fata suka iya, suka ci gaba da yi. Mahauta ke ba majema dukiyar shara a lokacin da watan Muharram ya kai goma. Ke nan, mahauta ne iyayen gidan majema. Barkwancisu ta jini ce ba kamar masu wasa kawai ba. Sana'a ta sanya wasa tsakanin mahauta da makiyaya kuma, makiyaya ne iyayen gidan mahauta domin ta ~angarensu ne suke samun abincinsu.

### 3.2.3 Wanzamai da Ma}era/ Sharifai

Wanzamai taubassan ma}era ne da sharifai ga al'ada. Sharifai jikokin Annabin rahama (S.A.W), wato Hassan da Hussaini. Haka kuma akwai labarin wani wanzami da ya yi wa Annabi S.A.W. }aho, bayan ya cire }ahon sai ya so ya zubar da jini a }asa, ya ga }asa ta tsage domin bu}atar jinin. Da ya ga }asa ta tsage sai ya fasa ya dubi sama, ita ma ta bu]e domin bu}atar jinnin. Haka ita ma ya fasa, ya }yale ta sai ya shanye jinin. Nan take sai Annabi ya tambaye shi ya ce "Shanye jinin ka yi?" Sai wanzamin ya kar~a ya ce, "Shanyewa na yi". Jin haka da Annabi ya yi sai ya ce "Wuta ba za ta }one ka ba". Wanzamai na takalar sharifai da maganar 'masu jiran ta Annabi', wato sadaka. Sharifai kuwa sai su ce wa wanzamai, Kana so kai ma a ba ka? Sai wanzamai ya ce "A'a ba ni so" Nan take sai Sharifi ya ce "Subhanallahi! Akwai wanda ba ya son na Annabi? Sai ]an wanzan!

Wasan taubassakan da ke gudana tsakanin ma}era da wanzamai na maigida da yaro ne. Kowa na cewa shi ne ubangidan wani. Sai dai a al'ada mai bayarwa ya ]ara mai kar~a. Don haka, ma}era ne masu gidajen wanzamai saboda sai ma}era sun }era sannan wanzamai ke samun kayan aiki.

### 3.2.4 Barkwanci Masu Goro da Masu Gishiri

Sana'ar goro na bu}atar ruwa gishiri kuma ba ya bu}atar ruwa ko ka]an. Duk lokacin da mai tallar goro ya ha]u da mai sayar da gishiri sai ya yi masa wasa ya tambaye shi cewa "A ]an sa ma ruwa ka]an? Ko kuma a lokacin damina, musamman idan akwai hadari, za ka ji mai tallar goro na yi wa mai gishiri wasa yana cewa "Allah Ya sa a sako ruwa yanzu-yanzu". Shi kuma mai gishiri ya ce ba amin ba saboda ya san wasa ce mi goro ya ja shi da ita, ba don ba ya son a yi ruwa ba.

### 3.2.5 Barkwanci Masu Ra}umai da Masu Jakai

Barkwanci da ke tsakaninsu ta sana'a ce ba ta jini da }abilanci ba. Dukkansu masu amfani da dabbobi ne domin sufuri. Wasan da suke yi na }ara dan}on zumunci

tsakaninsu. Koyaushe mai ra}umi ya ha]u da mai jaki, sukan yi wasa da juna gwargwado. Masu ra}umai na takalar masu jakai da cewa, “Mai jaki munafukin matatai” Shi kuma mai jaki ya mayar wa mai ra}umi da cewa, “Mai ra}umi ~arawon keso, matarka ba ta shanyan ragga” Har gobe idan aka tambayi ]ayan wa]annan mutane, wane ne taubashinsa ta fuskar sana’a? Zai fa]i cewa mai ra}umi idan mai jaki ne, ko kuma mai jaki idan mai ra}umi ne. Don haka dangane da taubassan Bahaushe, masu ra}umai da jakai sun }ara wa Borno dawaki. Asalin wasarsu kishi ne da nuna fifiko kan juna. Mai ra}umi na kishin mai jaki domin ganin yake ya tare masa wuri tunda sana’arsu ]aya, har ma suna ganin su ne masu gidan masu jakai.

### 3.2.6 Direbobin Mota da Masu Ra}umai

Direbobin mota taubassan masu ra}umai ne ~angaren sana’a, saboda ko dauri Hausawa sun ce, mai koda ba ta son mai koda. Ala}ar da ke tsakanin mai ra}umi da mai jaki, irin ta ke tsakanin direbobin mota da masu ra}uma. Haka kuma, masu ra}uma na kallon su ne masu gidajen direbobin mota domin suna bugun gaba da asali ba da abin da zamani ya kawo ba. Su kuma direbobin mota na ganin su ne masu gidajen masu ra}uma har wani lokaci sukan yi musu wasa da cewa, da mai ra}umi da ra}umi da kayan da aka ]auko duk su zo su shiga a kai su wurin da suke so.

Idan aka yi la’akari da wannan dangantakar wasannin da ke faruwa a tsakanin Hausawa da Hausawa ‘yan uwansu da kuma Hausawa da wasu }abilu tare da uwa uba asannin da ake samu a sakamakon dangantakar sana’o’in Hausawa na gargajiya ya isa ya zama wata hujja ta tantance Bahaushen asali. Dalili shi ne, wannan taubassaka da ke gudana a tsakanin al’ummar Hausawa abin bugun gab ace ga kowane mutum da ke alfahari da zamansa Bahaushe a fa]in }asar Hausa.

## 4.0 Kammalawa

A cikin wannan darasi kamar yadda aka gani an tattauna ne game da wasannin barkwanci da Hausawa ke gudanarwa a tsakaninsu da kuma wasu }abilu da suke zamantakewa tare da su. An kuma fahimci cewa ana aiwatar da wasanni ne domin a samar da raha da

nisha]i a duk inda aka ha]u. A kan hakan ne darasin ya fito da rabe-raben barkwancin Hausawa.

## 5.0 Ta}aitawa

A dun}ule darasin ya fito wa da ]alibai masu nazari da muhimman batutuwa da suka shafi barkwanci a al'adun zamantakewar Hausawa, an kawo misalai da dama game da rabe-raben barkwanci da dalilan wasannin musamman a tsakanin }abilu da masu sana'a.

## 6.0 Auna Fahimta

1. Mene ne barkwanci?

2. Wa]anne dalilai ke haifar da wasannin barkwanci?

3. Fayyace wasu daga cikin nau'o'in barkwancin Hausawa.

## 7.0 Manazarta


Brown, R. (1940) " On Joking Relationship" *African Journal* Vol. No.3 Kano. Bayero University.

|a~ura S.A. (1983) Barkwanci, Kano. Kundin Digirin Farko, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

CNHN (2006) {amusun Hausa Na Jami'ar Bayero.

Ibrahim M.S. '(1982) Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci Kan Rayuwar Hausawa' Kundin Digiri na Biyu, Kano.Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Kwakwachi K.H. (2010) Asalin Hausawa, Harsashi Limited.

Muhammed M.S. (2010) Zumuncin Bahaushe. Kundin Digirin Farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu [anfodiyo, Sakkwato.

Maso M. (1973) 'The Nupe Kingdom in the Nineteenth Century. A Political History' Kundin Digiri na Uku Birmingham. University of Birmingham.
Smith M.. Government In Zazzau, (1800-1950) The International African Institute, London. Oxford University, Press.

Musa R.(1982) ‘Wanzanci A {asar Hausa’ Kundin Digiri na Farko Kano. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Sharifai I (1992) Take da Kirarin Sana’o’in Gargajiya. Kundin Digiri na Biyu, Kano. Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Sarki H.A. (Maso M. (1973) ‘The Nupe Kingdom in the Nineteenth Century. A Political History’ Kundin Digiri na Uku Birmingham. University of Birmingham.
Smith M.. Government In Zazzau, (1800-1950) The International African Institute, London. Oxford University, Press.
2000 ) Tarihin Zuwan Musulunci Afirka da Shigowarsa {asar Hausa.

Saulawa Y. (1974) Mahauta da [abi’o’insu. Kundin Digirin Farko, Kano.Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Salisu M.S. (1984) Wasannin Wasu Sana’o’in Hausawa na Gargajiya, Kundin Digirin Farko Kano, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Tukur A. (1999) Kowace {warya Da Abokiyar |urminta, Gidan Dabino Publishers No. 8 Janruwa Street, Sani Mainagge, Kano, Nigeria.

Umar M.B. (1986)Dangantakar Adabin Baka da Al’adun Hausawa. Kano. Triump Publishing Company.

Umar M.B (1970) “ Barkwanci Tsakanin Hausawa da Wasu {abilu” *Makon Hausa*.
Kano, Jami’ar Bayero.